*RUFAFFEN SIRRI*

*NA SADNAF*

*ADABI WRITERS ASSOCIATION*

*BISMILLAHI RAHAMANIR RAHEEM*

*PAGE 1*

"Ba abinda na tsana sama da abinda zai Shiga tsakanina da baccina,kamar na kurma ihun bakin ciki haka nake ji a lokacin da naji Abban Nusrah na ta  shafani wanda nasan mai hakan ke nufi,tun kafin nayi bacci bai neme ni ba sai yanzu,ban motsa ba dan har ga Allah bazai samu abinda ya keso har ya gamsu ba,sai dai shi kadai yayi kidan sa yayi rawar sa duk da ba abinda ya shafe shi ko baccin nake idan yayi ra'ayi ko ban bashi hadin kai ba zai juyo dani ne ya samu biyan bukatarsa.

Ina Jin lokacin da ya rabani da zanin dana dora a saman t shirt din dake jikina,a madadin ya juyo dani sai naji ya rungumeni ta baya,ya fara k'ok'arin neman hanya da jikinsa dan tsawon zamana dashi ban wani san dan aike ba balle har wai a motsa min sha'awa,shi dai burin sa kawai ya shafani sama sama ya samawa kansa nutsuwa,inda naji Yana k'ok'arin yi yasa nayi saurin janye jikina,sai a lokacin na motsa na juyo Ina kallon sa cikin mamaki,shi kuwa idonsa a kankance ya kara jawoni,sai na juyo a rigingine dan ya samu abinda yake so dan Ina tunanin dan ta gefe yasa yayi hanyar da ba haka ba,sai dai a madadin ya hau kaina sai naga ya Kara juyar dani ya kankameni da hannu daya ya sa hannu daya ya Kara danna jikinsa wajen da yasa na Kara janye jikina da bala'in sauri na Mik'e zaune cikin mamaki Ina kallonsa.

K'ok'arin jawoni yake na janye jikina Ina "Lafiya kuwa Abban Nusrah mai haka"?

"Wane irin tambaya ne wanan Sajeeda bangane mai haka ba ki matso na samu nutsuwa ki koma baccin ki"

"To ai kai din ne bangane ba Kai ma kasan ba wajen nutsuwar ka nufa ba bayana naji kana k'ok'arin shiga"

Tsaki yayi ya Kara jawoni da k'arfi Yana "Ta bayan yafi dadi bari kigani"

Da karfi naga Yana Neman tura jikinsa bayana

Da k'ok'awa na fusge jikina cikin tashin hankali da mamaki na sauka daga gadon na nufi wajen

haske na kunna na zuba masa ido kamar yanda shi ma ya zubo min ido, tamkar an like min baki haka naji dan tsabar mamaki na ma kasa magana,shekarar mu  Ashirin da biyu da Aure bana Jin da gani har shi bakine a wanan fagen balle ince sani ne bai yi ba shi yasa yake k'ok'arin nema na ta baya har Yana cevmin yafi Dadi.

"Abban Nusrah anya a hayyacin ka kake kuwa"?

Mik'ewa yayi ya nufo wajen da nake tsaye yayi kasa da muryarsa yana "Sajeeda a hayyacina nake nasan zaki ji wani iri amma ki taimaka ki ba ni hadin kai ina so na gwada ta bayan nan ance yafi dadi"

"Allah ya kiyaye Kabiru Allah ya kiyaye ni zaka nema ta baya ta Inda ake kashi,kabiru Anya Kaine kuwa?waye yace ma ka nemi matar ka ta baya, idan Wanda ya baka shawara bashi da ilimi kai ina ka Kai naka ilimin bayan kasan haramun ne, bazan iya ba Kai ma da ka yi tunanin kayi gwajin ka fara istigifari"

Kasa ya Kara yi da murya cikin rarrashi  ya matsoni Yana "Sajeeda yanzu baza ki iya taimaka min ba ki bari nayi sau d'aya sai muyi istigifari an dade ana kwadai ta min ta bayan nan haba matata"

Ya fara k'ok'arin rungumoni na ture shi da iya karfina dan zuwa yanzu ma sai naji tsoron uban yayana ya kamani,gani nake kamar bashi ba

"Kabiru Ina ga ba'a hayyacin ka kake ba a tsawon lokacin da nake tare da Kai nasan baka shaye shaye ballantana nace ba'a hayyacin ka kake ba,a iya sani na ka na da ilimin ka daidai gwargwado ka san abinda ya ke daidai da wanda yake haramun, bazan tab'a maka biyayya na Sabawa Mahallicina ba Ina mai rokon ka idan a hayyacinka ka ke wani ne ya baka shawara ka zo ka neme ni ta baya,ka gaggauta rabuwa da koma waye dan so ya ke ya Kai ka halaka"

Daga haka na nufi Kan gado na na dauki zanina na  daura nayi hanyar fita daga d'akin ya hau kwalla min kira Yana

"Sajeeda Sajeeda karki sake ki bar d'akin Nan

Ko juyawa ban yi ba har na bar d'akin  har lokacin ban daina mamakin sa ba.

Koda na fito dan karamin palon namu fitila na kunna idona ya sauka akan agogo naga karfe uku na dare na zauna akan kujera tare da dafe kaina jikina har rawa yake bansan tunanin ma da ya Kamata nayi ba.

Na kasa yarda da abinda ya faru yanzu a daki,na kasa yarda mijina uban yayana da shekarar mu Ashirin da biyu da aure da arzikin Yara biyar har mun aurar da Yar mu ta fari Nusrah shi ne yau dare daya zai nemeni ta baya wai ya dade yana san yayi gwaji an ce Masa yafi dadi har

waye zai ce wa Kabiru ya gwada abinda Allah ya haramta.

Sosai na zurfafa a tunani bansan tsawon lokacin da na d'auka Ina saka da warwara ba,sai Kiran sallah ne ya katse min tunanin da na tafi.

Mik'ewa nayi na koma d'akin.

A kwance na ganshi Yana dan girgiza kafarsa da alama ba Bacci yake ba idonsa biyu.

Bandaki na shige na daura alwala na fito har lokacin Yana kwance bai motsa ba,nasan fushi yayi,da ace wani abin na Masa da har zai yi fushi dani da sai na bashi hakuri,amma ni nasan ba laifin da na masa bazan tab'a masa biyayya a sabon Allah ba ba muyi haka tun kuruciya ba sai yanzu da muka Manyan ta,tsawon zamana dashi ban tab'a hana shi hakkin sa ba Koda kuwa fada mu ke amma dai yau na bijire masa dan bazan iya Sabawa Allah ba,
tsigar jikina har tashi yake idan Ina hararo yanda wai zai sadu dani ta baya.

Sallah nake amma na kasa yin sa a nutse sabida tunanin da ya dankare min zuciya.

Har na sallame Yana kwance zuwa yanzu sai naji kamar canzo kabiru aka yi bashi bane dan iya sani na baya Wasa da Sallah fushi dani bazai saka wai yak'i fita massallaci sallah ba.

Kasa hakuri nayi da carbina a hannu na Mik'e na zagaya ta wajen da ya kwanta Ina "Abban Nusrah "Abban Nusrah yau ba zaka yi sallah bane"?

"Dama can ke kike saka ni nayi Sallah"?

"Bani nake saka ka kayi sallah ba amma dai bai dace idon ka biyu kana Jin ana sallah ka k'i tashi kayi akan lokaci ba"

Tsaki yayi ya juya min baya.

Zuwa yanzu bazan iya fadan kalar mamakin da nake na sauyawar halin mijina dare daya ba,ga nemana ta baya ga k'in sallah.

Bai tashi ba sai da gari yayi haske ya shige bandaki ya dauro alwala yazo ya tada sallah Yana sallamewa ya fice daga d'akin.

A ranar sukuku na wuni na rasa mai ke damuna dan tunda Abban Nusrah ya fice daga gidan bai Kara dawowa ba.

Har karfe hud'u na yamma Ina zaune zuciyata fal da tunanin muryar Yasmeen ya katse min

tunanin da na tafi "Umma ko dai magani zan d'auko miki ki sha"?

Girgiza kaina nayi na aro murmushi na yafa a fuskata sam bana so ta fahimci Ina cikin damuwa,dan nasan sai ta fini ma shiga cikin damuwar, kallonta da nake fuskar kanwata nake gani a fuskarta Margayiya Nuratu damuwar da nake ciki yasa naji hawaye na zubo min.

"Umma kuka kike"?

Share hawayena nayi Ina "ba kuka nake ba Yesmeen na tuna kanwata ne kawai Allah ya gafartawa Nuratu"

"Bata amsa ba illa idon ta da naga ya ciko da kwalla shekara goma kenan da rasuwar kanwata da ta kasance mahaifiyar Yesmeen.

Ruk'onta ya dawo hannuna Ina balain kaunar yesmeen tamkar yanda nake kaunar yayan cikina, Yesmeen ta Kara siye zuciyata ne daga lokacin da rukon ta ya dawo hannuna,tana da bala'in biyayya da hankali duk wani abu data san ina so bata Wasa dashi bata da burin daya wuce taga ta faranta min ko Yaya ta gani a cikin damuwa itama tayi ta damuwa kenan.

Ko yanzu ma nasan ba lailai taci abinci ba sabida ta gani a cikin damuwa.

"Jeki d'auko mana abinci mu ci dan nasan baki ci abinci ba.

Tura abincin kawai nake ba wai dan Ina gane dandanon sa ba,na daure na hadiye damuwar da nake ciki dan Kar na Kara dagawa Yesmeen hankali.

Koda muka gama cin abincin daki na shige na cewa Yesmeen zan dan kwanta dan itace take yin aikace aikacen gidan Kamar yanda ta Saba kafin Nusrah tayi Aure tare suke aikace aikacen gidan,dan su biyu ne kawai Mata kannen Nusrah duka maza ne,Saifullahi Fahad Hamza da Annur.

Sosai na tsinci kaina a cikin damuwa dan tunda nake da Abban Nusrah bai tab'a fita Yana fushi dani ba dan muna samun sabani zamu shirya,duk da Yana da zuciya nasan hanyar da nake bi na shawo kansa,amma jiya abinda ya b'ullo min dashi ya girmama tunanina bazan tab'a iya barin sa ya neme ni ta baya ba sai kace wasu jahilai.

Karfe goma Sha daya ya shigo gidan fuskarsa a bala'in hade ina zaune a palo Ina jiran dawowar sa dan har yara duk sun yi Bacci.

Ko sallama bai yi ba ballantana ya kalli Inda nake, d'aki ya shige batare da ya amsa sannu da zuwan da nake masa ba.

Da ido na bi bayan sa Ina Kara mamakin fushin da ya ke dani na rashin gaskiya har ga Allah

mamaki da al ajabi nake ,mik'ewa nayi na d'auko farantin da na jera abincinsa na bi shi d'akin.

Ko da na shiga a gefen gado na gan sa a zaune yana duba wani abu kamar a takarda ban dai san mai yake dubawa ba"

Na ajiye farantin a gefen teburin dake gefen gadon  Ina

"Abban Nusrah Sannu da  dawowa"

Bai dago ba ya cigaba da duba takardar Hannun sa

"Abban Nusrah mai na maka kake fushi dani?a iya sanina ba abinda na maka Abban Nusrah wani bak'on al amari ka zo min dashi wanda ni nasan kasan haramun ne,dagani har Kai ba yara bane,ga ta hanyar da Allah ya hallata ma ka neme ni ka samu nutsuwa dani,amma dare daya Abban Nusrah kace zaka neme ni ta baya ta Inda Allah ya haramta kaga dan na k'i bin umarnin ka bai Kamata kayi fushi dani ba dan babu biyayya a sabawa Allah,bansan waye ya baka wanan gurguwar shawarar ba,iya sanina duk wayanda kake mu'ammalla dasu ba mutanen banza bane bansan waye ya ce ma ka gwada ta baya zaka ji dadi  ba,taya wajen da ake kashi yayi dadi Ni dai kayi hakuri zan iya k'ok'arina dan na gamsar da Kai amma ban da ta baya"

Sai a lokacin ya dago ya kalleni ya ajiye takarda a gefen pillo Yana "Sajeeda duk abinda nake yi Ina sane tsawon zamana dake Ina ga baki tab'a ganin na neme ki ta baya ba,gwaji ne kawai nake so nayi naji abinda ake ji ba wani abu ba,amma tunda kin nuna bakya so shikenan ba zan Kara nema ba,na dauka duk abinda nake so matsawar bai fi karfin ki ba Zaki iya min"

"Wanan yafi karfina ne Kabiru shi yasa bazan iya ba abinda akace haramun ne ban ga dalilin da zai saka kace zaka gwada ba mu fa ba Yara bane idan muna raye ma wani shekara zaka gan mu da jika"

"Ya isa haka Sajeeda Kinga na Kara neman naki ne yanzu"!?

Shiru nayi Ina kallon sa yaja siririn tsaki ya kwanta ya juya min baya.

Nace masa ga abincin sa yace bazai ci ba.

Wasa Wasa mijina ya fara fushi dani dan naki bari ya nemeni ta baya Wanda zuwa yanzu lamarin nasa ya fara bani tsoro ko Yaya na shawo kansa asan na faranta Masa rai, a madadin yayi ta hanya da ya dace sai naga Yana neman tura jikinsa bayana.

Halin nan daya bijiro min dashi ya matukar daga min hankali dan kullum cikin fada mu ke.

Gashi mu ba Yara ba ballantana nace wani Zan nemi shawarar sa Wanda ni nasan mu ya

Kamata ma mu ringa hana wasu ba dai mu ba.

Ko a yanzu da ido nake bin sa har ya gama shiryawa bai ce min komai ba ya  fice daga dakin na sauke ajiyar zuciya ina tunanin mafita Kiran Nusrah daya shigo wayata ya katse min tunanin da nake.

Ina dagawa muka gaisa kamar yanda muka saba Inda take sanar min zuwan ta anjima na ajiye mata dambu na saki murmushi Ina sai ta zo.

Na Mik'e nayi waje dan na fadawa Yesmeen zuwan Nusrah duk da nasan kila ma sun yi waya.

Ina fitowa naga Abban Nusrah a zaune a doguwar kujera duk a tunanina Yama fita ashe fitowa yayi ya zauna a palon.

Yesmeen kuma na tsugunne a gabansa tana hada mi shi shayi.

Fitowa ta yasa ta dago tana "Umma Ina kwana"

Zama nayi a gefen shi fuskata d'auke da faraa na hau amsa gaisuwar ta ko kad'an bana so yarana su fahimci wani abu.

Tana gama hada masa ta mike tana bari ta d'auko kofi ta hado min shayin na girgiza mata kai akan ta bar shi sai anjima.

KABIR

Da ido ya bi Yesmeen din har ta shige d'aki ya d'auki shayin ya fara kurba a hankali har ya shanye Yana Jin idon Sajeeda a kansa.

Yana dire kofin ya mik'e yayi waje batare da ya tsaya Jin mai Sajeeda ke cewa ba.

Yana fita ya haye  machine din sa bai zame ko'ina ba sai wani hadadden gida da fadar haduwar sa bata Baki ne.

Mai gadi ya riga da ya gane shi hakane yasa ya bude masa ya shige da machine dinsa kansa tsaye ya nufi d'akin saukar baki dake farfajiyar gidan.

Kamar yanda yayi tsamani a zaune ya tarar da Alhaji Rabiu a cikin dakakiyar shaddarsa dake ta kyalli kamar madubi.

Sai da Kabiru ya sama wa kansa wajen zama.

Alhaji Rabiu yace "An dace kuwa"?

Sai da Kabiru ya sauke ajiyar zuciya yace "wlh ba'a dace ba duk ta inda kake tunanin zan biyo mata na biyo mata wlh tak'i bani hadin kai"

Murmushi Alhaji Rabiu ya saki Yana "Na fa san irin su haka suke da balain taurin kai Amma idan tasan wata ai bata San wata ba ka tashi muje wajen shugaba mu masa bayani"

Ya mik'e Yana k'ok'arin yin hanyar waje.

Kabiru yayi saurin dakatar dashi yana "Rabiu Ina kaunar matata tunda na yarda zan yi harkar nan zuciyata take cike da fargaba da tsoro ko bacci bana iya yi dan Allah muje wajen shugaba ka fada masa ya duba min ko zan iya yi da wata na samu biyan bukatata ba sai Sajeeda ba.

"Ikon Allah toh wa zaka samo"?

"Akwai yar kanwarta da nake rike da ita da ita nake so na samu biyan bukatar tawa"

"Bani da ta cewa muje daga can muji ko zai yu......

Hmmm

*RUFAFFEN SIRRI*

*NA SADNAF*

*ADABI WRITERS ASSOCIATION*

*Page 2*

Kabiru har suka je Suka dawo bai iya magana ba sabida kasan zuciyarsa cike take da tsoro,ji yake Kamar ba zai iya ba dokokin da Abubuwan da akace yayi sun masa yawa da tsauri,a hankali ya Kai dubansa wajen Alhaji Rabiu da ya kasance abokinsa tun primary da a lokacin ya fi shi k'ok'ari nesa ba kusa ba dan shi yake zuwa na karshe ma a ajinsu da kuwa suka gama primary  bai Kara saka shi a idonsa ba,bai Kara jin labarin sa ba sai a shekara biyu da suka wuce ya had'u dashi,sai da yayi da gaske ya gane shi sabida yanda ya dawo fari kal sabida yadda hutu da Jin dadi suka zauna masa tashin farko,kyautar dubu dari ya Masa,ya hada da bashi lambarsa,duk kalar rayuwar da yaso tun Yana karami na rayuwar Jin dadi shi yake gani a wajen Rabiu.

Gashi ya girma zai iya cewa ya d'auko tsufa tunda Yana dab da aurar da 'yar cikin sa duk bai samu cikar burin nasa ba.

Tuni yaji ya kwadaitu da san yayi kudin fiye ma da da hakane yasa ya makalewa Alhaji Rabiu ko zai taimaka Masa ya sama mi shi aiki irin nashi da shi ma zai samu kudin.

A haka Alhaji Rabiu ya ringa masa yawo da hankali Yana kasuwanci yake yi sai da yayi dagaske Rabiu ya fito ya nuna masa ta hanyar da ya samu kudin sa,idan har yaga zai iya.

Tsayuwar motar Alhaji Rabiu a wani tamfatsatsen gidansa da matarsa ta uku take ciki ya katse tunanin da Kabiru ya tafi.

Yayi horn Mai gadi ya bud'e masa.

Tun da suka shiga gidan Kabiru ya saki baki da hanci Yana kallon Aljannar duniya,maganar shugaba na dawo Masa a kunne,"zaka yi kudi, idan nace ma kudi,Ina nufin kazamin kudin da zai saka duniya ta san ka zaka ji dadin rayuwar ka zaka bar wa yayanka tarin dukiya ka tabbata baka tsallake duk sharuddan da aka gindaya ma ba daga yanzu kafin wata ukun zaka fara dandana arziki amma ka iya takun ka"

"Sauko mu Shiga daga ciki ka gaisa da Aseeya"

Muryar Alhaji Rabiu ya katse Masa tunanin da yake.

"Rabiu anya zan iya wlh bansan mai yasa nake Jin bazan iya ba gani nake za'a iya gano ni da wuri bazan iya yiwa Sajeeda haka ba"

Murmushi Alhaji Rabiu ya saki Yana "Tunda na iya yiwa Sakeena Yar uwata haka Kai ma zaka iya bafa kasheta zaka yi ba,a cikin kankanin lokaci Kai ma zaka zama kamar ni,kayi amfani da abinda kake dashi ka samu cikar burin ka,kar ka karaya abokina muje dai daga ciki indai Muka bi komai a yanda Muka tsara wlh baza'a samu matsala ba"

Kabiru gyada Kai yayi duk da a kasan zuciyarsa gani yake bazai iya ba.

Yabi bayan Alhaji Rabiu yana karewa gidan kallo,hararo kansa kawai yake a matsayin Rabiun ya mallaki irin wanan gidan,ya ginawa su Saifullahi manya manyan gida daidai da Nusrah ma sai ya mallaka Mata gida da mota, tuni yaji ya Kara kwadaituwa da ya samu kudin,a lokacin da suka Shiga palon da Kamar a kasar waje suke da suka shiga.

A lokacin kuwa daya zauna kalle kalle ya cigaba da yi Alhaji Rabiu ya haye Sama minti biyar a tsakani sai gashi ya sauko ya zauna.

Kafin kace me masu aiki sun cika gabansu da kayan ciye ciye.

Alhaji Rabiu kuwa sai murmushi yake dayaga yanda Kabiru ke hadiyar yawu.

Takun takalmin Aseeya matar Alhaji Rabiu dake saukowa daga saman benen yasa Kabiru maida hankalin sa wajen benen.

Yarinya ce bata fi saar Nusrah Yar sa ba ko zata girmi Nusrah bazai fi da shekara biyu ba,kyakyawa ce ta ajin karshe tamkar ita tayi kanta fuskarta d'auke da murmushi,har ta karaso gefen Alhaji Rabiu ta zauna ta fara gaida Kabiru da ya hau washe baki kasan ransa Yana ta mamakin yanda yarinya karama ta yarda ta auri sa'an mahaifinta.

Bayan sun gama gaisawa ta mik'e ta koma sama,

"Rabiu yanzu Wanan Yar yarinyar ka Aura"?

Murmushi Alhaji Rabiu ya saki  ya zuba Lemo a kofi sai da ya kurba ya ajiye ya kalli Kabiru Yana "Shekara uku kenan da Auren mu Kuma ta wajen nan da matarka ta hana ka ta wajen nake neman ta"

Ido Kabiru ya zaro waje Yana "Kuma sai ta yarda"?

"Kwarai kuwa ba Ina da kudi ba,a yanzu da kake ganin ta bama tasan Inda zata Kai kudi ba kaga kuwa ko dan su dole ta yarda da bukatata dan sai da na tabbata Iyayenta irin talakawan nan ne sosai,dan a garin talla ma na hadu da ita,na cikata da kudi na cika Iyayenta da kudi, basu da gidan kansu kafin na aureta yanzu kuwa har yayyenta maza ba Wanda ban siyawa gida ba tana morata a zahiri Ina morarta a badini"

Sai yayi kasa da murya

"Tana samun ciki take b'ari na riga na bada mahaifarta"

Ni kuwa Ina nan da yayana bakwai suna jin dadin su a waje"

Kabiru mamaki ya sa ya kasa ma magana dan sai a yanzu ya gane da rabon amaryar kudin sa ke Kara hab'aka uwar yayan sa kuma ta masa silar kudin.

"Rabiu dama nima na auri wata ta zama silar kudin bana so na tab'a uwar Yayana da mu ka Sha wahala tare da ya Kamata ace a yanzu taji dadina shugaba ya bani wata uku ya bani Abubuwan da zanyi har zuwa matakin karshe,tunda Muka baro wajensa wlh jikina a sanyaye yake gani nake bazan iya ba"

Wani irin mugun kallo Rabiu yabi Kabiru da shi yana "Ka ga idan baza ka iya ba ka tashi ka bar min gida ka Kuma dawomin da kudadena da na baka,kudin nan idan kayi ni zaka bawa ko me ana ta nuna ma hanyar arziki kana baudewa,duk uban wahalar nan da ka ringa bani dama baka

tsayar da zuciyar ka ba abu kad'an sai kace baza ka iya ba dalla tashi ka bar min gida kasan Kuma baa yiwa kungiya haka indai ka fasa wlh sai an tab'a ka"

"Ba abinda nake nufi ba kenan Rabiu ba fasawa zanyi ba sharrudan yanzu sunfi bani tsoro ina tsoron na kuskure a samu matsala"

"Ka kwantar da hankalin ka kasa a ran ka zaka iya Sajeeda da kake ta fadi ba fa kasheta zaka yi ba balle,dadin ma da ita za'aji gefe guda Kuma idan an kwana biyu zaka iya auren Mata uku kayi ta more rayuwar ka abokina kana Jin dadi,yayanka ka gan su fes,ni kasan gabad'aya yarana suna kasar waje,shawara daya dai Zan baka duk yanda muka tsara ka bi zaka Sha mamaki kila.ma.ka fini himma wajen bada abin arziki kudi suyi ta hauhauwa ai ba dawwama zamu yi muna yi ba zamu Yi iya yin mu kudin ya Kai mana yadda muke so sai mu tuba muyi ta istigifari Allah Mai yawan afuwa da gafara ne zai yafe mana duk shekara muna d'akin sa muna neman yafiya  fa wanan ba wani abu bane"

"Hmmmm toh shikenan Allah yasa duk Kar na samu matsala Ina Addu'a Allah yasa Kar Sajeeda ta tab'a rafkoni dan tana da balain wayo da san tabi kwakwafi"

Da haka suka cigaba da hirarsu wajen laasar Alhaji Rabiu ya Kara tsara masa duk yanda za'a yi ya d'auko kudi ya bashi mai yawa ya raka shi ya tafi.

Sajeeda

Idan naga yarana gabad'aya a gabana ji nake kamar banida wani matsala a rayuwata, zuwan Nusrah yasa na manta da damuwa da hawan jinin da Abban Nusrah ke neman saka min,Ina zaune a tsakiyar su duk mun baje a tabarma ana ta hira, wayarta ya hau ringing tak'i d'auka ganin Kiran ya Kara shigowa nace "Wai ba za ki dauki wayar ki ba ko ba kiran ki ake ba"?

"Umma Ahmad ne fa na san cewa zai yi na dawo ni Kuma na fi so na gaisa da Abba kafin na tafi na ga kowa ban dashi bazan ji dadi ba idan ban gan shi ba"

"Sai ki Kira shi a waya ku gaisa maza tashi ki tafi gidan ki bana San shashanci dama mijin ki ke ta Kira kika k'i d'auka"?

"Umma dan Allah ki bari na Kira Ahmad nasan bazai hana ni jiran Abba ba"

Sai da na ga ta kira mijin ta ya amince ta jira Abban ta kafin na yarda ta zauna duk da har a kasan raina ba gajiya nayi da ganin ta ba gani nake kamar jiya na haifeta sai gashi cikin ikon Allah da ran mu ta girma tayi, aure duk Wanda ya ganta yasan tana d'auke da karamin ciki,a tunanin da nake na tuna halin da mahaifinta ya bijiromin dashi,take da girmana da komai nabi

sauran kannenta da kallo da duk sun ma fi Nusrah girma Annur da Fahad ne kawai basu fita girma ba,mutane da yawa sun d'auka saifullahi yayanta ne da yake girman yazo da zamani har wani saje da gemu ya ajiye, ba Mai yarda ta girme shi,
Shigowar Larai da sallama yasa Mu ka mai da hankalin mu wajen k'ofar tare da amsa sallamar da tayi,Larai yar aiki ce a wani gida dake bayan layin mu na riga da nasan da zuwan ta tunda hajiyar ta kirani akan zata turo ta ta kawo min kayan aiki.

Buhun hannun ta ta fara ajiyewa kafin ta sauke kayan dake Kan Almajirin dake biye da ita a baya ta zauna muka gaisa

Tana "ga kayan nan Hajiya tace ki duba abinda babu sai na karbo"

Kayan na duba naga duk abinda na bada list Ina bukata akwai hakane yasa na dago Ina "Karfe uku ne taron ko?

"I karfe uku ne idan Allah ya kaimu"

"Toh ba damuwa gobe karfe daya da rabi kizo da kulolin zuwa lokacin na gama in sha Allah"

Mik'ewa tayi ta min sallama ta tafi,

"Umma dan Allah ki daina wanan aikin wahalar wlh har ga Allah bana so sabida ke nake so na nemi kudi ki huta"

Cewar Faisal yana hade rai.

Saifullahi ya karba da "Abin nan na cimin tuwo a kwarya wlh nima bana san aikatau dinan da take karba kudin ma ba wani Mai yawa ba a gaskiya lokaci yayi da Zaki daina wanan aikin umma"

Murmushi na saki Ina "Ina ga tunda kuka taso kuka same ni da sana'ar nan, ni kadai nasan kalar rufin asirin da wanan sana'ar yamin bani kadai ba har daku tunda kunsan aikin baban naku ba wani mai kwari bane idan na daina ku kan ku zaku Sha wahala a yanzu idan ta biyani kudi na gobe shine zan samu kudin registration din jamb din ka"

Yana k'ok'arin magana Abban Nusrah ya shigo da sallama hannun sa d'auke da ledoji niki niki.

Tuni yaran Suka mimike Nusrah ta riga su isa wajen sa tana "Abba oyoyo tun dazu nake jiran dawowar ka sannu da zuwa"

Washe baki yayi Yana "Kin dade da zuwane"

"Kana fita nazo Abba"

"Ai da kin kirani a waya ai da na dawo da wuri ya kike ya maigidan naki"

A kunyace Nusrah ta ringa amsawa Bayan ta ajiye ledojin.

Daya bayan daya suka ringa Masa sannu da zuwa fuska a washe ya ringa amsawa sai da ya juyo muka hada ido ban kawo zai min kallon arziki ba naga ya sakar min murmushi take na saki murmushi Ina Jin dadi a raina na Masa sannu da zuwa a daidai lokacin da Yesmeen ta d'auko masa ruwa ta ajiye a gabansa.

Ganin su Saifullahi na k'ok'arin mik'ewa yasa yayi saurin dakatar dasu sai da suka zauna ya kalli Saifullahi Yana "Ni nawane ma kudin registration din ka"

Washe baki Saifullahi yayi Yana "Abba na dan yi aikin lebura na tara dubu goma yanzu ciko nake nema"

"Nawane cikon"

"Dubu goma Sha biyar ne"

Hannu yasa a Aljihu ya d'auko wrapper Dari biyar biyar,na gwallo Ido Ina kallon sa tamkar yanda duka yaran suma suka zaro ido suna kallon kudin,ya kirgo Dubu ashirin dan dani aka kirga kudin ya mikawa Saifullahi Yana "gashi nan kaje kayi registration din"

"Na gode Abba Allah ya Kara arziki"

"Ameen"

Ya kalli Faisal yana "nawane kudin jamb din naka"

Shima baki a washe ya fada masa ya kirga ya bashi zuwa lokacin farinciki da mamakin Inda ya samu kudi Mai yawa hakane ya cikani dan iya sanina yanzu ba lokacin samun kudin sa bane

Dan aikin nasa sai lokacin zafi sosai idan ya samu su gyaran freezer haka Ac franker da sauran su.

Mamaki bai Kara kasheni ba sai da naga daidai da Annur sai da ya tambaye shi matsalarsa ya kirgo kudi ya bashi ko Nusrah bai bari a baya ba ya kirgo Dubu goma ya  bata har ga Allah kasa motsi nayi dan a lissafin da nayi ya bada wajen dubu sabain,Ina ya samu irin wanan kudin mai yawa haka yadda ya bawa Nusrah dubu goma haka ya bawa Yesmeen da bakin su ke washe suna ta zuba Mai godiya da Addu'a sai amsawa yake bakin sa shi ma a washe.

Sai a lokacin yacewa Yesmeen ta d'auki ledar kajine a ciki ta wanke ta dora sai yarana suka Kara haukacewa da murna har Nusrah na wlh sai ta tsaya an gama ta tafi dashi.

Sai da duk Suka watse ya juyo ya kalleni yana "Hajajju yau nima na dan yi abin kwarai rabon da na yiwa yaran nan abu da kaina har na manta baki ji dadin da naji dana ga farin ciki a fuskarsu ba"

Murmushi na saki Ina "Allah ya Kara arziki ya Kara budi ni da adashe na ma Zan dauka na bawa Saifullahi yayi registration din sai Kuma Allah yayi ikon sa ka samu kudi"

"I Allah kuwa yayi Ikon sa Alhamdulillah ke ma ai ga naki siyayyan nan na miki"

Ya turo min daya ledar gabana

Baki a sake na bud'e ledar naga less ne guda biyu sai atamfa da wani bakin mayafi duk da ba wani sanin kaya masu tsada nayi da gani kayan masu tsada ne"

"Abban Nusrah a Ina ka samu kudi mai uban yawa haka"

Kabiru gyada kansa yayi dan yasan zaa rina indai Sajeedar daya sani ne sai ta tambaya

"Haduwa nayi da wani tsohon abokina ya zama mugun mai kudi,shi yamin kyautar kudin nan bai tsaya iya nan ba yace zai taimaka min na samu aiki"

"Wane abokin naka ne dan Kamar duk nasan abokanan ka"?

"Aa baki san wanan ba primary Mu ka yi tare"

"Allah sarki Allah ya saka Masa da alheri ya biya Masa bukatunsa na alheri yadda ya faranta mana Allah ya faranta masa"

"Ameen ya Allah"

A ranar tare duk Muka ci abinci cikin tsananin farin ciki su Annur a kudin da aka basu har da siyo sababin takalma.

Abban Nusrah ma zan iya cewa rabon da naga farin ciki  haka a fuskarsa har na manta.

Bayan sallah isha mijin Nusrah yazo Suka tafi.

Addua kawai nake a raina Allah yasa Abban Nusrah ya cire wanan mumunan abin a  zuciyar sa har ga Allah naji dadi da naga baya fushi dani bana san abinda zai Kara sawa na mu yi fada.

Ko da muka kwanta a ranar bai neme ni ta baya ba ta hanyar da Allah ya hallasta miji ya nemi matar sa ya neme ni bayan ya samu nutsuwa ya bani hakuri akan na kwantar da hankalina bazai Kara tunanin nemana ta baya ba sai a yanzu ma ya ringa nadama da yayi tunanin gwadawa.

Har ga Allah naji Dadi rumgume da juna muka yi Bacci.

3am

Kabiru a hankali ya leka fuskar Sajeeda yaga tayi nisa a bacci.
Ya zare jikinsa daga nata ya sauko a hankali sabida Kar ya tasheta daga bacci.

Gefen gadon ya duba a hankali ya d'auko pant din ta ya kudundune a hannun sa cikin sanda ya fice daga d'akin yayi waje.

Yana zuwa yayi bayan gida ya d'auko tukunyar kasar da ya shigo dashi da ba Wanda yasan ya shigo dashi,ya saka pant din a ciki  ya fara surutan da aka ce yayi a hankali Yana waige waige duk da Yana da tabbacin ba Mai ganin sa dan a sharrudan ance Kar ya sake ya yarda a gan shi.

Yesmeen.

Bata da nauyin bacci ko kad'an ko ya taji motsi sai ta farka.
Motsin k'ofa yasa ta bude idonta.

Kafin taji Kamar takun tafiya a ta Bayan dakinta Inda ta mik'e zaune tare da dafe kirjinta cike da tsoro.

A hankali ta Mike ta leka ta window..........

MG'S SKINCARE

Dame akafiki yar uwata?
Kyan fatar ko iya gyaran fatar?
Ina riba g macenda t Maida kanta sauran mata?
Shin haryenzu labarinmu kikeji ko kike bayarwa?
Hajiyata miye matsalar?
Fatar takice abun se lahaula?
Kingwada kingwada harkinsare?

Tsakanida Allah yaushe daren yayi balle wayewar garin?

Inbakida labarin MG'S wacce tasanki tasansu,
Gawurtaccen Kuma shahararren kamfanin gyaran fatane,duk lalacewar jiki,duk hautsinewar fata,duk yenda jikinki yazama abun kunya gareki, Ina tallata maki me gabadaya,

Muntarkato,munwarwaro,munqullo duk wani Abu daze maidaki wanke hannu kataba mun qara a cikin kayayyakinmu,muncire,muntsife,munfidda,mun tantance mun hadamaku wasu irin hadaddun lafiyayyun kaya masu masifar goge fata,wallahi duk fitinar fatarki inshallah,kinzo bustop,kisiya kiyikyanda ko mace,kan juyo ta waiwayo ta dubi halittar Allah,

Ga product din kamar hka,
Sabulu 4k

Mg's beauty kit 14k
Herbal whitening soap
Body cream
Face cream
Scrub
Cleanser
Glow oil

Sannan akwai flawless skin beauty kit 16k

Tsakanida Allah kigafa
Duk wannan garabasar Kuma kinazaune hba taso a dama dake a harkar yar uwata,

Ayi hakuri da sauyin farashi komi yatashine muma b hka mukasoba
Chat:08062991549,07046881166,07067210195,
Call,+2348064532391
Instagram:glow_with_mgs
Facebook:mg's skincare

Team glow😍

*RUFAFFEN SIRRI*

*NA SADNAF*

*ADABI WRITERS ASSOCIATION*

*Page 3*

Ba abinda take iya hangowa sabida duhu,amma dai kamar mutum take hango wa tunanin ta kila barawone ya shigo gidan hakane yasa tayi sauri ta bar jikin window ta nufi k'ofar d'akin cikin sand'a ta bud'e a hankali dan so take ta je k'ofar d'akin Umman ta sanar musu,tana fitowa Kabiru ya shigo shi ma cikin sand'a,ganin Yesmeen yasa gabansa mugun faduwa dan daga shi sai gajeran wando,itama jikinta ne ya dau rawa cikin rawar baki tace "Abba motsi naji a bayan dakina Ina tunanin barawone ya shigo shine na fito na fada muku"

Sai a lokacin Kabiru ya dan saki ajiyar zuciya dan duk tunanin sa ta gan shi

"Ki koma nima motsin naji shi yasa na fito ba kowa Ina ga b'eraye ne"

Da sauri ta juya ta koma ciki ta rufe kofar ta ta saka sakata ta kulle ta Kara gyara labulen window ko da ta kwanta sai ta kasa komawa bacci dan zuciyar ta cike take da tsoro tunda Nusrah tayi aure take jin tsoron kwana ita kadai.

Kabiru kuwa Yana shiga d'akin yayi sauri ya kwanta a gefen Sajeeda yayi rigingine Yana kallon ceiling sai murmushi yake shi kadai dan a yau kawai da ya rabawa yayan sa kudi ya sauke hakkin da ya Kamata ace shi yake saukewa ba Sajeeda ba sai yaji wani irin farin ciki da ya dade bai ji irin sa ba,yana bakin ciki yaga yaran sun tsallake shi idan suna zaune sun tafi wajen Sajeeda suna Yar murya ta basu kudi har Kuma suka girman kallon babu suke masa dan sau tari zai ji suna mun san Abba bashi da kudi,abun na matukar Kona masa rai  zai iya cewa tunda yaran Suka dai girma ba Wanda ya tab'a tunkarar sa yace Abba ina san kaza kayi min kaza duk wajen Sajeeda suke zuwa,Wanda yasan sabida bashi dashi shi yasa basa tunkarar sa abin arzikin da zai ce yayi shine a lokacin Auren Nusrah ya dan tab'a abin arziki,amma komai dai Sajeeda ke yi Kuma bata tab'a nuna gajiyawarta  ko damuwa ba dan macece ita Mai zafin nema,a yau da yaga ya Sanya yayansa farin ciki yaji ya Kara kwadaituwa da ya samu kudin.

Abu daya ke damun sa a cikin dokokin da aka shimfida masa,na kin sallah na tsawon sati daya,yaso ya nuna bazai iya ba Rabiu ya dage Masa.

Haka yayi ta sake sake har aka Kira sallah Asuba Sajeeda ta mik'e zaune cikin hamma da adduar tashi daga bacci,shi kuwa yayi saurin rufe idon sa kamar
Bacci yake.

Sai da ta sauka daga gadon ta hau neman pant din ta dan zani kawai ta rufe jikinta dashi.

Ganin ta duduba wajen da ta kwanta bata gani ba sai tayi tunanin ko wajen da Kabiru ke kwance ya danne,hakane yasa ta hau tashin sa akan ya tashi yayi wanka Kar ya makara sallah asuba.

Kabiru kuwa kamar mai baccin ya mike Yana mitsitsika ido,ya mik'e tsaye ta janye bargon ta

hau duduba Inda ya kwanta bata gani ba sai gashi har zanin gadon ta cire,Kabiru kuwa ya San mai take nema Sarai hakane yasa ya shareta ya shige bandaki yayi wanka ya fito ko alwala bai yi ba ya nufi wajen kayan sa.

Sajeeda kuwa cikin mamakin rashin ganin wandon ta tace "Abban Nusrah kaga ban ga pant dina ba sai dubawa nake"

"Toh tsayawa Neman pant zakiyi ko Kuma wanka zaki Shiga sabida kar ki makara sallah asuba,kin wani daddage da nema kamar baki da wani"

"Ba haka bane Abban Nusrah kasan  yesmeen na shigowa d'akin tayi gyara Kar nazo taga pant akan gado Ko a wani wajen kaga da kunya ko"

""Umm ni dai na tafi massallaci sai ki dage da nema"

Yayi waje.

Sajeeda Kuma ta shige bandaki dan tayi wanka ta yanke idan ta iddar da Sallah sai ta gyara d'akin ko zata gani.

Kabiru kuwa yana fita ya labe daga waje Yana kallon lokacin da su Saifullahi suka fito daga gidan suka nufi massallacin.

Sai Kuma yaji kirjin sa ya masa nauyi Mai bambanci Arne da musulmi sallah ce fa, yanzu haka zai yi sati kenan ba saka goshin sa a kasa ba? tuna irin kudin da zai yi yasa ya ture tunanin a ransa dan a wanan yanayin da yake ciki kudi kawai shi ne burin sa dan Rabiu  yace masa Rabin masu kudin garin nan duk ta haka suka yi kudin su.

Sai da ya ga yaran sun dawo sun shige ciki shima ya fito daga lungun da ya b'uya ya Shiga gidan.

Koda ya Shiga daki Sajeeda ya Tarar ta daddage da neman pant da hijabin da tayi sallah a jikinta har zanin gadon ta canza sabida Neman da take shi kuwa ya hade rai dan ko da wasa baya so ya bata fuskaar da zata ishe shi da maganar pant din ta.

"Abban Nusrah kaga har daga katitar nan nayi wlh Babu pant ba dalilin sa"

"Mtsss kina da matsala wlh Tom mai Kika daddage kina nema daya ne dake"?

"Aa ba dayane dani ba Ina ta mamakin yanda zan kwana da abu a gefena yanzu na duba ko sama ko kasa bangani ba"

"Baki da abin yi ne Sajeeda ki cigaba da nema idan Kuma ba barawone ya shigo ya rasa mai zai dauka sai wandon ki"

Kabiru yace tare da Jan siririn tsaki,ya kwanta Yana zai koma bacci karfe goma ta tashe shi daga bacci zai je wajen abokinsa da ya bashi kyautar kudi yace masa yaje Yana san ganin sa.

Da toh ta bishi ta fito daga dakin tana tunanin kila wani wajen ma pant din yayi ta tsaya wahalar da kanta.

Tare suka yi abincin karyawa da Yesmeen dake bata labari taji motsi jiya a bayan windonta,ko baccin arziki bata yi  ba

Dariya Sajeeda ta saka mata ta ringa ce mata matsoraciya yanzu haka b'eraye ne.

Sajeeda

Tare muka ci abinci da Abban Nusrah da yazo fita ya bani Dubu biyar Wai nayi cefane har ga Allah daga jiya zuwa yau bansan kalar Farin ciki da Addu'ar da nayi wa Abban Nusrah ba, hakika ya kyautata wa nida yarana,dan ko da Abban su ya fita suka shigo hirar kyautar da aka musu kawai suke Annur kuwa ya hau cewa "Nayi mafarki Abba ya Zama mugun Mai kudi Wai ya  gina wani gidan bene duk muna ta murna amma ban ga umma a gidan ba"

Murmushi na saki Ina "idan baka gani a gidan ba wata Abban ku ya auro kenan,a lailai auta kyautar da aka ma ya maka dadi irin wanan mafarki haka.

Tare muka yi aikin abincin da aka kawo min da Yesmeen dan Kamar na mayar nima na dan huta tunda na samu Yan canji,dan daidaikun Rana ne baa kawo min aikatau Kuma har ya zame min jiki.

Da yamma Ina d'aki sai ga Abban Nusrah ya shigo gidan da sallama fuskar sa Kamar gonar auduga ba kowa a gidan sai ni kadai dan duka yaran sun tafi islamiya.

Nima ganin fuskarsa a washe yasa nima na washe bakina Ina "Abban Nusrah Mai muka samu ne naga fuskar ka d'auke da Annuri haka"

Zama yayi a gefena Yana "Sajeeda Ina ga mun kusa zama masu kudi"

"Allah Abban Nusrah abokin naka ya nemo ma aikin ne"?

"Daga wajen sa nake yanzu haka ai yanzu ma zama bai Kama ki ba tashi Zaki yi mu tafi ki

tayani yi masa godiya Kinga yau ma kudin daya bani kyauta Sajeeda"

Gwalo ido nayi a lokacin daya bud'e ledar dake hannun sa wrapper Dubu Dubu ne guda biyar,mik'ewa nayi na dafe kirjina Ina "Abban Nusrah duka wanan kudin ya baka aikin me yake yi haka"?

"Ke kinsan kudin sa kuwa wanan ai ba komai ne ma a wajen sa ke baki ga alkawarukan da yamin ba a ciki kuwa har da kyautar gida yace bazai manta alherin da na masa muna Yara ba"

Kudin daya dora a cinyata kawai nake juyawa har ga Allah sai najini a tsorace tambayoyi nake so na yiwa Abban Nusrah amma bana so na rusa Farin ciki da yake ciki,a wanan zamanin har wane irin kudine da shi haka jiya ya bashi kyautar dubu dari biyu yau Kuma ya d'auko dari biyar ya bashi.

"Wai ya na ga ba kya farinciki ne Sajeeda Allah ne ya turo min shi ya taimaka min fa Allah yasan  tsawon shekarun da na dauka Ina aikin wahala"

Murmushi yak'e nayi Ina "ba haka bane Abban Nusrah Mai zai hana ni murna kawai Ina ta mamakin yanda daga jiya zuwa yau ya iya baka kyautar dubu dari bakwai zugudum a wanan zamani ko dan uwan ka ke da wanan kudin ba lailai ya iya baka irin wanan kyautar ba"

"A wajen masu kudi kyautar dubu dari bakwai ba komai bane Sajeeda sabida dai bamu da kudin ne shi yasa kike ganin yawan kudin, ba za ki gane abinda na ke fada ba sai anjima idan mun je gidan Zaki tabbatar da ko miliyan daya ya bada kyautarsa ba zai ji komai ba"

"Allah ya saka masa da alheri"

"Ameen Ameen ai idan ya samo min aikin nan sai na siya miki tsalallen mota,su Saifullahi ma sai na bi su da motoci"

"Allah ya yarda yasa arzikin na alheri ne a gare mu Abban Nusrah kasan wani arzikin masifa ne,ni wlh a rayuwata rufin asiri kawai nake so bani da wanan burikan tashin hankalin indai zanci sau uku a rana yarana su kawo bukatar su na musu ba tare da na gaza ba wlh Alhamdulillah"

"Sajeeda kenan yanzu dai tashi kije ki boye mana kudin ki zo ki fada min Abubuwan da ake bukata a gidan"

D'aki naje na boye kudin na dawo wajen sa duk jikina a sanyaye bansan mai yasa ban ji Ina mugun Farin ciki ba shi kuwa sai zuba yake yana lissafa yadda idan ya samu kudi zai canja

mana rayuwa ko girki da na so dorawa hana ni yayi yace yau bazaa yi girki ba Kuma bai yarda na Kara karbar aikatau ba.

Koda Yara suka dawo haka ya tara su Yana tambayar su abinda suke so.

Tuni duk suka haukace da murna daga Mai cewa machine yake so sai Mai cewa keke yake so Annur kuwa sai tsalle yake Yana mafarkin sa ya tabbata Abban su ya Zama Mai kudi,Abban Nusrah kuwa sai washe baki yake Yana su Kara saka su a addua ai Yana ganin nan da sati biyu zamu bar gidanan.

Ni dai da ido nake bin sa yanda ya hakikance Yana zuba lissafi Taya mutumin da ba shi da ko asi sai ya fita yayi buga buga tashi daya ya ringa wanan lissafe liisafen sai Kuma nayi tunanin Allah Kan iya azurta bawan sa a dare daya zai Kuma iya talauta bawan sa a cikin mintuna.

Bayan sallah isha yace na shirya mu tafi gidan abokin na sa na masa godiya na so ya bari zuwa gobe ya dage mu tafi.

Haka na shirya cikin dogon hijabina na haye machine din sa mu ka dau hanya.

Ni dai ban san wajen da mu kayi ba kalle kalle kawai nake har mu ka iso wani wawakekken gida da aka masa ado da fitilu masu haske kamar ba dare ba.

Haka kawai na ji tsoro ya Kara rufe ni na hau sallati a daidai lokacin da ya kashe machine d'in na sauko yayi parking a gefe ya hau buga gate d'in.

Wani ne ya bud'e yana ganin Abban Nusrah ya washe baki Ya rusuna ya bashi hanya tare da masa sannu da zuwa, nidai tsayawa nayi daga baya Ina mamakin yanda Mai gadin yasan Abban Nusrah har yake wani rusunawa.

Sai da Abban Nusrah ya juyo ya nuna min hanya na Shiga gidan da bismillah  dan sai naji Ina karkarwa har Ina Jin sanyi na Shiga na.

Abban Nusrah kuwa kamar yasan gidan yayi gaba nayi saurin ruk'o hannun sa ya juyo Yana kallo na.

"Abban Nusrah tsoro nake ji ka ga girman gidan fa"

Nace Ina kalle kalle

Ya janye hannun sa Yana "mai abin tsoro ke dai kawai ki biyoni"

Kirjina na dukan uku uku na cigaba da bin sa a baya har Muka karaso wani k'ofar da

gabad'ayansa glass ne.

Abban Nusrah ya danna wani waje k'ofar ta bud'e da kan ta,ya shige nima nabi bayan sa Ina zare ido,dan tunda nake a rayuwa ta ban tab'a ganin irin Wanan gidan ba.

Ba kowa a palon Abban Nusrah kuwa ya samawa kansa wajen Zama ya nuna min kujera akan na zauna.

Ni kuwa rawar da jikina yake yasa na zauna a kasa.

Abban Nusrah ya d'auko wayar sa daga Aljihu Yana "gamu nan mun zo"

Daga haka ya mai da wayar cikin jaka.

Ni dai Sam ban ji hankalina ya kwanta ba dan Addu'a kawai nake a zuciya ta.

Takun da na jiyo yasa na daga kaina Ina kallon sama.

Wata mata ce mai kib'a fuskarta d'auke da murmushi bayan ta Kuma wani ne shi ma da kib'ar sa da Alama shi ne Abokin Abban Nusrah da matar sa sai naji hankalina ya dan kwanta har suka karaso wajen da mu ke.

Matar tace "Haba ya zaki zauna a kasa ki zauna a sama mana"

"Aaa nan ma yayi"

Duk yanda naso ta barni a kasa ki tayi har sai da na hau saman kujerun na hau gai da abokin Abban Nusrah da ya kura min ido ya na Kare min kallo.

Ku sha ruwa Mana"?

Matar sa tace dan suna Zama aka cika gaban mu da kayan ciye ciye ni dai tunda na zauna na rasa nutsuwa ta buri na kawai mu bar gidan.

Kaina a sunkuye naji Abban Nusrah na fada mi shi kawoni yayi na masa godiyar alherin da ya Masa.

A lokacin matar ta koma sama haka ne yasa na sauko daga Kan kujeran na hau Masa godiya cikin murmushi daya bayyana hakoran makkar sa yace "ba komai uwargida baxan iya biyan Kabiru alherin sa a gareni ba dan ya taimaka min sosai sabida ni maraya ne,abincinsa haka zai kawo mu raba dan na taimaka Masa ba wani Abu bane".

Godiya na Kara Masa yace ba komai ya Kara da "akwai wani gida da nake so na bar masa

kyauta dan  yace min gidan da kuke ciki ba naku bane haya ne,dan haka a satin nan ku fara shirye shiryen komawa na bar muku gidan halak malak,sannan zan d'auke shi aiki a company na zaa na biyan sa albashi miliyan daya kowane wata"

Tunda ya fara magana na saki baki Ina kallon sa dan gabad'aya ji nayi na girgiza da Abubuwan da yace zai yi mana.

Kamar an like min baki haka na ringa kallon sa Abban Nusrah kuwa sai godiya yake zuba Masa Yana ba komai.

Sai da Abban Nusrah ya kalleni na iya bud'e bakina Nima na hau masa godiya.

Ko da mu ka zo tafiya kudi ya d'auko Mai yawa ya miko min nak'i karba dan wlh wani irin tsoro naji ya Kara rufeni Kuma gabana bai bar fad'uwa ba idan dai na hada ido dashi.

Sai da muka fito na daga palon na fara samun nutsuwa nayi gaba na bar su a baya.

Kabiru

Yana ganin Sajeeda tayi gaba ya kalli Alhaji Rabiu yana "Kasan idan ba haka muka yi ba wlh haka zata tayi min tambayoyi"

"Nasan fa irin su haka sakeena ke da wanan taurin Kan,yanzu abinda za'ayi kayi k'ok'ari jibi ku koma gidan sabida ka fara aiwatar da abinda aka saka ka"

"Ba zamu wuce jibi ba"

Daga haka su ka yi sallama.

Sajeeda

Har muka isa gida Sam ban ji zuciyata ta kwanta da wanan sauyin rayuwar da muke neman samu ba hakane yasa sai da muka zo kwanciya nace "Abban Nusrah bansan Mai yasa hankali na bai kwanta da wanan canjin da muke neman samu ba,taya haka kawai zai d'auko gida sukutum guda ya mallaka ma dan kawai ka taimaka Masa Kuna Yara Anya mutumin nan ba dan yankan Kai bane?wane irin aiki zaka Masa da zai d'auko har miliyan daya ya baka a wata"a gaskiya!!

Wani irin tsawa ya daka min daya tilasta min yin shiru"Sajeeda dama bakya san na cigaba a rayuwata? kinfi so na dawwama a haka a talauci kina jinki kamar mai gidan tunda ke kike yin komai a gidan,kinfi so na zama kamar yaron ki ko? bakya so kiga na samu na kaina

Toh bari kiji na fada Miki da hannu biyu Zan karbi arzikin da ya tunkaroni idan Kinga bazaki iya ba sai kisan nayi"

Daga haka yaja dogon tsaki ya juya min baya.

Ko da na hau bashi hakuri inaso na fahimtar dashi nufina ko ta kaina bai bi ba.

A haka na kwanta a gefen sa ina sake sake da bacci barawo kuwa ya daukeni na hau Mafarki da Kabiru da abokin sa

Mafarki........

MG'S SKINCARE

Dame akafiki yar uwata?
Kyan fatar ko iya gyaran fatar?
Ina riba g macenda t Maida kanta sauran mata?
Shin haryenzu labarinmu kikeji ko kike bayarwa?
Hajiyata miye matsalar?
Fatar takice abun se lahaula?
Kingwada kingwada harkinsare?
Tsakanida Allah yaushe daren yayi balle wayewar garin?

Inbakida labarin MG'S wacce tasanki tasansu,
Gawurtaccen Kuma shahararren kamfanin gyaran fatane,duk lalacewar jiki,duk hautsinewar fata,duk yenda jikinki yazama abun kunya gareki, Ina tallata maki me gabadaya,

Muntarkato,munwarwaro,munqullo duk wani Abu daze maidaki wanke hannu kataba mun qara a cikin kayayyakinmu,muncire,muntsife,munfidda,mun tantance mun hadamaku wasu irin hadaddun lafiyayyun kaya masu masifar goge fata,wallahi duk fitinar fatarki inshallah,kinzo bustop,kisiya kiyikyanda ko mace,kan juyo ta waiwayo ta dubi halittar Allah,

Ga product din kamar hka,
Sabulu 4k

Mg's beauty kit 14k
Herbal whitening soap
Body cream
Face cream
Scrub
Cleanser
Glow oil

Sannan akwai flawless skin beauty kit 16k

Tsakanida Allah kigafa
Duk wannan garabasar Kuma kinazaune hba taso a dama dake a harkar yar uwata,

Ayi hakuri da sauyin farashi komi yatashine muma b hka mukasoba
Chat:08062991549,07046881166,07067210195,
Call,+2348064532391
Instagram:glow_with_mgs
Facebook:mg's skincare

Team glow😍

*RUFAFFEN SIRRI*

*NA SADNAF*

*ADABI WRITERS ASSOCIATION*

*Page 4*

Mafarki

A kwancen da nake naji motsin bud'e k'ofar dakina hakane yasa na bud'e idona sai naga abokin Abban Nusrah ya shigo da Jan zani daure a kugun sa hannun sa rik'e da tukunyar kasa,sai na Mik'e da sauri cikin tsananin tsoro na fara kwallawa Abban Nusrah Kira akan ya tashi,dan ba iya abokin nasa ne ya shigo ba har da wasu a bayan sa suma da tukunyar kasa a hannun su,ihu nake iya karfina na kasa d'auke idona daga kansu na Kai hannu na dan na tashi Abban Nusrah sai na ji baya gefe na har suka zagaye gadon da na ke kwance na cigaba da ihu Abokin Abban Nusrah ya fusgoni da k'arfi ya Kai hannun sa wajen zani na, na saka ihu!"

A daidai lokacin da naji an rik'e ni ana girgiza ni na bud'e ido na da sauri tare da mik'ewa zaune

kirjina na dukan uku uku a lokacin da na farka na ga ashe mafarki nake duk na jike da gumi,na Kankame Abban Nusrah da ya rik'e ni gam yana "lafiyarki kuwa"?

"Mafarki nayi Abban Nusrah innalillahi wa Inna ilaihi rajiun innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

Na cigaba da sallati Ina kallon k'ofar dakin mu dake rufe dan sai nake ganin kamar ba mafarki nake ba

"Kiyi Addu'a ki koma ki kwanta"

"Abban Nusrah mafarkin abokin ka nayi"

"Gwara da ki ka ce mafarki ba gaske ba ki koma bacci dan Allah"

Ya fara k'ok'arin cire ni daga jikin sa na Kara Kankame shi mu ka kwanta ahaka.

Mafarkin da nayi na nan daram a idona,ko kad'an ban runtsa ba dan gani nake ko Yaya na rufe ido zan ga sun shigo bansan Mai yasa nayi mafarki da abokin Abban Nusrah ba,Mai ma'anar wanan mafarkin da nayi.

Idona biyu har aka Kira sallah Asuba na tashi na daura alwala Abban Nusrah kuwa sai sakin munshari yake,a yanzu baya sallah akan lokaci sai nayi ta tashin sa kafin ya tafi massallaci.

Duk tashin da na masa bai tashi ba da na dame shi  ma tsawa ya daka min hakane yasa na rabu dashi nayi Sallah ta ina ta mamakin canjin da nake gani a tare dashi,sai Kuma na tuna wai abokinsa yace zamu bar gidanan take naji wani irin tsoro da fargaba ya rufeni da na tuna mafarkin da nayi dashi,jikina na gaya min mutumin nan baa a banza zai taimake mu ba bansan mai yasa jinina bai d'auke shi ba ko dan na saka shi a raina shi ya sa nayi irin wanan mafarkin dashi.

Har na fito Muka hada abincin karyawa da Yesmeen zuciyata cike take da tunani har sai da Yesmeen tayi ta tambaya ta mai ke damuna nace mata ba komai.

Karfe tara da rabi su Saifullahi suka shigo dan su karya fuskar su a washe,Annur kuwa ya zauna a gefe na bayan duk sun gaisheni yace "Umma nifa yanzu kullum sai nayi mafarki Abba yayi kudi"

Da sauri na daga masa hannu Ina "ka ringa mana Addu'ar idan alheri ne kudin Allah ya tabbatar mana"

"Ai yama tabbatar in Sha Allah yaro babban ka ya zama Mai kudi,Umman ka ke so mu cigaba da zama a talauce ba cigaba"

Naji maganar Abban Nusrah a baya na na waiga Ina kallon sa a daidai lokacin da ya iso gefena ya zauna fuskar sa d'auke da murmushi Yana amsa gaisuwar da suke Masa.

Ya janyo faranti ya fara zuba dankali yana cigaba da magana "Saifullahi Kai da Faisal yanzu idan muka gama karyawa zamu je ku rakani gidan da abokina ya bar min kyauta nasan zaku ga kwana biyu na dan samu kudi,wani aminina ne tun muna primary Allah ya hada ni dashi Mai kudine sosai hakane yasa yace zai taimaka min yanzu haka jiya nida mahaifiyar ku mun je jiya ta masa godiya ba iya kyautar gida kawai yace zai min ba har aiki zai bani a companyn sa zaa ringa biyana miliyan daya duk wata"

Ihu Suka saka gabad'aya suka hau murna har da tsalle Yesmeen itama sai murna take

"Abba yanzu kana nufin sabon gida zamu koma Wanda yafi wanan"?

Saifullahi yace cikin tsananin murna da farinciki

"Sabon gida zamu koma ai zamuje kuga gidan daga nan ma sai muje ku masa godiya"

Murna kawai suke Yesmeen kuwa jiki na rawa ta d'auko wayarta ta Kira Nusrah ta hau labarta mata naji itama ta saki ihu ta cikin waya tana zata zo gidan.

Nidai da ido kawai na ringa bin su banji Ina murna ba na rasa dalili hakika cigaba ne yazo mana Wanda ban tab'a tunani ko mafarkin sa ba amma na rasa mai yasa naji a madadin naji ni cikin Farin ciki nake Jin akasin haka  har ga Allah bana san mu bar gidanan abokin Abban Nusrah sam bai kwanta min ba Ina addua Allah yasa tarayyar su ya  zame Mana alheri.

Yaran ko ta kaina basu Kara bi ba suka yi waje duuu dan Abban Nusrah ma cewa yayi duk suzo su tafi suga gidan.

Basu dawo gidan ba sai wajen laasar bakin su Kamar gonar auduga sai labarta mun kyaun gidan suke da haduwar sa ,suka d'auko Dubu hamsin suka bani akan abokin Abban su ne ya basu kyauta,sai fadar kirkin shi suke suna murna wai Abban su ya zama Mai kudi nidai ban iya ce komai ba sai dai sake sake a zuciya dan ban samu fuskar ma da zanyi wata magana ba.

Sai da muka zo kwanciya Naga na kasa jurewa dan Abban Nusrah cemin yayi a gobe goben nan zamu tashi mu bar gidan Kuma baza mu dau komai ba dan akwai komai a gidan

Duk da nasan magana ta zata b'ata masa rai haka na daure na fara magana Ina "Abban Nusrah daga haduwar ka da abokin nan naka ina ga ko sati ba'ayi ba har a cikin Yan kwanakin nan ya maka irin wanan alherin har dasu kyautar gida Abban Nusrah Kar idon mu ya rufe ya Kamata muyi bincike a kansa kafin mu koma gidan da ya bamu,ya Kamata mu tabbatar da irin sana'ar da yake yi  saboda mu samu kwanciyar hankali wlh zuciyata bata dauki wanan abokin naka ba

tsoro nake ji Kar ya zama bata hanyar halak yake samun kudin sa ba Abban Nusrah"

Rabiu yace Yana kada mukulin hannun sa

Kabiru yayi saurin gyada kansa Yana "ka bani shawara Rabiu bana so na Kara kwanciya da Kare wallahi Allah hankalina ya tashi da yadda naga gaban Sajeeda na fitar da ruwa mai doyi baka ga yadda ta zabge ba, bana so Sajeeda ta dagoni"

"Ka Kara Aure kawai abokina kayi auri yarinya da zata maka biyayya ka ringa samun abinda kake so a jikinta, idan ka gama morarta sai ka saketa,haka zaka yi tayi,har ka tsalleka wanan matakin kazo namu matakin"

"Ko Zan Kara Aure Rabiu ba yanzu da Sajeeda take Kan ganiyar rashin lafiyarta ba Kamata

yayi na bari a dan kwana biyu sai na bijiro da zancen Karin aure amma Ina fito da maganar aure yanzu zata zargi dan larurar da take ciki ne"

"Toh shikenan sai ka san nayi ai ba dai a so ka tsallake duk sharadin da aka baka"

"Yanzu dai abinda za'ayi kafini sanin Yan mata Yan matan nan ka zaka nemo min na samu nayi na watan nan inyaso nan da wata biyu sai na bijiro da maganar Karin aure kaga ba mai zargina ba abinda yanzu yake daga min hankali sama da wanan wankan karfe dayan da zan nayi a bayan gidan da yayar Sajeeda bata gidan da bani da matsala tunda Yesmeen bata gani"

"Mai zai hana toh ka canza mata daki,maana tunda Sajeeda yanzu ba lafiya gareta ba sai ka nemi ita yayar ta ringa kwana da ita kaga da haka zaka samu ka yi abun ka.

Sai a lokacin Kabiru ya dan samu nutsuwa shawarar da Rabiu ya bashi.

Basu rabu ba sai da Rabiu ya nemo Masa Yan mata biyu ta hanyar irin Yan matan da yake muamalla dasu,suna zuwa Suka tsadance daya Bayan daya zai neme su saboda san abun duniya duk Suka yarda suna ganin yawan kudin da zasu samu, Kabiru kuwa ya shige bandaki ya shafa maganin sa ya fito.

Bai samu ya koma gida ba sai wajen sha daya na dare.

Koda ya Shiga gidan Yaya Abu kawai ya tarar a Palo tana kallo,Yana Jin muryar su Saifullahi daga d'akin su.

Sai da suka gaisa da yaya Abu ya shige d'akinsa sai da yayi wanka ya fito yana jin sa a cikin nishadi,batun sallah kuwa babu,dan yanzu idan akwai abinda ke Masa wahala bai wuce sallah ba,dan ba  kowane lokaci yake yi ba,yau ba karamin dadi yaji da Yan matan da Rabiu ya hada shi dasu ba,har ga Allah daya daga cikin su ta kwanta masa Husna ya samu yadda yake so,dan har lambarta ya karba dan ji yayi ma zai iya aurenta bata fi sa'ar Yesmeen ba.

Koda ya fito d'akin Sajeeda ya shige dan ya dubata.

Sajeeda

Mafarkin da nayi  ya tsaya min a zuciya dan kasa ma samun nutsuwa nayi,sai da na saka Saifullahi ya ruko mun hannun Yesmeen ya kawota d'akina, daga mafarkin nan da nayi nasan cewar dagani har Yesmeen muna cikin mugun hatsari nama Shiga hatsarin tunda Kabiru ya gama dani, Yesmeen na ganin Saifullah ya bar d'akin tayi saurin Mai do da fuskarta kasa tana "Umma ya jikinki"?

Sai na cije lebbena dan ni kadai nasan mai nake ji a jikina dan yanzu kasana ma ji nayi Yana

numfashi shi kadai,

"Umma dan Allah dan Annabi karki nunawa Abba kinsan komai wallahi dazu ma sai da ya zo har dakina ya shakeni ya Sha alwashin kasheni idan har sirrinsa ya fita Umma wallahi Abba zai iya kasheni ki taimaka min ki rufe sirrin nan, mu dage da Addu'a da saukar Qur'ani, in Sha Allah zaki warke idan guduwa ma zamu yi sai mu gudu"

Girgiza kaina nayi ina "Yesmeen ranki da nawa a hannun Allah yake yau ko mutuwa nayi,lokacina ne yayi,ji nake idan ban tona sirrinsa ba bazan samu kwanciyar hankali ba,dan ya fara tunani tura su Saifullahi kasar waje,idan har zai iya mun wanan cutar ya kurmantar da Annur dan ya siyar da su Saifullahi ba wahala zai Masa ba gwara na nuna masa nasan sirrin sa"

Yesmeen zubewa tayi a gabana ta hau magiya sai kuka take tana na rufa mata asiri Abban nusrah kasheta zaiyi idan na nuna masa nasani

Na ruko hannun ta Ina "Ki kwantar da hankalin ki bazan nuna Masa ke Kika fadamin ba,ba Kuma magana Zan Masa ba da kaina nake so na gano sirrin sa ya Kuma san cewar nagani din ba fada min aka yi ba da naso na fadawa su Saifullahi sirrin sa dan su san cewar zai iya yin kudin dasu suma amma na fasa fada musu zan dai hana tafiyar tasu"

Yesmeen magiya kawai take akan na rufa Mata asiri sai da na rantse mata akan bazan fada masa komai ba ta samu nutsuwa dan na yanke abinda zan yi bazai tab'a zargin Yesmeen ce ta fada min wani abu ba.

Bayan fitar Yesmeen daga d'akin Yaya Asmau ta shigo na fada mata ta bar Yesmeen ba sai ta tafi da ita ba Yaya Asmau tafi nuna kulawar ta a kaina akan wacce na Kira da yayata ni gani nake ma Kamar murna take da rashin lafiyata tunda duk zata yi abinda ranta ke so.

Ba Mai hanata.

Kafin Yaya Asmau ta koma dakinta na Kara rokonta akan ta saka mallamai suyi min Addu'a da sauka tamun alkawari da zata saka ayi min Addu'a.

Ba ta  kuwa bar dakina ba sai da ta tabbatar da naci abinci Yaya Abu bata lekoni ba sai wajen goma ta shigo tana har yanzu bata ga Abban Nusrah ya dawo ba dama yana dadewa hakane"?

Kai kawai na gyada mata.

Ta sa Kai ta fita.

Tana fita na fara susa dan wani irin kaikaiyi naji kamar na cire gabana na Yar ga ruwan dake bulbulo min duk wanan masifar uban yayana ne ya jefani saboda abin duniya.

Haka na kwanta Ina zubar hawaye idan ya lafa na daina idan ya motsa na cigaba da susa,Ina Jin lokacin da Abban Nusrah ya dawo na dauka zai lekoni sai naji shiru Wanda hakan na nufin dakinsa ya wuce sai da ya dau tsawon lokaci naga ya turo k'ofar d'akin ya shigo sanye da jallabiya kudin haram sun zauna masa dan har wani kiba yayi Yana sheki.

Ya zauna a gefen gadon Yana "Sannu Sajeeda ya jikin naki"?

Mik'ewa nayi na zauna Ina "Abban Nusrah dare daya na wayi gari da wanan masifar  a jikina,a ranar da na fara Jin canji a jikina a ranar da ka kusanceni ne na karshe Abban Nusrah shekara ashirin da doriya muna tare Kai ma kasan ban taba cuta makamancin wanan ba,Mai zai jawo min wanan masifar"?

Wani irin kallo ya fara min cikin hade rai ya fara magana Yana "Toh mai kike nufi da tunda na kusance ki na karshe kika ji jikinki ya canza kina nufin ni na saka Miki cuta ko me?idan a jikina kika kwashi wanan cutar ni zaki gani haka ne,wanan cutar kila a bandaki Kika kwaso ko a wani wajen dan haka ki cigaba kawai da Shan magungunan da aka Rubuto miki Zaki warke a hankali kinci abinci"?

Ba karamin daurewa nayi na danne abinda nake ji ba,na gyada masa Kai da naci abincin ya fara magana Yana "Ina ganin ya Kamata Yaya Abu tazo ta ringa tayaki kwana ni sai na ringa kwana a dakina har zuwa lokacin da zaki warke"

"Tun baaje koina ba Abban Nusrah ka fara guduna kenan bazaka iya kwana da ni waje daya ba"?

"Aaa Sajeeda akan me Zan gujeki,kawai Ina ganin a yanzu kina bukatar kulawa sosai,shi yasa nace tazo ta ringa kwana anan ai na dan lokacine"

"Abban Nusrah bana so Yaya Abu tazo ta kwana Kai nake so ka kwana din idan Kuma dan larurata zaka ki kwana dani shikenan ba komai"

Nace Ina Jin kamar na shako shi har sai ya daina numfashi so nake na Kama Abban Nusrah da kaina shiyasa nake so mu ringa kwana waje daya.

Kabiru kuwa ganin Sajeeda ta dage yasa yace zai kwana din zuciyar sa fal da tunanin yadda zai gudanar da abunsa ba tare da su Yaya Abu sun gan shi ba.

Haka ya ringa sintiri daga dakinsa zuwa na Sajeeda Yana tunanin yadda zai yi,bai san mai yasa wankan sai a bayan gidan zai yi ba ji yake Kamar ya taso su Yaya Abun yace su koma dakinsa su kwanta.

Haka yayi ta juye juye har Sha biyun  na dare Yana Jin saukar numfashin Sajeeda dake nuni tayi nisa a bacci,a hankali ya lekata ya ga baccin dai take cikin sand'a ya mik'e ya fito daga d'akin.

Ya nufi bakin k'ofar d'akin Yesmeen ya Kara kunnensa Dan yaji ko zai jiyo motsin su ba abinda yake ji sai karar fanka.

Cikin sand'a ya koma dakinsa ya jawo tukunyar kasar da ke d'auke da ruwan maganin ya tube Zigidir Yana jira daya ta karasa yayi waje yayi wankan.

Sajeeda
Duk abinda yake yi Ina kallon sa rufe idona kawai nayi Kamar Mai baccin Yana fita na bud'e idona kila wani abun zai aikata tunda Yesmeen tace na ringa fitowa karfe biyu na dare Zan ganewa idona.

Gabana faduwa kawai yake a lokacin da na mik'e tsaye Ina Jin kamar na Fadi saboda rashin kwarin jiki cikin sand'a na isa bakin k'ofar Ina lek'e ta ramin mukulin k'ofar.

A Kan idona yazo ya fito daga d'akin sa tsirara da wani bakin tukunyar kasa a hannun sa,tuni naji jikina ya dauki wani irin rawa dan duk abinan labari Yesmeen ta bani ban taba gani da idona ba a yau zan gan shi da idona.

Numfashina kamar ya d'auke haka na rik'e kirjina har sai da ya fice na bud'e k'ofar dakina a hankali na fito Ina Jin kafafuna kamar bazasu iya d'aukana ba.

A haka nayi waje na labe Ina sauke numfashi Kamar Mai cutar Asma,yadda naga Abban Nusrah a tsirara ya matukar daga min hankali

Sai da nayi minti goma a labe kafin nayi bayan gidan a hankali Ina Jin jiri na neman zubar Dani.

A tsaye yake a bayan gidan tsirara Ya daga tukunyar kasar sama ruwa na zuba a jikinsa can gefe Kuma wani tukunyar kasa ne da wutar kyandir.

Kallon Abban Nusrah kawai nake Ina k'ok'awa da numfashina a lokacin da kowa ke bacci shi ya fito Yana tsafi duk akan duniya.

A haka Zan tsaya har sai ya gama nafi so ya gani da idonsa ya tabbatar da idona na ganshi ba Yesmeen ce ta fadamin ba.

Dafanin da naji anyi ta baya yasa na bud'e baki dan na saki ihu.....

*Karku manta da saka yar uwata a adduar ku Allah ya kubuto ita ya tsare mata mutuncinta ameen*
*ZAN KOYA MIKI YADDA ZAKI HADA TURAREN WUTA KYAUTA SBD KISAMU ABINDA ZAKI DOGARA DA KANKI KIYIMIN MAGANA TA WANNAN NUMBER 08144679009*

*HUMKAM INCENSE GIDAN KAMSHI DA GYARAN JIKI*

MATAR DA HAIHU MUNTANADAR WANI PACKAGE MAI TAKEN TUNA BAYA RANAR FARKO DARE DAYA MAI DUMBIN TARIHI

*MUNA GYARAN JIKIN AMARE SOSAI MUNA SAIDA TURARUKA DA MAGANIN MATA MASU KYAU DA INGANCI*

KANAWA KUZO HUMKAM TA *ZAN KOYA MIKI YADDA ZAKI HADA TURAREN WUTA KYAUTA SBD KISAMU ABINDA ZAKI DOGARA DA KANKI KIYIMIN MAGANA TA WANNAN NUMBER 08144679009*

*HUMKAM INCENSE GIDAN KAMSHI DA GYARAN JIKI*

MATAR DA HAIHU MUNTANADAR WANI PACKAGE MAI TAKEN TUNA BAYA RANAR FARKO DARE DAYA MAI DUMBIN TARIHI

*MUNA GYARAN JIKIN AMARE SOSAI MUNA SAIDA TURARUKA DA MAGANIN MATA MASU KYAU DA INGANCI*

*INA MATAR DA KE FAMA DA INFECTION MUN TABADAR MUKU MAGANI SADIDAN WANDA DA ZARAN KIN FARA AMFANI DASHI ZAKIJI YADDA ZAKI FITSARE WANNAN SANYIN INSHA ALLAH*

MUNADA TURARUKA MASU SIRRIKA NA MATAN AURE  KAMAR SU

*HATSABIBIYAR TURARE*
*NI DA MIJINA*
*SAI KABIYONI*
*SHU'UMAR HUMRA*
*BITA ZAIZAI*
*DARE DAYA WANKA GOMA*
Hmmm wadannan pls banda yan mata matan aure kadai zanbasu duk budurwar da ta siya ta shafa babu ruwana
08132506044

OTHER ROOM WANNAN TURARE MAI SUNA OTHER ROOM BA NORMAL TURARE BANE

SIRRIKAN DA KE CIKINSA BAYANIN SAIDAI MU HADU TA PRIVATE

*INA BUDURWAR DA JARABAWA TA FAD'A MATA MUNTANADAR MINI WANI SET MAI SUNA BACK TO VIRGIN 08132506044*

*MAGANIN MATA MUNA SA KURMA KUWWA,SATA SHAKAF,GUMBA TSUMI ZUMA DA SAURAN SU HAJIYA INDAI MATSI KIKESO KISAI BACK TO VIRGIN*
*INA MATAR DA KE FAMA DA INFECTION MUN TABADAR MUKU MAGANI SADIDAN WANDA DA ZARAN KIN FARA AMFANI DASHI ZAKIJI YADDA ZAKI FITSARE WANNAN SANYIN INSHA ALLAH*

MUNADA TURARUKA MASU SIRRIKA NA MATAN AURE  KAMAR SU

*HATSABIBIYAR TURARE*
*NI DA MIJINA*
*SAI KA BIYONI*
*SHU'UMAR HUMRA*
*BITA ZAIZAI*
*DARE DAYA WANKA GOMA*
Hmmm wadannan pls banda yan mata matan aure kadai zanbasu duk budurwar da ta siya ta shafa babu ruwana
08132506044

OTHER ROOM WANNAN TURARE MAI SUNA OTHER ROOM BA NORMAL TURARE BANE
SIRRIKAN DA KE CIKINSA BAYANIN SAIDAI MU HADU TA PRIVATE

*INA BUDURWAR DA JARABAWA TA FAD'A MATA MUNTANADAR MIKI WANI SET MAI SUNA BACK TO VIRGIN WANNAN SET DIN ZAKISHA MAMAKIN YADDA ZAI HADE JIKINKI GAMGAM.  08132506044*

*MAGANIN MATA MUNA DA KURMA KUWWA,SATA SHAKAF,GUMBA TSUMI ZUMA DA SAURAN SU HAJIYA INDAI MATSI KIKESO KISAI BACK TO VIRGIN*

*WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE 30-35*

Dafanin da naji anyi yasa na bud'e baki dan na saki ihu dan na mugun tsorata sai naji muryar Yesmeen dake k'ok'arin rufe min baki cikin muryar Rada tana "Umma kizo ki koma ciki karki bari ya ganki"

Sai a lokacin na juya Ina kallon ta cikin mamaki,ita kuwa ta hau waige waige tana k'ok'arin Jan hannuna dan mu koma ciki,ni kuwa na fara k'ok'arin fusge hannuna Ina kallon Abban Nusrah da ya gama watsa ruwan ya ajiye tukunyar kasar nima kasa nayi da muryata na fusge hannuna Ina "Yesmeen ki koma ciki nafi so yagani saboda yasan nasan sirrinsa a yanzu mai ya fito dake"?

"Umma idan Kika bar shi ya ganki wallahi zai dauka ni na fada miki Dan Allah kizo mu koma ciki,ki Rufa min asiri Umma"

Yadda naga jikinta na rawa cikin tsoro yasa na bi bayan ta dan Jana kawai take a haka muka koma ciki tayi saurin shigewa dakinta na bita da kallo Ina mamakin ya akayi ma ta ga fitowa ta,sai Kuma na tuna tace bata fiye bacci ba tunda ta gano sirrin Abban Nusrah ko tsoron su Yaya Abu su ganta bata ji,a haka na koma dakina ba dan zuciyata na so ba,amma na riga na yanke a raina sai na nunawa Abban Nusrah nasan sirrin sa.

Ko da na koma d'aki kwanciya nayi Ina jiran ya shigo d'akin

Dama fitilar d'akin a kashe take,Koda ya dawo dakin cikin sand'a Ina kallon shi,har ya iso gefen gadon ya kwanta a hankali Yana leka fuskata,idona a bud'e yake hakane yasa Muka hada ido dashi ya ja da baya da sauri da alama ya tsorata ni kuwa nace "Abban Nusrah Ina kaje daddaren nan"?

"Dama idonki biyu"?

"Tun dazu na farka dan nayi fitsari sai naga baka d'akin har dakin ka na duba naga ko can ka koma saboda kana kyankyamin kwana kusa dani"

A dan duburburce ya fara magana Yana "Motsi naji a can waje shine naje na leka kinsan na fada miki barayi su addabi unguwar nan taya zan yi kyankyamin ki Sajeeda"

Ya kwanta nesa dani,ya juya min baya,na zubawa bayansa ido Ina tunani
Har ga Allah so nake nace masa karya yake yi bayan gida yaje yayi tsirara Yana wanka har yanzu ban dawo daidai ba da yadda na gansa tsirara duk tsawon lokacin nan ban taba sanin

farkawar da nake daddare naga baya d'akin ashe abinda yake  fita ya aikata kenan.

Haka na matsawa kaina da tunanin hanyar da ta dace nabi wajen nuna Masa nasan sirrinsa naga Yesmeen a tsorace take,mafarkin Kuma da nayi ya tsaya min a zuciya,ya zama dole na tonawa Abban Nusrah asiri.

Bazan biyewa Yesmeen Ina rufe sirrin mugu azzalumi ba.

Daidai da Sallah ma na kasa tashi nayi na taimakawa kaina da Addu'a dan wani irin zazzabi ne a jikina,wajen karfe hudu naji jikina ya dauki wani irin kaikaiyi da mugun zafi,bansan lokacin da na mik'e zauna na fara sallati Ina sosa ko'ina na jikina ba,kasana kuwa sai bulbulo da ruwa yake Mai doyi, Abban Nusrah kuwa ya farka daga baccin da ya fara d'aukar sa ya kalleni yana "Jikin ne Sajeeda sannu bari na dauko miki magani"

Ya mik'e ni kuwa na cigaba da sosa jikina da naji kamar wuta ake huramin,yanzu ba iya kasana nake jin kaikaiyin ba duk jikina gabad'aya.

Kuka kawai nake Ina Kiran Sunan Allah,ko maganin da Abban Nusrah ke miko min ban iya karba ba,kafin gari ya karasa wayewa jikiina yayi wani irin rudu rudu ya canza kala Kamar ba na mutane ba.

Kabiru

Hankalin sa ba karamin tashi yayi da yadda yaga jikin Sajeeda ya koma ba dan tuni duk fatar jikinta yayi wani irin duhun kala a idonsa ma sai yaga kamar fatar jikinta ya koma kalar Karen da ya sadu dashi, sallati kawai yake a ransa Yana tunanin abun yi dan shugaban su bai fada masa duk haka Sajeeda zata dawo ba,gashi yace ba abinda zai iya yi a akai haka Sajeeda zata tayi ta fama,da alama Sajeeda dak'yar ma take numfashi, hankali a tashe ya koma dakinsa ya d'auko wayarsa ya Rabiu a waya Yana d'auka ya fara zayyana mishi abinda ke faruwa,Rabiu kuwa ya hau tsara masa abinda zai yi da zai kau da zargin komai a zuciyar Sajeeda,ya kashe wayar ya turo Masa  lambar Wanda zasu je wajen sa da bakin su ya zama daya.

Kabiru kuwa kamar gaske ya koma d'akin Sajeedan da ta daina ma iya sallati sai hawaye da numfarfashi da take faman yi,

Haka ya taso Yaya Abu akan tazo su Kai Sajeeda wani asibitin.

Yaya Abu kanta sai da ta tsorata da yadda jikin Sajeedan ya koma, tafiyar mintuna Suka iso wani karamin asibiti  batare da b'ata lokaci ba likitan da Kabiru ya Kira ya hau duduba Sajeeda, Kabiru da Yaya Abu na zaune suna kallon sa har ya gama ya fita.

Sajeeda

Kukan zuci kawai nake dan nasan tawa ta Kare ,ta k'arfi nakeso na damko Yaya Abu na fada mata Kabiru ne ya jefani a halin nan amma na kasa magana dan ji nake jikina Kamar ba nawa ba,abinda yake bani mamaki da Kabiru yadda ya nuna damuwar sa kamar bashi yayi kudi dani ba,har da dan hawayen sa yau daa ce bansan sirrinsa ba cewa zanyi nafi kowa dace da samun miji Mai kaunata dan Yaya Abu sai kwantar Masa da hankali take saboda ya kasa Zama waje daya duk wanan abin fa yasan asibti bazasu iya min magani ba, amma saboda ya nuna bai San komai ba yake ta sintirin kawo ni asibiti,Koda likita ya dawo bayanin da naji Yana yiwa Kabiru da Yaya Abu yasa hawaye ya fara gudu a fuskata,Wai a fadar likitar da nake tunanin hada baki yayi dashi Wai wani kwauro ne ya cijeni,wanda cizon kwaron guba ne,gubar ne ya haifar min da wanan kaikaiyi da canza fatar har ruwan dake zubo min a jikina,matsalar Kuma wanan kwaron ba lailai ko na Sha magani na warke ba sai dai ayi ta adduar sauki na ringa Shan magunguna akai akai, Abban Nusrah  da Yaya Abu kuwa sai sallati suke, Abban Nusrah har da hawayensa Yana rik'e likita Wai ya taimaka masa idan da akwai abinda zai iya yi akai,likita kuwa yace ba abinda zai iya Yi akai ya cigaba da bawa Abban Nusrah hakuri akan ya daina daga hankalinsa kawai ya maida hankalina sa wajen kula dani kila a gaba a dace na warke.

Abban Nusrah a tunanin sa bansan sirrinsa ba haka yayi ta min sannu Yana rike da hannuna har ruwan da aka samun ya Kare aka sallame mu bayan ya lafto uban magunguna Yaya Abu kuwa sai cewa take wane irin kwarone haka ita dai bata tab'a ji ba.

Abban Nusrah kuwa ya hau ce mata akwai yasan ma wata da ya ciza.

Haka muka dawo gida, Abban Nusrah ya ringa kula dani,Yana wani tattalani,ni kuwa kullum jikina Kara rikicewa yake a yanzu ko tashi bana iya yi, adduar zuci kawai nake dan wani irin rama nayi,ba abinda kake hangowa a jikina sai kasusuwana,jikina kuwa na ta fidda ruwa mai doyi,yanzu Abban Nusrah bama ya iya kwana a dakina,amma idan garin Allah ya waye kafin ya fita haka zai ta kula dani,har da dan kukansa wai duk ya nuna ya damu da halin da nake ciki,Yaya Asmau kuwa kullum sai ta kirani,ta dubani,ta Kuma shaida min ta saka a ringa min Addu'a ana min saukar ita tafi yarda da makiya ne suka jefe ni ba wani kwauro daya cijeni,daidai da mahaifina da mahaifiyata sai da suka zo dubani,ba Wanda zai  zo dubani bai girgiza da yadda na dawo ba,duk Wanda ya tambayi Mai ya sameni haka,Abban Nusrah da Yaya Abu sai su hau bayanin kwaro ne ya cijeni shi yasa na dawo haka, tunda iyayena suka zo nake Neman hanyar da zan  fada musu sirrin Abban Nusrah ko Zan samu su tafi dani su nemi mallamai su mun Addu'a,bansan Kuma ta yadda zan fada musu ba dan bana iya magana bansani ba ko wani abu Abban Nusrah yamin da ya saka naji bana iya magana, fadar tashin hankalin da iyayena suka Shiga da halin da nake ciki bata bakine dan mahaifiyata Gwaggo tunda tazo bata da aikin da ya wuce kuka,a gaban idonsu kuwa Abban Nusrah sai Kara kula dani yake, duk dan ya nuna musu Yana kula dani,

Na lura so take ta kebbe dani,amma ganin Abban Nusrah yasa ta kasa sakin jikinta tana dubani sai ta fita,mahaifina kuwa kwana daya kawai yayi ya koma,akan zai Nemo min maganin

gargajiya kila a dace, ana sauran kwana biyu mahaifiyata ta koma Abban Nusrah ya fita da zumar wai zaije ya dawo akwai kayansu da ya iso da zai je ya gani bazai Dade ba zai dawo.

Fitarsa da minti biyar sai ga mahaifiyata ta shigo fuskarta cike da damuwa ta zauna a gefen gadon tana Kare min kallo hawaye ya hau zubo mata tana "Sajeeda Kinga yadda kika dawo kuwa?Wane irin kwarone wanan da zai cijeki ki koma haka,har cizon sa yasa kiringa fitar da ruwa mai wari haka daga gabanki?Wai me ke faruwa da ku ne haka?ya akayi Yesmeen ta makance?mai ya kurmantar da Annur,?na kasa gane Mai ke faruwa da ku haka,na tambayi mijinki yace dare daya kuka wayi gari Annur ya daina iya magana Yesmeen Kuma ta daina gani,duk a cikin shekara daya wanan masifar ta same ku haka mai yake faruwa haka?

Gwaggo ta sosa min inda yake min kaikaiyi na hau k'ok'arin na bud'e bakina dan nayi magana amma na kasa alama kawai nake Mata da hannu dan a Kira min Yesmeen ko zan samu ta fadawa mahaifiyata abinda ke faruwa bani da sama da ita,ita zata iya taimaka min na fita daga hannun wanan azzalumin,amma mahaifiyata ta kasa ganewa sai kuka ta saka min tana adduar Allah ya bani lafiya tana Shan alwashin daina bacci dan addua kawai zata ringa min,karshe sai Yaya Abu ce ta shigo d'akin,ta ajiye kumatu tayi jajjir da ita saboda Jin dadin da ta samu da alama rashin lafiyar da nake Dadi yake mata dan tamkar ita ta Zama matar gidan,ita ke girki,ta ajiyewa Abban Nusrah nasa,duk abinda ranta keso kawai take yi, kafin Gwaggo tazo ma sai ta kusa yini bata lekoni ba sai dai naji muryarta a Palo tana dakawa su Annur tsawa.

Ina ji Ina gani haka mahaifiyata ta tattara ta koma bansamu bakin yi mata magana ba.

Tsawon wata uku sai dai a kwantar Dani a tayar,Yesmeen sai dai ta faki idon Yaya Abu da na Abban Nusrah idan baya Nan ta shigo dakina ta dubani,idan Ina bukatar wani abu sai tamin kafin ta tafi,Nusrah ma haka ta ringa sintirin zuwa dubani,Ina ji Ina gani bani da bakin magana Abban Nusrah ya tattara Saifullahi da Adnan suka fita waje karatu,duk da halin da nake ciki yasa Suka nuna basa san zuwa amma Abban Nusrah haka ya tilasta musu Suka tafi suna hawaye suna min Addu'a samun sauki.

Sati biyu da tafiyar su Abban Nusrah yasa aka zo aka fara kwashe kayan mu wai zamu koma Abuja.

Yaya Abu kuwa sai murna take tana wani shishigewa Abban Nusrah Kamar wata matar sa .

Ranar lahadi Abban Nusrah ya zo da wani katon Jeep ya kwashe mu muka dau hanya,kukan zuci kawai nake dan ban taba tunanin magana zata yanke min ba gashi ko tafiya bana iya yi da tuni na bar gidan yanzu dai sai yadda aka yi dani, gidan da ya Gina katon gaske ne gidan bene duk mai hankali da tunani dole ya dasa ayar tambaya akan Abban Nusrah a cikin shekara guda yayi wanan kudin har ya iya tamfatsa irin wanan gidan,har da Nusrah muka tafi,nidai tunda muka Isa shi da Yaya Abu suka ririkeni Suka kaini wani katon daki fuskar Abban Nusrah d'auke da murmushi ya hau cemin nan ne dakina,daga haka ya sa Kai ya fice yarana ma ban ga

alamar suna wani farin ciki ba Ina Jin muryarsu daga waje da alamar zagaye gidan suke.

Ina Nan a kwance Nusrah ta shigo tana shigowa ta zauna a gefena tana "Umma Ina Abba ya samu irin wanan kudin yayi ginin gidanan wallahi umma na fara tsoro kwanaki kince mun zaki min magana akan Abban mu baki zo kinmin ba wallahi tunda ga ranar ban Kara samun kwanciyar hankali ba gashi yanzu bakya iya magana umma gidanan fa zaiyi miliyoyin kudi"

Inama Ina da halin da zan bude bakina da na mata magana tana k'ok'arin magana Abban Nusrah ya shigo Yana "Nusrah har kin gama ganin gidan"

Murmushin yake tayi tana "Eee Abba wallahi yayi kyau sosai yanzu nake bawa umma labarin haduwar gidan"

"Gobe zan riketa ta zagaya gidan itama naga alamar ta gaji,Allah ya baki lafiya Sajeeda"

"Allah ya tsine maka albarka Kabiru Allah ya tona maka asiri"

Na amsa Masa a zuciyata a daidai lokacin da Nusrah ta fice daga d'akin.

Shima ya juya ya fita.

Kwana biyu Nusrah tayi ta tafi.

Duk zuciyarta cike da damuwa.

Tunda muka dawo Abuja Abban Nusrah ya rage kula dani,sau daya yake lekoni idan ya lekoni bana Kara ganinsa a d'akin ma yanzu ni kadai nake kwana su Annur ke lekoni sai idan Yesmeen taga ba kowa sai ta shigo a gurguje ta kawomin ruwan Addu'a ta daga kaina na sha duk da bana magana tace min kwana take tana Addu'a ta tofa a cikin ruwa ta faki ido ta kawomin na Sha.

Yau ma Ina kwancen na jike Inda nake kwance hawaye kawai nake wacce na Kira da yayata ko sau daya yau bata lekoni ba,wajen Sha biyu sai ga Abban Nusrah yaci kwalliya cikin shadda Kamar wani ango kallon sa kawai nake sai da ya fesa turare a d'akin ya zauna a gefena Yana "Sannu Sajeeda ya jikin naki"?Allah ya sauwake ya baki lafiya

Ya riga yasan bani da bakin magana da Ido kawai nake bin shi,ya Kara cewa "Kinci abinci kuwa"?bari na Kira yaya Abu ta gyaraki sai ta kawo Miki abincin"

Daga haka ya mik'e ya fita waje na rufe idona Ina jin kirjina na bugu da karfi.

Kabiru

Yana fita yaci Karo da Yaya Abu da taci kwalliya Kamar zata je biki tana ganin sa ta hau washe baki tana "yanzu nake Shirin hawa sama na kiraka akan kazo ka karya"

"Ai ba ma najin yunwa Yaya Abu Dan Allah Yaya Abu Sajeeda ta bata wajen da take kwance ki taimaka ki gyara ta a bata abinci taci"

"Ee dama so nake idan na karya sai na Shiga wajenta dan idan ban karya ba wallahi bazan iya cin abinci ba idan na gyarata yanzu haka zaka yi ta jinyarta har sai ta warke"

Kabiru sosa kansa yayi Yana "Kin tabo min inda yake min kaikaiyi Yaya Abu kinsan bazai yu muyi ta zama haka ba Zan cutu da yawa dama Ina Shirin tararki da maganar Zan Kara Aure dan zamana a haka bazai yu ba"

"Zaka Kara Aure Kuma Kabiru"?

"Eee amma ke kawai na fara fadawa bana so na dagawa Sajeeda hankali sai an kwana biyu Zan fada Mata"

Yaya Abu ido ta hau kikiftawa har Kabiru ya tafi ya barta a tsaye.

Zuciyarta fal da tunani ta shige d'akin Sajeeda.

Rai a kuntace ta taimakawa Sajeeda ta gyara jikinta ta kai Mata abincin.

Tunda Kabiru ya fada mata zai Kara Aure bacci ya kaurace Mata ta rasa me ke mata Dadi a rayuwa.

Sai da ta kusa sati tana saka da warwara kafin ta yanke abinda za tayi,bazai tab'a yuwa ta bar Kabiru yayi wanan auren ba.

Yau da ta kasance laraba bayan ta gama abincin karyawa ta d'auko na Sajeeda ta Kai Mata dakinta tana bari taje ta dawo tazo ta bata abincin.

Tana fitowa ta hau sama dan ta duba Kabiru dan bata so yazo ya sameta a d'akin Sajeedan.

Tana Hawa sama Yesmeen dake lebbe tayi saurin Shiga d'akin Sajeeda jikinta na balain rawa.

Tana Shiga ta matsa kusa da Sajeeda tana "Umma karki Sha kunun nan ta zuba Miki Abu a ciki karki Sha umma"....

*ZAN KOYA MIKI YADDA ZAKI HADA TURAREN WUTA KYAUTA SBD KISAMU ABINDA ZAKI DOGARA DA KANKI KIYIMIN MAGANA TA WANNAN NUMBER 08144679009*

*HUMKAM INCENSE GIDAN KAMSHI DA GYARAN JIKI*

MATAR DA HAIHU MUNTANADAR WANI PACKAGE MAI TAKEN TUNA BAYA RANAR FARKO DARE DAYA MAI DUMBIN TARIHI

*MUNA GYARAN JIKIN AMARE SOSAI MUNA SAIDA TURARUKA DA MAGANIN MATA MASU KYAU DA INGANCI*

KANAWA KUZO HUMKAM TA *ZAN KOYA MIKI YADDA ZAKI HADA TURAREN WUTA KYAUTA SBD KISAMU ABINDA ZAKI DOGARA DA KANKI KIYIMIN MAGANA TA WANNAN NUMBER 08144679009*

*HUMKAM INCENSE GIDAN KAMSHI DA GYARAN JIKI*

MATAR DA HAIHU MUNTANADAR WANI PACKAGE MAI TAKEN TUNA BAYA RANAR FARKO DARE DAYA MAI DUMBIN TARIHI

*MUNA GYARAN JIKIN AMARE SOSAI MUNA SAIDA TURARUKA DA MAGANIN MATA MASU KYAU DA INGANCI*

*INA MATAR DA KE FAMA DA INFECTION MUN TABADAR MUKU MAGANI SADIDAN WANDA DA ZARAN KIN FARA AMFANI DASHI ZAKIJI YADDA ZAKI FITSARE WANNAN SANYIN INSHA ALLAH*

MUNADA TURARUKA MASU SIRRIKA NA MATAN AURE  KAMAR SU

*HATSABIBIYAR TURARE*
*NI DA MIJINA*
*SAI KABIYONI*
*SHU'UMAR HUMRA*
*BITA ZAIZAI*
*DARE DAYA WANKA GOMA*
Hmmm wadannan pls banda yan mata matan aure kadai zanbasu duk budurwar da ta siya ta shafa babu ruwana
08132506044

OTHER ROOM WANNAN TURARE MAI SUNA OTHER ROOM BA NORMAL TURARE BANE SIRRIKAN DA KE CIKINSA BAYANIN SAIDAI MU HADU TA PRIVATE

*INA BUDURWAR DA JARABAWA TA FAD'A MATA MUNTANADAR MINI WANI SET MAI SUNA BACK TO VIRGIN 08132506044*

*MAGANIN MATA MUNA SA KURMA KUWWA,SATA SHAKAF,GUMBA TSUMI ZUMA DA SAURAN SU HAJIYA INDAI MATSI KIKESO KISAI BACK TO VIRGIN*
*INA MATAR DA KE FAMA DA INFECTION MUN TABADAR MUKU MAGANI SADIDAN WANDA DA ZARAN KIN FARA AMFANI DASHI ZAKIJI YADDA ZAKI FITSARE WANNAN SANYIN INSHA ALLAH*

MUNADA TURARUKA MASU SIRRIKA NA MATAN AURE  KAMAR SU

*HATSABIBIYAR TURARE*
*NI DA MIJINA*
*SAI KA BIYONI*
*SHU'UMAR HUMRA*
*BITA ZAIZAI*
*DARE DAYA WANKA GOMA*
Hmmm wadannan pls banda yan mata matan aure kadai zanbasu duk budurwar da ta siya ta shafa babu ruwana
08132506044

OTHER ROOM WANNAN TURARE MAI SUNA OTHER ROOM BA NORMAL TURARE BANE SIRRIKAN DA KE CIKINSA BAYANIN SAIDAI MU HADU TA PRIVATE

*INA BUDURWAR DA JARABAWA TA FAD'A MATA MUNTANADAR MIKI WANI SET MAI SUNA BACK TO VIRGIN WANNAN SET DIN ZAKISHA MAMAKIN YADDA ZAI HADE JIKINKI GAMGAM.  08132506044*

*MAGANIN MATA MUNA DA KURMA KUWWA,SATA SHAKAF,GUMBA TSUMI ZUMA DA SAURAN SU HAJIYA INDAI MATSI KIKESO KISAI BACK TO VIRGIN*

*WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE 35-40*

"Karki Sha kinji umma wallahi ta zuba abu a ciki bari na tafi Kar tazo ta kamani naga ta hau sama wajen Abba"

Daga haka tayi waje da sauri.

Da ido na bita har ta fita sai na kasa gane Inda maganar ta ta dosa sai naji kwakwalwata ta kasa bani hadin kai nayi tunanin mai Yesmeen ke nufi da Kar na sha kunun da yayata da muke uwa daya uba daya ta kawo min,tana nufin abun cutarwa ta saka min kenan kirjina ya doka da k'arfi jikina ya dauki b'ari iya sanina ban yiwa Yaya Abu wani Abu da zata cutar dani akan me zata saka min Abu a kunu,maganar Yesmeen na karshe da na tuna yasa naji kaina ya sara min,wai ta hau sama wajen Abba,mai zata yi a sama wajen Abban Nusrah, shigowar ta dakin yasa na zuba mata ido Ina kallonta,sanye take cikin doguwar rigar atamfar ta cika rigar tam,har da dan kwalliya tana zuba kamshi,a haka ta hau sama wajen Abban Nusrah,sai na tafi tunanin yadda take zuba kwalliya tunda muka dawo Abuja,sai naji na kasa yarda shaidan ya raya min wai yayata so take taja hankalin mijina tunda yanzu a kwance nake bana iya komai,Koda ba a kwance nake ba taya zata tab'a tunanin Jan hankalin mijina bayan uwar mu daya uban mu daya ,a wane dalili zata zuba min abu a kunu iya sanina Kuma Yesmeen bazata tab'a mata sharri ba,kallon ta kawai nake inaso na hada tunanina waje daya

Ita kuwa room freshner ta d'auko a gaban mudubi ta fesa a d'akin ta zauna a gefen gadona ta hau mamatsa hanci tana "Sajeeda Allah ya yanke Miki wanan wahala da wanan rayuwar da kike na a kwantar a tayar wai ace jikinki ke fitar da wanan warin,Allah ya kawo Miki sauki na har abada wallahi da wanan wahalar da kike fama dashi,gwara ace ma mutuwa Kika yi Kika huta,kin zama hoto ba magana miji kuwa sai dai ki ganshi daga nesa,magani ba irin Wanda baa yi ba ba sauki,Allah ya yanke Miki wanan wahala kanwata wallahi Mai kaunarki bazai so ya ganki a haka ba, Allah yasa wanan jinya da Kika Sha ya zama silar shigarki aljanna sannu"

Kallonta kawai nake jikina na wani irin rawa maganganun ta sun matukar daga min hankali yayata ita ke min fatar mutuwa yayata ita takeso ta kau dani,mai nayiwa Yaya Abu da har take min fatan mutuwa,idan na mutu mai ribar ta,sai na tuna yadda take shishigewa Abban Nusrah idan ya shigo d'akin ta hau tambayar sa mai zaa dafa Masa,dama dan Abban Nusrah take wanan kwalliyar so take na mutu ta Aure shi kenan,?hawaye ya hau zubo min Ina Jin zafi a kirjina,wanan wane irin masifa da jarrabawa ne, mijina ya kassara min rayuwa yayata Kuma tana so ta karasa ni saboda kwadayin abun duniya, Mai na musu haka da zafi,

Kuka nake sosai kirjina na sama da kasa ita kuwa
Ta d'auko kunun tana "Sannu Sajeeda ya zaki yi da kaddara haka Allah ya rubuta miki"

Ta ajiye kunun ta matso kusa dani ta dagani daga kwancen da nake dan tsaf zata daukeni

saboda rashin nauyi bama nama a jikina ta saka min pillo daga wajen kaina,tana "Kunun gyada ne nasan kina so shi yasa na miki"

Kallon ta kawai nake yaushe rabon da Yaya Abu ta kawomin abun karyawa da wuri,wani zubin ma mantawa take sai dai Yesmeen idan ta faki idonta ta kawomin,ko ta tashi kawo min haka za ta yi ta yamutsa fuska tana nuna kyankyamina take,a yau sai gashi da wuri ta kawo abin karyawar saboda ta zuba min abu a ciki,a daidai lokacin da ta kawo cokalin kunun bakina,na kau da kaina hawaye na cigaba da zubomin na hau addua a zuciyata Ina "Ya Allah nasan mutuwa dole ce ya Allah ka ara min tsawon rayuwa ka bani lafiya ka gwada ikon ka akan Abban Nusrah ka bani lafiya yaga na warke,ya Raheem bana iya ibada saboda ba abinda nake iya yiwa kaina,Allah nayi tawasali da kyawawan sunayenka ka  bud'e min bakina na iya magana karka bawa yayata ikon cin galaba a kaina Allah nasan halin nan da na tsinci Kaina a ciki jarrabta ce daga wajenka Ina mai neman sasauci a wajen ka dan ban Isa na gujewa kaddara ta ba ka bani ikon cinye wanan jarrabawar ka bani tsawon rayuwa yayata ta gani a raye"

Yaya Abu juyo da fuskata tayi  tana "Ki Sha kunun Nan Sajeeda na fada Miki saboda ke nayi"

Turo k'ofar d'akin da akayi yasa muka kalli bakin k'ofar,Yaya Abu ta hau washe baki da taga Abban Nusrah ne ya shigo ya ci kwalliya da shadda ruwan zuma,shi ma bakin sa a washe ya karaso gefen gadon,na zuba Masa ido Ina kallonsa ya zauna a daya gefen Yana "Sannu da dawainiya Yaya Abu kina k'ok'ari sosai Allah dai ya biyaki ya saka Miki da alheri da bakya gidanan bansan ya zanyi ba"

Ba kunya ba tsoron Allah Yaya Abu ta kankantar da murya ta hau wani abu da ido tana "Ni Dan Allah ka daina cemin Yaya Abun nan ka kirani da Abu ko zainab ni idan kana Yaya Abu Nan sai naji kamar wacce ta tsufa bayan ni ba tsohuwa bace tunda haihuwa ta daya, matarka kuwa shekara daya kawai na bata"

Rufe Baki Abban Nusrah yayi Yana "Ai ko kwana daya kika bawa Sajeeda dole a baki girmanki na yayarta"

Kallon su biyun kawai nake Ina hararo Yaya Abu ta samu cikar burinta na kau dani, ta auri Abban Nusrah,dama Yaya Abu zata iya auren mijina,ashe ba abanza mahaifin mu ke mata fadan bakin Hali ba,dan lokacin da muke Yara indai na samu Abu ko nuratu haka zatayi ta fushi tana bakin ciki,akwai ranar da naci na biyu a islamiya mahaifinmu ya bani kyautar sabon littafi da fensir,daddare duk muna kwance ba bacci nake ba a kwance nake dan ba wuta da wuri Mu ke kwanciya Ina kwance da Nuratu a katifar dake kasa sai naga ta sauko daga kan gadon ta nufi wajen kayana har zan tashi zauna na fasa sai gashi ta bude akwatin karfen da kayana yake ciki,ta d'auko littafin ta yaga ta karya fensir din ta maida min akwati,har na girma na kasa manta abinda tamin da sai da na girma na gane bakin ciki yasa tamun haka, Haka idan muka samo kyautar abu ni da Nuratu sai ta yaga,ko auren Abban Nusrah da nayi murna take saboda tasan ba Mai kudi bane mijinta yafi shi hali, maganar Abban Nusrah ya katse min tunanin da na

tafi,Sajeeda ki sha kunun Mana"

"Tun dazu nake fama da ita ta Sha tak'i sha Kuma saboda ita na dama kunun nan"

"Ko dai zafine da kunun"?

Girgiza kai Yaya Abu ta hau yi tana "Ina fa kunun yaga zafi"

Sai ta Kai cokalin bakinta ta fito da harshenta ta dandana tana ba zafi"

Sai a lokacin ta tuna dandana kunun tayi ta Kuma hadiye,ta mike da azabar sauri ta fara sallati tana tari da k'arfi tana kakalo amai tayi waje da gudu,

Lumshe idona kawai nayi Ina yiwa Annabi sallati,da kanta ta dandana kunun da take so ta kasheni dash,sai Kuma na fashe da kuka dana tabbatar da kasheni dai Yaya Abu ke San yi Abban nusrah kuwa ya bita bakin kofa Yana mata sannu ya dawo wajen da ta zauna ya Kara d'aukar kunun Yana "Ina ga tsarkewa tayi tashi ki Sha kunun Sajeeda ko wani abun kikeso kici"?

Ido na zuba Masa Ina Addu'a Allah yasa shi ma ya  Sha kunun wallahi da zan ga abinda zai kashe Abban Nusrah Dadi zanji,kunun ya kawo bakina yaga na Kara kau da kaina sai ya ajiye kunun Yana "ko Tea Zaki sha,Wai bakya gajiya da kuka ne Sajeeda dan Allah ki bar kukan nan karki jawowa kanki wani matsala bari na hada miki shayi Ina ga kunun ne bakya so.

Ya mik'e yayi waje.

Kabiru.

Yana fita yayi hanyar kitchen Yana Shiga yaga Yaya Abu nata kakarin amai, gefen ta Kuma ga gwangwanin Madara ta bud'e ta lafta a kofi,

Shi kuwa cikin mamaki ya karasa wajen ta Yana "Yaya Abu lafiya kuwa mai ya kawo Miki amai Kuma"?

Yaya Abu kuwa hannu kawai take turawa bakinta tana kakarin amai,gudun Kar Kabiru ya zargeta yasa ta zuba ruwa a madarar ta kafa Kai ta shanye.

Sai da ta shanye ta kalli Kabiru dake ta jera Mata sannu tana "Wallahi bana San kazanta wari na shaka shine naji zuciyata na tashi"

"A cikin kunun warin yake"?

"Aaa Ina Kai kunun bakina na shako warin"

"Ai da kin fara gyarata kafin ki bata abincin naga yau ma ai warin da sauki Sannu bari na dama mata shayi Kamar kunun ne bata so"

Yaya Abu bata iya magana ba saboda cikin ta da taji Yana murda mata da ciwo,

Ta Kara dama wani madarar a daddafe tayi d'akin ta dan d'akin ta daban aka ware Mata,Yesmeen ma na da nata d'akin.

Tana shigewa daki ta daga Kai ta kwankwade madarar ta kwanta rub da ciki tana "da kaina nake neman kashe kaina banda rashin hankali da b'atar basira mai ya kaini dandana kunun duk wanan kabirun ne ma ya rudani naje na dandana

Ta Kara cije lebbenta saboda sosai taji cikinta na karta mata duk da sai da tayi amai,bata tab'a tunanin haka maganin ke da mugun karfi ba,ai wanan da Sajeedan ta sha da asirin ta ya tonu an gano ita ta saka mata magani a kunu,ya zama Dole ma ta Nemo Wanda bai Kai wanan k'arfi ba,ta dade tana Addu'a Sajeeda ta saukaka mata ta tafi da kanta batare da ta karasa ta ba,tunda ta gano irin arzikin da Kabiru yake dashi ta fara kwadaituwa da san itama ta dandana arzikin,ganin Kuma Sajeeda na fama da rashin lafiya yasa ta fara tunanin idan har Sajeeda ta mutu zata iya auren Kabirun ta mori arzikin sa sai ta fake da ta aure shi ne dan ta kula da yaran da wanan kudurin nata ta fara yiwa Sajeeda fatan mutuwa,har mamaki take yadda take ganin Sajeeda na raye dan ba karamin jin jiki sajeedan ke ba,daya hannun kuma ta ringa dan shishigewa kabirun tana caba ado,Sajeeda sam bata dace ma da arzikin Kabiru ba ita ta dace da arzikin, sai dai duk kwalliya da girkin da take yi bata ga alamar Kabiru na ganewa ba watakila dan Yana ganin Sajeeda shi yasa bazai tab'a kawo tunanin aurenta a zuciyarsa hakane yasa ta fara tunanin hanyar da zata bi ta karasa Sajeedan da kafar ta daya ke duniya daya a lahira,tana tsaka da tunanin abun yi Kabiru ya tareta da zancen zai Kara Aure,a ranar ko bacci bata yi ba idan har ta bari yayi auren hakan na nufin bazai tab'a aurenta ba idan kuwa tayi gaggawan kau da Sajeeda dole ma yayi tunanin auren ta,sai gashi Sajeeda bata Sha maganin ba ta Kare a dandana maganin da bata San Yana da mugun karfi ba,dan Mai gadin gidan tasa ya siyo mata maganin,dole ta Kara siyo wani,dan wanan yayi k'arfi da yawa tunda har a yanzu cikinta ciwo yake.

Tasan indai ta kau da Sajeeda ba mai kawo zargin ba mutuwar Allah da Annabi tayi ba,tunda dama ta dade tana fama,Kiran da ya shigo wayarta ne ya katse mata tunanin da take tana d'auko wayar ta ga Gwaggo ce ke kiranta,mai da wayar tayi ta ajiye dan yanzu Gwaggo ta fara matsa Mata da waya akan Sajeeda kusan kullum sai ta kirata ta tambayeta ya jikin Sajeeda.

Sajeeda

Abban Nusrah bai Dade da fita ba sai gashi ya dawo da kofin shayi a hannun sa har lokacin kuka nake,wa zai yarda wai uban yayana ne ya maidani haka saboda yayi kudi,wa zai yarda yayata da ta saki nono ta bani itace ke san ganin ta kasheni saboda kawai ta auri mijina

da take ganin yayi kudin da bata san ta hanyar da ya samu kudin ba, duk na jikina ke san cutar dani wane irin zamani ne wanan da Allah ya kawo mu,wai yayata ita take San ta kasheni,nata a yanzu sai naji yafi tsaya min a rai,na Abban Nusrah bai girgizani kamar yadda na Yaya Abu ya girgizani ba,dan dama shi namiji bashi da tabbas,ita Kuma Yaya Abu fa Yar uwata ce ta jini,da yanzu mutuwa tayi,auren Abban Nusrah zatayi ba tare da taji komai a zuciyarta ba,nasan shi ma Abban Nusrah tsaf zai aureta tunda da sauranta,waya sani ma ko ma suna soyayyar yanzu,bansani ba tunda nasan Abban Nusrah Yana cikin maza masu karfin shaawa.

Muryar Abban Nusrah ya katse min maganar zucin da nake Yana "ki bude bakin ki na Baki shayin Sajeeda Ina saurine zan fita ana jirana idan na dawo akwai maganar da zamu yi"

Kau da kaina nayi dan shi ma yanzu ba yarda nayi dashi ba, kila shi ma so yake ya kau dani kawai ya huta,zan ta zama a haka har sai idan Allah ya jefo min Yesmeen  dakina ta bani abinci naci.

Tsaki yaja daya ga na kau da kaina ya ajjye kofin shayin Yana "Kina da matsala Sajeeda yanzu abincin ne bazaki ci ba sai kin wahalar da mutane,idan bani ba ba kowane namiji ne zai iya jure irin wanan wahalar ba shekara guda Ina fama.

Kallon sa kawai nake hawaye na gudu a fuskata Yana k'ok'arin mik'ewa wayar dake gaban Aljihunsa ya fara ringing sai ya koma ya zauna Yana "Gwaggo ce nasan Kira tayi ta duba jikinki"

Wani Irin sanyi naji a zuciyata ko da makiyana ne a zagaye dani, Ina da wacce nake zuciyarta ta damu da halin da nake ciki,

Muryarta da naji ya ratso wayar da ya saka a handsfree yasa na baza kunnena Ina Jin muryar mahaifiyata.

Bayan sun gaisa Gwaggo tace "Kabiru har yanzu bata iya magana ne"?

"Wallahi bata iya magana har yanzu"

"Kabiru ko gida zaka kawo ta na nema mata maganin gargajiya  anan wallahi Ina cikin damuwa ko baccin kirki bana iya yi, kullum da tunanin Sajeeda nake kwana a raina yarinya Mai biyayya da tausayin iyaye duk yarana ba mai biyayyarta dan Allah ka dawo da ita gida,kila a dace da Sama Mata magani anan,Ina Nan ne kawai amma zuciyata na can wajen ku banaso kaga ko Ina damun ka a waya kullum,Abu ma yanzu sai da na kirata bata dauka ba"

"Gwaggo ki kwantar da hankalinki wallahi nan din ma Ina nema mata magani Kuma Yaya Abu na kula da ita sosai,bazan iya kawota na dora muku wahala ba,yanzu ma akwai wani likita da aka hadani dashi ance idan muka je wajen sa zamu dace"

"Abinda nake so ka gane so nake a. Gwada mata maganin gargajiya kila zaa dace tunda ana ta gwada na asibitin yak'i yi"

Ido na gwallo na fara gurnani Ina girgiza kaina da naga Abban Nusrah ya dage bazan je ba kuka kawai nake dan burina na koma gida,nasan idan aka dage da Addu'a zan iya warkewa ko ban warke ba na samu bakina ya bud'e na fallasa sirrin Abban Nusrah da na Yaya Abu,zamana a gidanan yanzu hatsarine tunda Yaya Abu so take taga ta kasheni.

Duk gurnani da girgiza kan da nake Kabiru haka ya bawa mahaifiyata hakuri akan bazai yarda ya maidani gida ba tayi ta min Addu'a har suka yi sallama ya kashe wayar.

Ya mik'e Yana "ba yadda zan maidaki gida a haka kina kallon komai yi Miki ake Gwaggo ta tsufa bai Kamata na dora musu nauyi ba zan fita idan na dawo akwai maganar da nake so mu yi"

Daga haka yasa kai  ya fice daga d'akin.

Haka na kwanta Ina sharbar kuka bani da Mai taimaka min yanzu sai Allah shi kadai nake dashi ya Kuma san halin da nake ciki.

Awa biyu a tsakani sai ga Yesmeen ta shigo d'akin da sauri ta rufe k'ofar da mukuli tana "Umma dafatan baki Sha kunun ba umma wallahi mama so take ta kasheki kinsan ta d'auka bana gani,da naje kitchen da lalube dan na Sha ruwa sai naga tana zuba magani a kunun bansan Mai yasa take so ta kashe ki ba Umma ko dai guduwa zamu yi Ina tsoron mama ta cutar dake bansan Mai Kika Mata ba"

Ta karashe tana share hawaye

Ta gyara min zama ta kafamin ruwan da ta shigo dashi a bakina na shanye Ina Jin sanyi a zuciyata wallahi indai zata bani ruwan na Sha sai naji nutsuwa Yesmeen Allah ya mata wani irin baiwa da ko ni da nake babba bana Jin Ina da Zurfin iliminta.

Da sauri ta sauko dani daga gadon ta cire zanin gadon ta  shimfida wani,ta kaini bandaki ta gyarani,ta dawo dani, duk abinda take cikin sauri take yi tana gamawa ta fita ba jima ta dawo ta hau ban shayi tana fadamin ta leka Yaya Abu taga kamar bacci take sai da ta tabbatar da na koshi ta maida kofin ta dawo ta rike hannuna tana "Umma mama da Abba bazasu tab'a cin galaba akan ki ba zan fara k'ok'arin nema Mana hanyar da zamu gudu,kafin lokacin umma tunda bakya iya sallah,bakya iya magana kar bakinki ya yanke da istigifari ki ringa yiwa Annabi sallati kiringa karanta hasbunallahu wa neemal wakeel ki rik'e Abu ukun Nan,umma Allah zai kawo miki sauki in sha Allah bari na tafi anjima zan dawo akwai abinda kike bukata"?

Kai na girgiza mata Ina Jin kaunar ta a Raina,yarinya Yar karama da hankali,ban taba tunanin

rashin magana da bana yi na ringa sallati a zuciyata Ina istigifari ba dan bani da aikin daya wuce kuka da tunani amma a yanzu tunda ta tunasar dani Zan ringayi.

Koda ta fita sallatin kawai na ringayi Ina istigifari har bacci yayi awon gaba dani.

Na hau mafarki na warke na fara magana shigowar Yaya Abu d'akin a mafarkin yasa na saki ihu a mafarkin dan da wuka ta shigo zata caka min.

A firgice na tashi daga mafarkin da nayi Ina bud'e idona naga Yaya Abu ta turo k'ofar d'akin da plate din abinci a hannun ta tana "Au bacci kike toh tashi kici taliya da Mai da yaji tunda dazu baki Sha kunu ba.......

*ZAN KOYA MIKI YADDA ZAKI HADA TURAREN WUTA KYAUTA SBD KISAMU ABINDA ZAKI DOGARA DA KANKI KIYIMIN MAGANA TA WANNAN NUMBER 08144679009*

*HUMKAM INCENSE GIDAN KAMSHI DA GYARAN JIKI*

MATAR DA HAIHU MUNTANADAR WANI PACKAGE MAI TAKEN TUNA BAYA RANAR FARKO DARE DAYA MAI DUMBIN TARIHI

*MUNA GYARAN JIKIN AMARE SOSAI MUNA SAIDA TURARUKA DA MAGANIN MATA MASU KYAU DA INGANCI*

KANAWA KUZO HUMKAM TA *ZAN KOYA MIKI YADDA ZAKI HADA TURAREN WUTA KYAUTA SBD KISAMU ABINDA ZAKI DOGARA DA KANKI KIYIMIN MAGANA TA WANNAN NUMBER 08144679009*

*HUMKAM INCENSE GIDAN KAMSHI DA GYARAN JIKI*

MATAR DA HAIHU MUNTANADAR WANI PACKAGE MAI TAKEN TUNA BAYA RANAR FARKO DARE DAYA MAI DUMBIN TARIHI

*MUNA GYARAN JIKIN AMARE SOSAI MUNA SAIDA TURARUKA DA MAGANIN MATA MASU KYAU DA INGANCI*

*INA MATAR DA KE FAMA DA INFECTION MUN TABADAR MUKU MAGANI SADIDAN WANDA DA ZARAN KIN FARA AMFANI DASHI ZAKIJI YADDA ZAKI FITSARE WANNAN SANYIN INSHA ALLAH*

MUNADA TURARUKA MASU SIRRIKA NA MATAN AURE  KAMAR SU

*HATSABIBIYAR TURARE*
*NI DA MIJINA*
*SAI KABIYONI*
*SHU'UMAR HUMRA*
*BITA ZAIZAI*
*DARE DAYA WANKA GOMA*
Hmmm wadannan pls banda yan mata matan aure kadai zanbasu duk budurwar da ta siya ta shafa babu ruwana
08132506044

OTHER ROOM WANNAN TURARE MAI SUNA OTHER ROOM BA NORMAL TURARE BANE SIRRIKAN DA KE CIKINSA BAYANIN SAIDAI MU HADU TA PRIVATE

*INA BUDURWAR DA JARABAWA TA FAD'A MATA MUNTANADAR MINI WANI SET MAI SUNA BACK TO VIRGIN 08132506044*

*MAGANIN MATA MUNA SA KURMA KUWWA,SATA SHAKAF,GUMBA TSUMI ZUMA DA SAURAN SU HAJIYA INDAI MATSI KIKESO KISAI BACK TO VIRGIN*
*INA MATAR DA KE FAMA DA INFECTION MUN TABADAR MUKU MAGANI SADIDAN WANDA DA ZARAN KIN FARA AMFANI DASHI ZAKIJI YADDA ZAKI FITSARE WANNAN SANYIN INSHA ALLAH*

MUNADA TURARUKA MASU SIRRIKA NA MATAN AURE  KAMAR SU

*HATSABIBIYAR TURARE*
*NI DA MIJINA*
*SAI KA BIYONI*
*SHU'UMAR HUMRA*
*BITA ZAIZAI*
*DARE DAYA WANKA GOMA*
Hmmm wadannan pls banda yan mata matan aure kadai zanbasu duk budurwar da ta siya ta shafa babu ruwana
08132506044

OTHER ROOM WANNAN TURARE MAI SUNA OTHER ROOM BA NORMAL TURARE BANE SIRRIKAN DA KE CIKINSA BAYANIN SAIDAI MU HADU TA PRIVATE

*INA BUDURWAR DA JARABAWA TA FAD'A MATA MUNTANADAR MIKI WANI SET MAI SUNA BACK TO VIRGIN WANNAN SET DIN ZAKISHA MAMAKIN YADDA ZAI HADE JIKINKI GAMGAM.  08132506044*

*MAGANIN MATA MUNA DA KURMA KUWWA,SATA SHAKAF,GUMBA TSUMI ZUMA DA

SAURAN SU HAJIYA INDAI MATSI KIKESO KISAI BACK TO VIRGIN*

"Taya Zan Sha wahala bayan Ina taka tsantsan da komai,wanan kame kamen da kake fa kana auren yarinya da zata maka biyayya fa an wuce wajen,baka da fargabar komai sai dan aikin da bazaa rasa ba"

"Toh idan na aureta bata bani hadin kai ba fa ta zama mai taurin kai irin na Sajeeda"?

"Sajeeda a mutanen da tazo ai,na yanzu suna da San kudi ga Ateeka nan Ina ta moreta Ina cikata da kudi,Kuma ko damuwa batayi ba Dan tana samun abinda take so,Kamar yadda nima nake samun abinda nake so,auren nan kawai zaka yi,ka samu ka ringa cika duk aikin da aka baka,itama nasan ka kasa nemanta ne Saboda halin da take ciki,Ina ta baka shawara ka kaita a cika aikin nan kak'i

Ido Kabiru ya zaro Yana "Bazan iya ba Rabiu iya wanan da nayi ya Isa ba sai na karasa ta ba har ga Allah baa san raina nayi harkar nan da ita ba taurin kanta ya jawo Mata"

"Toh ai gani nake idan baka karasa  ta ba bazaka saki jiki ka mori kudinka ba duk tsawon lokacin nan Wai ka kasa Kara Aure wai Kar aga ka mata wulakanci,da nine da tuni nayi biyu ma,nasan banda an rufe mata baki da tana magana zaka iya zuwa kace min zaka fita a kungiya dan naga kamar tsoron ta kake"

"Bazaka Gane ba Rabiu Sajeeda tamun hallaci a rayuwa ta kaunaceni shi yasa nake jin ban kyauta mata ba amma zan tura gidansu Barakan sati biyu kawai  zaa saka dan ko ba'a Sakani aiki ba yanzu ji nake idan banyi ta bayan nan ba Zan iya zaucewa na siye Iyayenta da kudi sosai,har sun kori saurayinta,duk da naga alamar ba Sona take ba Iyayenta ke tilasta Mata Ina sakar musu  kudi nasan an wuce wajen.

"Kudi ai sunyi  a rayuwa  abokina kayi abinda ranka ke so ko jarirya ka nuna kana  indai kana da kudi,da gudu zaa baka,yanzu abinda za'ayi  sai ka nemi wata a titi kayi aikin kafin kayi auren"

Hira suka Kara tab'awa kad'an kafin suyi sallama Kabiru ya kwanta Yana tunanin yadda zai barje baraka idan har ya aureta,dan yarinya ce mai tarbiya dan ko gwada rike hannun ta bai tab'a ba dan babu ma fuska hakan ya Kara kwadaita masa da san ya aureta ya ringa yiwa Iyayenta ruwan kudi,da yake mabukata ne da hannu biyu Suka rike shi, mahaifin Barakan ma idan zai gaishe shi sai ya rusuna,ba Kuma komai ya jawo haka ba saboda Yana da kudine.

Sajeeda

Ba abinda na saka a gaba yanzu sama da Addu'a dan tunda bakina ya daina yankewa da addua nake Jin dadin jikina,babbar matsalata yanzu Yaya Abu ce da naga ta karfin tuwo take so ta kasheni,yanzu bata tilasta min naci abinci bama ta kawomin,dan sai dai naji muryarta daga Palo,sai dai idan Yesmeen ta faki idonta ta kawo min naci.

Bansani ba ko canza salo tayi ni dai addua kawai nake Allah ya kareni daga sharrrinta.

Ina nan a kwance wajen sha biyu na Rana sai ga Abban Nusrah ya shigo yana washe baki,hannunsa rik'e da waya,yana "Ma Sha Allah na shigo d'akin sai dai kasan ba magana take ba,bani Nusrah"?

Muryar mijin Nusrah da naji yasa na baza kunnena Ina jin Mai suke cewa,barka barka da naji Abban Nusrah nayi Yasa na gane Nusrah haihuwa tayi,tuni hawaye ya hau zubo min na faranciki dan ban taba kawowa Ina rayye zata haihu ba,tana yawan Kira ta layin Abban Nusrah da sai ya shigo zai fada min ta Kira wani zubin idan ta matsa Masa sai ya kawo wayar ya saka a handsfree,haka zatayi ta magana ita kadai tana min kuka da Addu'ar samun sauki,Ina Umman take Abba dan Allah kasa tayi motsi naji ana yin suna Zan taho"?

"Ai kema kinsan ba iya motsin za tayi ba amma bari naga ko zatayi"

Ya matso da wayar bakina "hawaye na zubo min na fara gurnani dan ta jini,bani da bakin magana Amma Addu'a nake akan Allah ya bata lafiyar shayarwa,cikin rawar murya ta fara magana  tana "Umma Allah ya baki lafiya kina raina cikin nan ne dama ya hanani zuwa washegarin suna zanzo,in Sha Allah akwai wayanda na saka suke miki addua anan umma dan Kamar larurarki bata asibiti bace Unma Sunan ki zaa saka wa jaririya zaa ringa kiranta da ummi"

Rabon da nayi murmushi Ina ga tun kafin Abban Nusrah ya kashemin rayuwa,maganar Nusrah yasa na saki murmushi na fara gurnani,Abban Nusrah ya d'auke wayar daga wajen bakina yana "Yau kinsa Umman ki murmushi rabon da naga fuskarta haka har na manta"

"Allah Abba naji dadi, in Sha Allah umma zata samu lafiya kullum sai nayi mafarki ta warke"

"Zata warke ne ai Ina nan Ina nema mata magani,Gobe Zan saka mamanki ta taho ta zauna dake in yaso kwa dawo tare yanzu ki fadamin Abubuwan da kike bukata sai na turo Miki kudi ki siya,karki sake ki dorawa mijinki nauyin komai,a yanzu da nake dashi so nake na nuna Miki gatan da ban samu na yi miki ba a lokacin aurenki,Zan kashe abinda yayi daga Dubu dari zuwa miliyan daya in sha Allah"

"Abba miliyan daya fa kace"?

Murmushin ya saki Yana "Nusrah Abbanki yayi kudi,yanzu harkar Mai da nake na shigo min da kudi,Su Saifullahi ma zasu zo hutu wata mai kamawa Ina nan na siya musu mota iri daya"

Kallon Abban Nusrah kawai nake Ina mamakin yadda yake lissafa jin dadi da Haram,daga yadda Naga muryar Nusrah yayi kasa nasan itama mamakin arzikin nasa take,dan shi kadai ya cigaba da magana Yana zai tura mata Yaya Abu,zai Kira can Malumfashi yasa Yan uwansa suje Mata,Yana jira yanzu nan ta turo acct din ta zai saka Mata Dubu dari biyar ta Kuma turo na mijinta.

Nusrah kuwa sai cewa take ita bata bukatar komai ya bar shi,yadda take magana ma da alamar a rude take,sai da ya daka Mata tsawa akan ta turo masa acct dinta yanzu Nan kafin ransa ya b'aci ya kashe wayar Yana k'ok'arin magana aka turo k'ofar d'akin,kafin ma ta karasa shigowa kamshin turarenta ya fara iso Mana,nasan ba kowa bace sai Yaya Abu.

Ta saka Riga da skirt gotai gotai da ita ya matse ta ko kunya bata ji sai uban tumbinta da ta matse kamar mai ciki,daidai da tafiyar ma cikin rangwada take ta canza murya Abban Nusrah da a yanzu na lura ya fara rainata yace "aa hajiya Abu wanan kwalliya haka ko dai kinyi sabon bazawari ne"?

Sai tayi wani farr da Ido a daidai lokacin ta karaso gefen gadon ta zauna tana "Wane irin bazawari ana zaune kalau kawai dai nayi kwalliya ne dan naji dadin jikina Dan a rayuwata bana San kazanta"

Dan ta karfin tuwo take so ma ya daina shigowa wajen Sajeedan ya ringa ganin kazantar ta ita Kuma kwalliya da take dauka ya ringa ganin tsaftar ta,Dadi kamar ya kasheta da taga Yana satar kallon ta

Tunda ta zauna na lura Abban Nusrah na Kare Mata kallo kasa kasa,dan ba lafiyayyen mijin da zai ga yadda ta bulbula turare ta matse bai ji ya harba ba,

Kallon su kawai nake Ina Jin dama Ina da bakin magana da yau Yaya Abu taji magana a bakina da Abban Nusrah na tona masa asiri,

Maganar Abban Nusrah ya katse min tunanin da nake Yana "Gobe idan Allah ya kaimu idan ba damuwa dan Allah zaki je wa Nusrah ki dan zauna da ita har ayi suna Kinga ya Kamata ace akwai babba a wajenta,duk da zan buga waya su harira suje Suma,sai kiyi min list din Abubuwan da ya Kamata a siya a Kai,dan so nake ki tafar Mata da gara"

Tuni Yaya Abu ta dan canja fuska dan ko kad'an ma bata so tayi nisa da  gidan,dan bata san ma abinda zai nesanta ta da katon gida da shi kansa kabirun

Cikin yak'e ta fara magana tana "Toh idan na tafi wa zai kula da ita Sajeedar kasan fa Yesmeen ba gani take ba"

"Karki damu zan ringa kula da ita har ki dawo zan dan fita kafin na dawo sai ki rubuta list din Abubuwan da zaa siya a Kai"

"Toh mai zai hana mu fita tare kawai ba sai a sisiyo Abubuwan da ake bukata ba"

"Kuma fa kin kawo shawara bari na shirya toh"

Duk da ido nake binsu, Abban Nusrah yayi waje,Yaya Abu ta bi shi a baya tana rangwada.

Ina Jin motsin su a Palo,har fitar su basu dade da fita ba sai ga Yesmeen ta shigo d'akin,ita ta bani abincin karyawa ta gyarani kamar yadda ta saba,sai da ta gama ta zauna a gefena tana "Umma Ina so mu gudu,bansan ya zanyi wajen daukarki ba tunda ba iya tafiya kike ba,so nake mama tana barin gidanan gobe idan shima Abba ya fita sai mu gudu,toh bansan yadda zanyi ba

Sam bamu ji motsin komai ba sai ji Muka Yi an turo k'ofar ni da ita muka waiga da sauri.......

ALBISHIRINKU 🥳🥳 ALBISHIRINKU 🥳🥳🥳🥳 MANYAN MATA
Takunce dai A&Z COLLECTION takara zuwa muku da kayanta masu sauki da inganganci👌👌

Muna da supplement nau,i kala kala

Sannan akwai sabulu Mai suna HALFCAST SOAP hmmm hajiyata duk yadda za,ai karki Bari abaki labarinshi Dan sabulune dayake aiki cikin kwana uku kacal 👌zakiga yadda kalarki zata koma kiyi haske me kyau bana bleeching ba haka Zaki dinga sheki kina haskawa acikin jama,a 🔥🔥🔥
Koda kindaina amfani dashi ba,abunda fuskarki zatai saboda  natural ne Wanda sukai bleeching yabata musu jiki dafuska Kuma kunemeshi Yana dawo dakalar fata baidaya bacan Baki nan fariba 😄
Akwai cream gamasu San suhada set Wai ai hajiyata saikin zama taurariya acikin taurari mudin kika mallakeshi💃💃💃
Kira ko WhatsApp 09037870422

Karku manta muna da supplement kala kala

Na matsi

Na gyaran breast
Na hips
Na slimming
Na fari
Na gashi
Dasauransu

Haka zalika muna :

HADIN MAI  JEGO
HADIN UWARGIDA
HADIN AMARYA

Kuma duka afarashi me rahusa kedai kawai kituntubeni 👇👇
09037870422

Muna garin kano muna tura Kaya ko,Ina cikin aminci 🤝

Sai Allah yakawoku

*WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE 55-60*

Wani irin ajiyar zuciya na saki a lokacin da naga Hamza ne,ya dawo daga makaranta Kuma lokacin tashin su bai yi ba, Yesmeen kawai yake kallo cikin tsananin mamaki,na maida kallona wajen Yesmeen data rude ta rasa yadda za tayi dan ya riga da ya ganta,duk da Hamza yarone sai naji dama ta fada masa halin da muke ciki,tunda Hamza nada zurfin tunani, kila shi ya iya sanin hanyar da zai bi mu gudu daga gidan,a daidai lokacin da ya karaso wajen mu Yana "Aunty Yesmeen dama kina gani"?

"Ina gani Hamza Dan Allah karka fadawa kowa Ina gani kanina zan fada maka dalilin da yasa nayi karyar makanta,mai ya dawo da Kai gida yanzu bayan lokacin tashin ku bai yi ba Ina Annur"?

"Aunty Yesmeen Mai yasa toh bakya so a San kina gani"

Gurnani na fara yi Ina kallon yesmeen so nake ta fadawa Hamza gaskiya ta fito ta fada Masa halin da muke ciki tunda da waya a hannun sa kila ya Kira min Gwaggo a waya ya fada mata ta kawo min agaji,amma Yesmeen ta k'i fada Masa ta hau magiyar ya rufa Mata asiri Kar ya nunawa kowa tana gani tayi alkawari zata fada Masa,Hamza da yace mantuwa yayi na Assignment din da aka hada mi shi na Yan ajinsu dan shine monitor school bus ya kawo shi dan ya d'auka  dan yau zasu yi presenting shi yasa ya dawo,daga haka ya fice daga d'akin.

Hawaye kawai nake Ina kallon yesmeen,Yesmeen tana ganin k'ok'ari take ta taimaka min Wanda ita bata san rashin fadawa kowa da tsoron da ta saka a ranta zai kai ga Yaya Abu ta samu cikar burinta akaina ko shi Abban Nusrah ya karasani,tunda ya fara tunanin nemana ta baya,haka ta tsaya min surutun idan Yaya abu tayi tafiya zata faki idon driver ta fita ta samo mota yazo ya d'auke mu.

Addu'oi da ta saba yimin tayi min ta tofa a ruwa sauran ta shafa min a jikina,haka ta zauna a d'akin har sai da taji motsin bud'e gate tayi sauri ta fice daga d'akin.

Kabiru

Koda Suka fita a gaban mota Yaya Abu ta kame,ta dora mayafin ta akan kafadarta bai kawo komai ba yaja motar suka dau hanya wani katon super market,sai k'ok'ari yake wajen  danne zuciyarsa daga kallon Yaya Abu da  yaga tana ta wani musketa musketa ga kamshin ta da ya cika motar,tuni zuciyarsa ta fara Masa sake saken da yake k'ok'arin yakicewa daga zuciyarsa da karfi, magana da tayi cikin murya kasa kasa yasa ya waiga Yana kallon ta "Yanzu idan na tafi gobe wa zai cigaba da maka girki"?

Murmushi ya saki yana "hajiya Abu kenan ai bani da matsalar abinci dan zan iya siyo mana muci,ko na yiwa baraka magana ta ringa dafa min har ku dawo,banda haihuwa nan da akayi ma da sati na sama Zan tura gidan su Barakan dan gaskiya zamana haka bazai tab'a yuwa ba"

"Wai har yanzu zancen auren naka na nan"?

Yaya Abu tace tana  jin bacin ran ambatar Barakan da yayi,wai duk kwalliya nan da take yi take Masa signa ya kasa ganewa,ko dan Yana ganin ita yayar Sajeeda ce shi yasa yaki ganewa

Gashi yau taga alamar ta burgeshi tunda Yana ta satar kallon ta, mik'a ta farayi tana hamma ta gantsaro kirjinta tana "Ni sai nake ganin kamar da ka dan jinkirta da zancen auren mu ga abinda Allah zaiyi"

Kabiru tuni yaji tana neman hargitsa shi,da mikar da tayi,tuna yayar Sajeeda ce ita yasa ya kau da Kansa daga kallon ta yana

"Tom idan ban auren ba haka Zan  zauna,ai a haka ma nayi k'ok'ari, ban ga alamar Sajeeda zata samu sauki kusa ba Auren kawai Zan yi saboda Kar na fada hallaka ko da  naje gida ai na fadawa su baba Zan yi auren duk sun saka min albarka itama Sajeedan duk da bata iya magana nasan ta amince da nayi auren saboda larurar ta,Baraka yarinya ce mai tarbiya in Sha Allah bazan samu matsala da ita ba zata rik'e su Annur da amana.

Yaya Abu  daina gane Mai yake cewa tayi dan hankalin ta yayi mumunan tashi,tana ji tana gani,duk burin da take ci da mafarkin da take da ta aure shi ta mallaki arziki Mai yawa zai tashi a banza,ba ranar banzan da bata yi mafarki ta zama matar gidan,tana abinda ranta ke so ba,idan har ta bari yayi auren nan,ba yadda za'ayi ya tab'a aurenta,Kuma kila karshen zamanta a gidan ya zo,dan zaa iya cewa ta dawo da Sajeeda gida taje ta cigaba da kula da ita,da a ce ta samu cikar burinta da yanzu anyi sadakar bakwai din Sajeeda,kila kafin tayi arbain ta samu Kan kabirun yace zai aureta, zama bai ganta ba tun kafin Kabiru ya Kai ga turawa gidansu yarinya da yake cewa zai aura
,har suka iso  super market din Kabiru yayi ta jidar kaya haka tayi ta zuba tunani,har sai da Kabirun ya tambayeta lafiyar ta kuwa tace masa ji tayi zazzabi na neman rufeta,ya Mata sannu Yana bari ya karasa siyayyan ya maidata gida.

Koda suka koma gida d'akin ta ta shige tana tunanin yadda zata yi.

Ya zama dole tayi Abu da gaggawa bata san wane irin taurin kai ne da Sajeeda ba,bata ga marabarta ma da mataciya ba tunda komai yi mata ake, arzikin nan itace ya Kamata ace ta samu,tunda Sajeedan tazo gangara gwara kawai ta rage mata wanan wahalar a kwantar a tayar din,tunda ta daina yarda taci abincin shaketa kawai zata yi har sai ta daina numfashi karyar ma rashin lafiya zata yi yadda bazata wani jewa Nusrah ba ko da Wasa bata San nisa da gidan.

Kabiru

Kuwa tana shigewa ya bita da kallo har ta shige, ya rasa tunanin da ya Kamata ma yayi akan Yaya Abun yadda take shishige Masa da Masa shagwaba har mamaki yake,ko jiya da safe haka ta hawo sama da sleeping dress,ko mantawa take ita yayar Sajeeda ce,yau da ace basu hada jini da Sajeeda ba ai da ya samu nama.

Kiran da Rabiu ya Masa ya tuna Masa aikin da ke gabansa, kwana biyu kacal ya rage Masa,sai yaji dama Yaya Abu ba yayar Sajeeda bace da ba abinda zai hana ya nemeta,Sajeeda kuma da zai nema asirin sa a rufe da sai yadda yayi da ita jikinsa Kuma yak'i bashi hadin kai, wanka ya sake Yi ya fice dan ya nemo wacce zata biya Masa bukatar sa

Yaya Abu kuwa karfe shidda na  yamma ta fito daga daki,ta dora girki,dan bata da burin daya

wuce yau dinan ta samu cikar burinta,idan har ta sake bawa Sajeeda abinci bata ci ba ba abinda zai hana ta danne Kan Sajeeda da pillo.

Tana gama girkin  ta zuba na Sajeeda ta saka maganin ta ajiye a gefe,ta fito daga kitchen din tayi wanka ta caba ado dan so take ta karfin tuwo ta jawo hankalin Kabiru kanta,sai da aka iddar da Sallah isha ta fito daga d'akin tasan Kabiru tunda ya sake fita bai dawo ba,gwara kawai yanzu tayi abinda za tayi kafin ya dawo din,tana Shiga kitchen ta hau  kwallawa  Hamza Kira da take jiyo maganar su a d'akin Sajeeda,dan so take su bar d'akin ta samu ta bawa Sajeeda abincin.

Hamza na zuwa ta bashi abincinsa tana su wuce suje suci abincin su.

Hamza na karba ya koma d'akin Sajeeda.

Ita Kuma Yaya Abu ta fito da abincin Yesmeen dan ta tsani taga ta fito daga dakinta tana bin bango,ba karamin Haushin Yesmeen take ji ba dan wani zubin sai taga kamar ma tana gani,a yau ne kawai ta gama girkin bata shigo kitchen neman wani Abu ba,amma indai tana girki sai ta shigo,a hankali ta turo k'ofar sai taga Yesmeen  ta saki littafin hannun ta da sauri ta mai da idonta sama,Yaya Abu ta saki baki tana kallon ta dan sai taga kamar karatu ta shigo taga tana yi"

Ba dai Yesmeen tana gani ta musu karyar bata gani ba,ta nufi wajen da Yesmeen din da kanta ke sama tana kalle kalle tana zuwa gabanta ta d'auki littafin taga littafin addu'oi ne daga dukkan alamu Yesmeen karya take yi musu tana gani idan bata gani taya zata dauki littafi tana karantawa,yesmen kuwa da jikinta ke rawa tana zuba Addu'a a zuciyarta Wayance wa tayi tana waye nan"?

"Nice nan ke da bakya gani ya akayi kike karatu"?

"Kafin na daina gani na Saba da karanta addu'oi mama shi yasa duk da bana gani,nakan d'auko na ringa shafa kowane shafi,sai naji kamar Ina gani"

Gyada Kai Yaya Abu tayi tana ba shakka toh ga abincin ki nan sai kici"

"Nagode mama"

Yaya Abu wani irin kallo ta zuba mata kafin tayi hanyar waje,ta bar k'ofar d'akin Yesmeen din a bud'e tana ayyana irin dukan da za tayiwa Yesmeen idan ta gano tana gani kitchen ta koma ta d'auko ragowar maganin da ta zubawa Sajeeda ta  fito ta koma d'akin Yesmeen cikin sand'a ta zubawa Yesmeen ido da idonta ke kallon sama har lokacin tana zaune a yadda ta barta abincin ta na nan a gabanta,sai shafa littafin addu'oi take tana miis mis da baki.

A hankali ta tsugunna a gaban Yesmeen ta barbada maganin a cikin abincin,tana cigaba da

kallon Yesmeen idan har Yesmeen tak'i cin abincin nan tasan tana gani idan kuwa taci tasan dagaske bata gani,dan ko kad'an bata yi motsin da Yesmeen zata san ta shigo ba ta koma gefe daya tana kallon yesmeen da har lokacin take ta shafa littafin,Yaya Abu kuwa tuni ta fara tunanin karya Yesmeen take  tana gani,tayi gyaran murya tana "Kici abincin ki Mana sai ya hucce"

Yesmeen duk abinda Yaya Abu take yi tana kallonta da ace Yaya Abu zata Mata kallon tsaf zata ga yadda jikinta ke balain rawa har tana hada gumi,da dukan alamu Yaya Abu so take ta kasheta itama dan tana kallon sama ne kawai amma tana kallon sadda ta zuba mata abu a cikin abinci,da kulle k'ofar d'akinta take Yi,Yaya Abu ya kafa Mata dokan ta daina kullewa dan ta tsani tazo ta ringa kwankwasawa, ta riga tasan Yaya Abu so take ta gano ko tana gani ko bata gani,a yanzu indai tak'i cin abincin nan zata gano tana gani,karshen ta idan Kabiru ya dawo aka fada Masa tana gani,a yau ya aikata lahira ba Mai iya kwaceta dan itama Yaya Abu ba karamin tsanarta tayi ba,da hankalin ta ba yadda zata ci abinda zai cutar da ita,a yau dai asirinta zai tonu dan bazata ci abincin ba, zata nunawa Yaya Abu tana gani,maganar Yaya Abu ya katse mata tunanin da take da tace taci abincin Mana Kar ya sallamce,duk Shirin da take yi na su gudu da Sajeeda idan har Yaya Abu ta tafi wajen Yesmeen gobe ya tashi a banza tsawan da ta daka Mata da "Kici abincn nan nace kuut a lailai yarinya nan ta dauka dunkulallen kai ne dani, har na shigo d'akin nan naganki da littafi kice min bakya gani,ci abincin nan nace"

Yesmeen so take ta saukar da kanta ta kalli Yaya Abu tace tana gani,ta fada Mata dalilin da yasa tayi karyar makanta,indai da zuciya a kirjinta ai dole ta tausayawa Sajeeda da ita kanta,sai dai a madadin ta saukar da kanta sai ta hau lalubar abincin ta d'auko cokalin ta debo abincin duk bisa umarnin zuciyarta dan Yaya Abu na gabanta a tsaye ta kame kugu da alama kiris take jira ta rufeta da duka,tana bude bakinta Yaya Abu ta tunkude hannunta ta d'auke abincin dan tasan indai tana gani tasan bazata tab'a yarda taci ba,tana ficewa Yesmeen ta kifa tayi sujada tana godewa Allah Dan Allah ne ya rufa Mata asiri ya kareta,yanzu ba iya Kabiru ne abin tsoro ba har Yaya Abun bata tab'a tunanin zata tunkuda hannun ta ba ta dauka zata barta taci abincin ba abinda zai zaunar da ita a gidanan da Sajeeda  Yaya Abu na tafiya gobe taga Kabiru ma ya fita zata Nemo Mai taimaka Mata su gudu,ta koma ta zauna tana Jin yadda kirjinta ke bugun uku uku,yau dai ta tsallake rijiya da baya.

Tana dagowa daga sujada ta koma ta zauna a daidai lokacin da Yaya Abu ta sake dawowa da wani plate din ta dire a gabanta tana "Ga wani abincin kici wancan da na d'auke abu ne ya fada a ciki.

Daga haka ta kullo rufo  dakin Yesmeen ta koma kitchen ta d'auko abincin Sajeeda,a yanzu ta tabbatar wa kanta da yesmen bata gani,ba yadda zaayi ta kashe Yesmeen,dan bata ga amfanin kau da ita ba za Kuma a gano idan suka tafi lokaci guda da Sajeeda dama gwaji take so tayi ta Kuma ga Yesmeen din ba gani take ba.

Sajeeda

Hawaye kawai ke zubo min da naga Hamza Wai shi ya kaini bandaki ya gyarani,ya canza zanin gadon da na b'ata ko kyankyamina banga yayi ba ballantana ya toshe hancinsa.

A fadar sa ma a d'akina zai kwana dan sunyi hutun makaranta,ina Jin lokacin da Yaya Abu ta kwalla masa Kira ya fita ba jimawa ya dawo da farantin abinci a hannun sa dama tare suke ci da Annur,shinkafa da taliya ne da miya,ya hau tsakiyar gadon ya juya abincin ya kalli Annur Yana yazo suci,haka Hamza ya ringa ci Yana bani a baki, Kamar yasan wani zubin da yunwa nake kwana dan Yaya Abu yanzu ba bani abincin take ba, Yesmeen Kuma ba ta iya zuwa ta bani dan Yaya Abu sai ta Kai Sha biyu a zaune a Palo tana kallo,a haka yayi ta bani har sai da na d'auke kaina ya bani ruwa na sha,yaje gaban mudubi ya kwaso magunguna na da ni nasan ba aikin da suke min amma ba bakin da zan hana a ringa bani,haka na Sha ya maida ledar gaban mudubi ya dawo ya zauna,Annur kuwa suna Gama cin abinci ya ringa buga game a tab din da Abban Nusrah ya siya musu,shi kadai ne banga Abban Nusrah ya siyawa waya ba,wayar Yesmeen ma da ya kwace Ina ganin dan Yasan tasan sirrinsa ne Amma sai cewa yayi wayar bata da amfani a wajenta tunda ba gani take ba,Hamza Kuma ya d'auko wayarsa ya ringa daddanawa,duk da ido nake bin su iya su da nake gani wallahi Dadi nake ji a raina,haka nake kwana ni daya Kamar mayya ba Mai kula dani,dama su barmin su su ringa kwana a d'akina nasan ko Yaya nayi gurnani Hamza zai tashi kila ya gane Ina bukatar wani abun ne,Yesmeen ma Yaya Abu ce ta koreta a ranar da ta shigo d'akin da dafa bango akan zata na kwana dani, Yaya Abu ta koreta akan me zata kwana ita da ba gani take ba ba Kuma wani abu za ta iya min ba.

Shigowar Yaya Abu ya katse min tunanin da nake na juya Ina kallonta,tana ganin su Annur ta hade rai tana "Uban me kuke nema a d'akin nan"?

"Ba komai dama munzo mu zauna da umma ne saboda ita kadai ce yau ma anan zamu kwana dan umma na bukatar kulawa tunda ba mai kulawa da ita daddare"

"Toh wanan ne baku Isa ba,bazaku kwana anan din ba,kaji min yaro da iyayi waye yace maka baa kulawa da ita maza maza tashi ku tafi dakinku zan bata abinci"

"Ai taci abincin tare muka ci abincin da ita dan Allah mama ki barmu mu kwana Yaya Saifullahi ma dazu da muka yi waya dashi cewa yayi mu ringa kwana da ita"

"Toh bazaka kwana ba nace so kake kace bana iya kula da ita har wani waya ake bugo ma ace ka kula da ita dalla tashi ku ficemin daga d'aki"

Annur da sauri ya dauki tab dinsa yayi waje,Hamza kuwa baa San ransa ba ya mik'e Yana kallona yayi waje.

Na hau zubar da hawaye kila ma kallon karshe Muka yiwa juna dan yau nasan Yaya Abu

shigowa tayi ta kasheni,dan rabon da Kuma ta kawo min abinci na manta tunda ta kawo abinci har tana koran yayana da suka ce Mata naci abinci ta dage akan su fita.

Ido na zubawa yayata da muke uwa daya uba daya tare muka taso duk da hallayenmu ba daya ba,amma har nayi aure ba karamin girmamata nake ba,ko da Wasa ban taba rainata ba,duk da nasan abubuwa da take min marasa kyau haka nake shanyewa amma yau itace ke san kasheni akan dukiya.

Tana ajiye abincin muka hada ido da ita,yadda nake kallonta yasa itama ta zuba min ido tana "Wanan kallon fa Sajeeda hakuri zakiyi haka Allah ya kaddara miki ke ba Mai nisan kwana bace karki wahalar dani ki bud'e bakinki na baki abinci kici"

Kau da kaina nayi da ta kawo abincin bakina,nasan bana iya motsi amma sai na gwada daga hannuna da ta sake kawo cokalin bakina sai na tunkude cokalin,na zubawa hannuna da na tunkuda cokalin da Ido Ina mamakin yadda aka yi har na iya daga hannuna dan hannun a shanye yake bana iya dagawa,itama da alama mamaki ne ya rufeta da ta ga abinda nayi,dan har mik'ewa tayi taja da baya ni kuwa na lumshe idona Ina yiwa Ar Raheem godiya Wai yau nice da motsa hannuna na yarda addua bata faduwa kasa a banza tunda har na iya motsa hannuna watarana zan iya bud'e baki nayi magana, kabara kawai nake a raina

Ita kuwa Yaya Abu da ta balain girgiza da ganin na motsa hannuna ta tako gefena ta daga hannuna tana "Daga hannun ki naga kinyi fa har Kika ture abincin da na baki?a lailai kice tafiya da magana ya rage Miki shikenan kin warke tab"

Ta ja da baya ta dauki abincinta tayi waje da sauri wato ba haka ta so ba Yaya Abu dai ta karfin tuwo take so taga ta kasheni,Raina dai a hannun Allah yake,tunda har na iya motsa hannuna a goben nan idan Hamza ya shigo Zan karbi wayarsa na Masa rubutu Addu'ar da nake Allah yasa Kar Yaya Abu ko Kabiru su cutar dani kafin gari ya waye.

Tuni na maida idona na rufe na ringa yiwa Annabi sallati Ina Jan istigifari,Ina Jin muryar Yaya Abu da Abban Nusrah a Palo,ya nuna Yana so ya shigo ya dubani,tace masa Kar ya tasheni bacci nake.

Kabiru

Hankalin sa a tashe ya dawo gida dan Mata biyu daya samu duk basu yarda ya nemesu ta baya ba,duk da lodin kudin da ya basu, haka suka dage idan har ba ta gaba zaiyi va bazasu iya ba,dayar ma arniya ce ya dauka zata yarda sai gashi ita mari ma ta waska Mai daya fara nemo bayanta da jikinsa ta sosoka mai zagi,ta saka kayanta ta fice.

Koda ya Kira Rabiu ya sanar Masa sai ce Masa yayi ai dole yayi aikin nan yau,idan ba haka ba zaa bashi Wanda yafi wanan,abinda zai yi ya koma wajen Sajeedan kawai idan bai yu ba ya nemi Yesmeen kawai tunda ba ta gani,inyaso ya toshe mata baki.

Da wanan shawarar ya dawo gida,yana dawowa yaga Yaya Abu ta hakimce a Palo taci kwalliya tuni yaji yayi wani irin harbawa ya fara Jin inama Yana da yadda zai yi ya nemeta ta baya,da yaji dadi.

Da faraa ta tarbe shi ta kawo Masa abincin sa ta ringa jansa da hira, shi kuwa sai cije lebbe yake dan ji yake kamar ya jawota,dan wajen zuba Masa abinci ma sai da ta goga Masa kirjinta,haka ya matse Yana Gama cin abinci ya haye sama,dan in ya cigaba da zama zai iya aikata abun kunya.

Allah Allah yake daya tayi ya fara zuwa d'akin Sajeedan,dan har wani magani ya siyo yadda ko jikinsa yaki mik'ewa indai ya sha sai ta mik'e ta k'arfi da yaji.

Yesmeen

Sha daya da rabi na dare ta fito daga dakinta cikin sand'a ta nufi d'akin Sajeeda a hankali ta tura k'ofar ta maida ta rufe.

Sajeeda dake kwance tayi saurin bud'e idonta ganin itace yasa ta saki ajiyar zuciya.

Yesmeen na zuwa tayi kasa da murya tana "Umma ko dai guduwa zamu yi yanzu tunda duk sunyi bacci mai gadi ma na leka shi naga yana bacci,mu gudu kawai umma yanzu ma mama so take ta kasheni"

Kai Sajeeda ta ringa girgiza Mata dan tasan ba yadda za'a su iya guduwa Mai gadi kawai na iya tona musu Asiri,sai ta daga hannunta Yesmeen tabi hannun da kallo tana gwallo idonta waje cikin Farin ciki,ta wawuro hannunta tana "Umma Kinga hannunki na motsi Zaki iya dagawa alhamdulillah umma yanzu magana ya rage miki alhamdulillah umma adduar da muke yi ne"

Yesmeen tuni ta manta da abinda ya kawota d'akin saboda murna ta d'auko kofi a gaban mudubi na tana bari ta Kara tofa min Addu'a a ruwa ta shafamin.

Ta zauna daga kasan gadona ta hau tofi,ni kuwa sai murmushi nake dan bakinta yak'i rufuwa saboda murnar da take da na motsa hannuna.

Motsin da muka jiyo daga waje yasa ni da ita muka waro ido, sai muka ji kamar kofata ake San bud'ewa.

Yesmeen hankalinta a tashe ta ajiye kofin ta fara tunanin wajen b'uya,da yake siririya ce ita zuruf ta shige karkashin gadona a daidai lokacin da aka turo k'ofar d'akin nawa a hankali kirjina

kamar ya fado a lokacin da naga Yaya Abu ce ta shigo ta maida k'ofar ta rufe a hankali ido na zuba Mata Ina kallonta kirjina sai sama da kasa yake saboda fargaba nasan ba alheri ne ya kawota d'akina ba.

A gaban gadon ta tsaya tana "Wai idonki biyu Sajeeda kiyi hakuri ki yafemin na gaji da ganin ki haka a kwance tafiyar ki shi yafi Miki alheri

Kuka kawai nake dan na gano so take ta kasheni na daga hannuna Ina nunata sai motsa bakina nake ita kuwa ta zagayo ta gefen gadon ta d'auki pillon da na dora kaina.

Ta kawo pillon ta dora a fuskata

Ihu ta saka sakamakon cafkar da Yesmeen ta kaiwa kafarta.

A daidai lokacin da Kabiru ya turo k'ofar d'akin daga shi sai gajaren wando....

ALBISHIRINKU 🥳🥳 ALBISHIRINKU 🥳🥳🥳🥳 MANYAN MATA
Takunce dai A&Z COLLECTION takara zuwa muku da kayanta masu sauki da inganganci👌👌

Muna da supplement nau,i kala kala

Sannan akwai sabulu Mai suna HALFCAST SOAP hmmm hajiyata duk yadda za,ai karki Bari abaki labarinshi Dan sabulune dayake aiki cikin kwana uku kacal 👌zakiga yadda kalarki zata koma kiyi haske me kyau bana bleeching ba haka Zaki dinga sheki kina haskawa acikin jama,a 🔥🔥🔥
Koda kindaina amfani dashi ba,abunda fuskarki zatai saboda natural ne Wanda sukai bleeching yabata musu jiki dafuska Kuma kunemeshi Yana dawo dakalar fata baidaya bacan Baki nan fariba 😄
Akwai cream gamasu San suhada set Wai ai hajiyata saikin zama taurariya acikin taurari mudin kika mallakeshi💃💃💃
Kira ko WhatsApp 09037870422

Karku manta muna da supplement kala kala

Na matsi
Na gyaran breast
Na hips
Na slimming
Na fari
Na gashi
Dasauransu

Haka zalika muna :

HADIN MAI  JEGO
HADIN UWARGIDA
HADIN AMARYA

Kuma duka afarashi me rahusa kedai kawai kituntubeni 👇👇
09037870422

Muna garin kano muna tura Kaya ko,Ina cikin aminci 🤝

Sai Allah yakawoku

*WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE 60-65*

Kabiru turus yayi Yana kallon Yaya Abu da jikinta ke balain rawa hannun ta na Kan pillow Yesmeen dake kasan gado kuwa ta janye hannun ta da sauri kirjinta sai bugun uku uku yake tana Addu'ar Allah yasa Kar Yaya Abu ta lekota ledar dake kasan gadon da ledar katifa ce ta shige ciki ta kudundune.

Yaya Abu kuwa wani irin tsorone ya rufeta ta ma kasa cire hannunta daga Kan pillon da take so ta danna akan Sajeeda, tsoron ganin Kabiru da cafkar da taji anyi wa  kafarta  ta kasan gado ya matukar razanata.

Kabiru kuwa kasa hada tunanin sa yayi gu daya Yana tunanin mai ya kawo Yaya Abu d'akin Sajeeda a daidai wanan lokacin da yake a matukar bukace kamar ya haukace dan maganin karfin maza ya kwankwade gabadaya saboda Kar ma jikinsa ya kwanta dan ta karfin tuwo yau

yake so ya samu biyan bukatar sa jikinsa har wani rawa yake saboda ya matsu ya samu biyan bukatarsa jikinsa a tsaye kyam

Hannun Yaya Abu da ya gani akan pillon dake fuskar Sajeeda da har lokacin bata iya d'auke hannunta ba yabi da kallo.

Sajeeda kuwa ta fara sheshekar kuka dan ta gane wani ne ya shigo d'akin shi yasa Yaya Abu bata danne pillon ba hannunta dake rawa ta Kai ta cire pillon daga fuskarta,sai a lokacin Yaya Abu ta iya motsawa ta janye hannunta da sauri

Kabiru da ya gama hada tunanin sa waje daya cikin tsananin mamaki ya dago hannunsa Yana nuna Yaya Abu da "Kasheta kike so kiyi"?

Girgiza kai Yaya Abu ta fara yi cikin tashin hankali ta fara  magana cikin inina ta ja da baya dan ji take kamar zaa Kara cafo kafarta tana  "Naaa shigo ne dan na dubata Kabiru taya Zan kasheta"

"Abu pillo fa Kika dora mata akan fuskarta kina k'ok'arin dannewa na shigo innalillahi wa Inna ilaihi rajiun Abu kashe Sajeeda kike so kiyi"?

"Yaya Abu da jikinta ke balain rawa grigiza kanta ta fara yi da sauri sai a lokacin ta gane ma a tsirara kabirun ya shigo ga  gajeren wandon sa a kumbure.

Gwallo ido tayi tana Kara Kare masa kallo a daidai lokacin da ya fara takowa cikin d'akin jikinsa na balain rawa da tsananin mamakin abinda yaga Yaya abu na Shirin yi dan sai yaji ma sha'awarsa na sacewa Saboda tashin hankali abinda ya shigo yaga Yaya abu nasan yi,"Abu kashe Sajeeda kike so kiyi "?

Yaya abu cikin dakiya da borin kunya ta fara magana tana danne tsoron da take ciki

"Kaine dai ka shigo kake san kasheta Kabiru taya Zan kashe kanwata,Kai mai ya kawo ka d'akin ta a haka yanzu a halin da Sajeeda take ciki har zaka iya nemanta? innalillahi wa Inna ilaihi rajiun yanzu so kake ka karasata saboda ka samu kayi Aure,ai ba sai ka kasheta ba Kabiru zaka iya sakinta mu tattara mu bar maka gidan,har ace a halin da Sajeeda take ciki na a kwantar a tayar zaka iya nemanta toh ta Ina ma zaka nemeta a halin nan da take ciki idan ba kasheta kake so kayi ba"

Kabiru da ransa ya fara b'aci ya daka Mata wani irin tsawan wargaza masa shiri da take Shirin yi gashi duk alamomin rashin gaskiya ya bayyana a fuskarta shi ba yaro bane da zata raina Masa hankali danne pillon take so tayi a fuskar Sajeeda ya shigo

"Laifine dan nazo wajen matata ko da nemanta nayi haramune karki wani wayance Abu dan da

zuciya daya muke zaune dake a gidanan ban taba kawowa zaki iya aikata haka ba,Kiri Kiri naga kina san danne kanta da pillo har mai kanwarki ta miki haka da kike so ki kasheta ?dama haka kike?yanzu da ban shigo ba kasheta zakiyi kenan Mai ta Miki"?

"Ni zaka yiwa sharri Wai taya Zan kashe Sajeeda gurnanin ta na jiyo Ina daga daki shine na shigo dan na dubata,ganin bata dora kanta a pillow ba yasa na daga kanta dan na dora Mata pillon sai naji an ja kafata ta kasan gado hakane yasa na saki pillon a kan fuskarta dan zaka ji ma nayi ihu lokacin da ka shigo wallahi ba kasheta na shigo nayi ba  karka manta fa kanwata ce uwar mu daya uban mu daya akan me Zan kasheta"?

Sajeeda

Wani  irin kuka ne ya  kwace min da naga Abban Nusrah yayi shiru alamar karyar da ta tsara Masa yayi tasiri a zuciyarsa na fara girgiza kaina Ina nuna ta da hannu Ina "Mai na miki Yaya Abu da kike San kasheni?Mai na Miki da na cancanci haka daga wajenki?iya sanina ban taba miki komai ba,yanzu akan duniya kika zabi ki kasheni?mai na Miki kike so kiga kin rabani da numfashina"?

Duk cikin gurnani nake magana Ina nuna ta da hannuna da naga kabiru ya zubawa ido cikin mamaki Yana kallo da alama bai tab'a tunanin zan iya motsa hannuna ba kirjina ciwo kawai yake min Ina kallon makiyana guda biyu Abban Nusrah shi ma shigowa yayi dan ya nemeni ta baya dan a tub'e yake daga shi sai gajeran wando,mijina uban yayana shi ya jefani a halin nan haka bai ishe sa ba sai ya Kara nemana ta baya,ya karasani daya gefen Kuma yayata da muke uwa daya uba daya da ita,ita takeso ta kasheni wai dan ta aure shi,akan ta gan shi da kudin da bata San da ya ya same shi ba kuka kawai nake Ina cigaba da nuna Yaya Abu da hannu

Yaya Abu da  hankalin ta ya Kara tashi da yadda taga Sajeeda na gurnani tana nunata da hannu ta matsa kusa da ita da sauri dan gani take tunda ta iya motsa hannunta kila ma bakinta ya budu tayi magana ta tona mata asiri

Ta ruko hannun Sajeeda tana "Ya Isa haka Sajeeda dole kiyi kuka saboda Kinga mijin ki na neman yimin sharri daga nazo  na taimaka miki,amma ba komai tunda kora da hali yake min goben nan zan tattara na bar gidan kafin wani Abu ya Sameki ace nice ni nasan  wani ne ya shigo dan ya cutar dake  tunda  na ji an rik'e min kafa ta kasan gadonki"

Fusge hannuna nayi daga rukon da tayi min Ina cigaba da gurnani, Abban Nusrah ya matso kusa da gadon ya ruko hannuna yana "Sajeeda Alhamdulillah kin fara iya motsa hannunki alamar kin fara samun sauki da kina da baki da kin fada min gaskiyar abinda Abu ta shigo yi miki dan daga yadda kike gurnani ni nasan bata da gaskiya bansan mai kika Mata take so ta kasheki ba"

"Wai ya zaka ce Ina so na kashe Sajeeda ne?akan me zan kasheta,ka fito kace ka gaji da zamana a gidanka ba sai ka hada damin sharri ba dan wani ne ya shigo yake san cutar da ita

ka Kuma leka kasan gadon kagani dan wallahi an ja kafata bari na leka kagani"

Kabiru kallonta kawai yake a lokacin da ta fara k'ok'arin tsugunnawa dan ta leka kasan gadon.

Yesmeen hankalinta idan yayi Dubu sai da ya tashi da taji abinda Yaya Abu tace d'auke numfashinta tayi ta cire hannunta dake cikin ledar da ta nannade jikinta dashi a hankali,ta mik'a hannun Yaya Abu na lekawa ta kwasheta da mari, Yaya Abu ta saki ihu tayi waje da balain gudu.

Kabiru kuwa ya mik'e tsaye da sauri ya ja da baya Yana kallon kasan gadon dan yaji karar saukar Marin.

Tabbas da mutum a kasan gadon dan kamar motsi ma yake ji a kasan gadon.

Har lokacin ihu Abu ke tsallawa tana Aljanine a kasan gadon

Kabiru kuwa da shi ma jikinsa ya fara rawa ya fara neman abunda zai haska kasan gadon da kuma sandar da zai bugawa koma waye ganin bai ga komai a d'akin ba yasa yayi kasa da murya Yana "Sajeeda da gaskiya Abu akwai mutum a kasan gadon nan bari na dauko wayata na haska na d'auko sanda ta watakila barawone Ina zuwa"?

Yayi hanyar waje da sauri,Yesmeen kuwa ta fito daga kasan gadon da ledar a nannade a jikinta ta shige zif din Sajeeda cikin zafin nama tana hada wani irin gumi,k'yarma kawai take saboda tsoro.

Kabiru na fita ya ci Karo da yaya Abu da ta dafe kumatunta tana cigaba da ihun "ka leka kagani Kabiru wallahi akwai mutum ko aljan a kasan gadon,motsin da najiyo daga d'akina yasa ni fitowa dan na dubata wallahi ka leka kagani"

"Shhhh to ki bar ihu mana haka Ina zuwa"

Ya haye sama da sauri ba jimawa ya sauko da wayarsa da ya Kunna tocilan daya hannun sa rik'e da sandar labule yayi d'akin Sajeedan a hankali Yaya Abu da jinta bai dawo sosai ba tabi bayansa itama.

Nesa da gadon ya tsugunna ya hau haska gadon sai dai bai ga alamar komai ba.

Yaya Abu kuwa ta gwallo ido tana "baka ga komai ba"?

Kabiru bai kulata ba ya cigaba da haskawa ganin bai ga komai ba yasa ya mik'e tsaye ya ajiye

wayarsa a gaban mudubi da sandar hannun sa ya nufi Kan gadon ya d'auki Sajeeda da har lokacin take kuka ya ajiyeta a Kan 2 Seater dake cikin d'akin ya daga katifar sama.

Yaya Abu dake bakin kofa ta saki ihu tana "Wallahi Aljanine ya rike min kafa ya taska min mari innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

Kabiru kuwa shi kansa sai da kansa ya daure da mamaki dan tabbas yaji karar Marin da aka yiwa Yaya Abu ta kasan gadon ya Kuma ji motsi amma sai gashi ba kowa a kasan gadon.

Yadda yaga Yaya Abu na cigaba da ihu a tsorace har su Annur dake d'akin su sai da suka fito yasa yacewa Yaya abu "Dan Allah ki bar ihun nan haka Kinga dai ba kowa a kasan gadon kila Aljanine ya ga zaki yi ba daidai ba ya cafo kafarki ya waska Miki mari, daga yau Sajeeda bazata Kara kwana a d'akin nan ba sama zan maidata dan Kamar zamanta a d'akin nan hatsarine"

Daga haka ya saki gadon ya nufi wajen Sajeeda da ta zaro ido tana gurnani

Yaya Abu da ta mugun tsorota dan ta gama yarda Aljanine ya ja kafarta ya waska mata mari ta shige dakinta da sauri ta kulle ta zauna a gefen gado jikinta na wani irin rawa ta yarda yadda Nuratu ke da Aljannu Sajeeda ma na dashi,dan tunda ta kuduri niyyar kashe Sajeeda ta daina cin abincinta idan har ba Aljannun ta ne suka fada mata ta saka magani a abincin ba ba yadda za'ayi tak'i ci,yau da ta so amfani da pillo Kuma Aljanin ya ruko mata kafa, tsoronta ma kar Aljanin ya biyota daki ya kasheta tunda ya b'ace daga kasan gadon.

Wani irin zabura tayi ta nufi kofarta ta bude tana kalle kalle,har zata doshi d'akin Yesmeen ta fasa dan dakin Yesmeen ma ya mata nisa nasu Annur ne a gefenta.

Ta fada dakinsu da sauri ta rufo k'ofar duk suna zaune da Alama basu koma bacci ba ta haye gadonsu ta kudunduna ta rufe idonta,tabbas Sajeeda nada Aljannu babu tantama da alama burin da taci na auren Kabiru ba zai tab'a yuwa ba dan dak'yar Aljannun ta su barta ta zauna lafiya idan ta ma samu nassarar kashe Sajeedan yanzu ma sajeedar tsoron ta take ji,a kwancen da take ta tafi tunanin suna Yara lokacin da ta addabi Nuratu mahaifiyar Yesmeen da Sajeeda,ranar da ta Zo ta hada musu sharri a kan su suka cinye abincin Babansu mahaifiyar su ta zane su,a ranar Nuratu Aljanunta suka tashi ta shaketa da bango har gobe da tabon a wuyanta shi yasa Sam basa shiri da Nuratu har kowa ya Kama gabansa har Kuma suka manyanta bata manta shakar ba dan farcenta ta soka mata a wuya,kila irinsa ne da Sajeeda, tsoro ne ya Kara rufeta,ta cije lebbenta tana hararo Asarar da zatayi na rasa arzikin da ta ciwa buri,tuna yadda taga Kabiru dazu da yaje d'akin Sajeeda ya saka ta mik'ewa zaune,mamakin yadda Kabiru zai nemi Sajeeda da gabanta ke fidda ruwa kawai take,da yanzu bata je d'akin ba haka zai nemi Sajeeda kila shi ma ya kwaso cutar yazo ya zuba mata idan da ta samu nassarar kau da Sajeedar, tuni taji tsigar jikinta na tashi har yawu na taruwa a bakinta dole Kabiru yaso Kara Aure,idan har shaawa na iya sawa ya nemi Sajeeda da Babu abin mora a jikinta,haka tayi ta juye juye tana tunanin kila ma Yana can Yana neman Sajeeda tunda ya haye da ita

sama,zata san yadda zata yagi rabonta kawai amma bazata tab'a iya auren Kabiru ba Koda Sajeeda ta mutu sai dai idan roba zai ringa sawa.

Yesmeen a hankali ta fito daga sip din ta jike da gumi Kamar an watsa mata ruwa,har yanzu jikinta bai dainawa rawa ba,dan ta hararo kalar shaka da dukan da zata Sha a wajen Yaya Abu da Kabiru ya ganta a kasan gadon,ita kanta bata san yadda tunanin wanka mata mari yazo Mata zuciya ba,cikin sand'a ta fito daga d'akin dan ba motsin da take ji,ta kalli matattakalr bene tana tunanin halin da Sajeeda ke ciki, hankalin ta ya tashi da sama da Kabiru ya maida Sajeeda dole tasan yadda zasu gudu a kurkusa,a yanzu ma so take ta samu wayar Hamza tunda shi yasan tana gani ta Kira Nusrah a waya ta fada mata halin da ake ciki,ko ta Kira Gwaggo idan har basu samu guduwa ba dan yau da gobe idan asirinta na rufuwa na karyar makanta watarana dole asirinta ya tonu,yau ma Allah ne ya tsallakar da ita.

Har zata haye sama ta tuna hatsarin da ke cikin hawa saman, Kabiru na iya Kamata.

Haka ta koma d'akinta,ta watsa ruwa ta daura alwala mai kyau,ta saka wani sabon doguwar rigarta da wata kanwar mahaifin ta ta taba Aiko Mata tsaraba tana balain san rigar shi yasa ta kasa sawa.

Bayan ta saka ta d'auko wankakken hijabinta na islamiya da yaje mata har kasa ta zura ta hau kan sallaya.

Sajeeda

Ina ji Ina gani Abban Nusrah ya hau dani sama sallati kawai nake a zuciyata Ina rokon Allah akan ya kareni daga sharrrinsa sai da hannuna ya fara motsi,inaso na tonawa Abban Nusrah asiri ta hanyar rubutu a waya sai gashi ta karfin tuwo yake so ya nemeni ta baya wallahi ko makiyina bana Masa fatan ya Shiga irin halin da na Shiga.

Wani daki ya shigar Dani da bansani ba ko dakinsa ne tunda ban taba Hawa saman ba ya kwantar dani har lokacin jikinsa a tsaye yake.

Hawaye kawai nake Ina girgiza kaina gurnani da Ina ga ya zame Masa sabo na fara yi.

Ya zauna a gefena yana "Yi hakuri Sajeeda ban taba tunanin akwai abinda zai iya cutar dake ba zamanki a d'akin kasa ba  amma yanzu ki kwantar da hankalin ki kina kusa dani, ko Yaya Abu bazan Kara yarda tazo kusa dake ba,dan banji na yarda ba kasheki taso yi ba tunda da idona naganta tana san danne pillon dake fuskarki,idan ma na samu nayi auren,sawa zanyi kawai ta tafi nima sai nafi sakewa,Kinga yanzu kin fara iya motsa hannun ki,gaba gaba in Sha Allah magana zakiyi Sajeeda Kinga halin da nake ciki"

Ya rike hannuna ya Kai jikinsa da naga Yana Motsi shi kadai yayi kasa da murya Yana "ki

taimaka ki sama min nutsuwa"

Kaina na fara girgiza Masa hawaye na zubomin.

Ya mik'e Yana nayi hakuri ya daukeni ya kaini bandaki ya sake wankeni kamar yadda yayi jiya ya kwantar dani,yadda Naga jikinsa bana Jin akwai abinda zai kwantar dashi,dan jikinsa har wani rawa yake idonsa jajjur,na sadakar da rayuwa wanan shine kaddarata sai na fara hangoni a kwance bana iya rik'e kashi,gabana na fidda ruwa,kila har tsutsotsi su ringa fitomin na rufe idona da naji ya daga kuguna sama kafafuna akan kafadarsa.

Jira nake ya tura jikinsa ta bayana naji shiru,hakane yasa na bud'e idona naga ya hada gumi jijiyoyi sun fito Masa a goshi Yana ta mulmula jikinsa da hannu daya Yana "Na shiga uku Mai haka"?

Sai na maida idona na lumshe na hau yiwa rabbi kirari,dan wanan yinsa ne Ina ma Ina da yadda Zan tashi na gode Masa ta hanyar sallah raka'a biyu amma bani da wanan damar sai sallati da nake yiwa mafi soyuwa a gare shi, kamar dai jiya haka yayi ta fama Yana yawo Zigidir a tsakar d'akin,hankalinsa yafi na jiya tashi Dan kwanciya tayi lagwaf ta kankance,haka ya cigaba da zirga zirga Yana jijiga sai da ya gaji ya ja gajeran wandonsa ya saka yayi waje

Nabi bayansa da kallo Ina "In Sha Allah har Allah ya kawo Mai taimaka min bazaka tab'a samun abinda kake so ba tsinanne dan wuta,sai da ya fita na fara tuno abinda ya faru awani da suka wuce a d'akina,haka kawai na saki murmushi Ina jinjina karfin halin Yesmeen na wanke Yaya Abu da Mari da ko ni da nake kanwarta bana Jin zan iya Kai hannu jikinta ta wani barin sai naji dama abu ta buga mata akai,wajejen karfe hudu bacci yayi awon gaba dani.

Bansan tsawon lokacin da na dauka Ina bacci ba sai muryar Abban Nusrah da na Hamza naji a d'akin.

A hankali na bud'e idona sai naga annur da Hamza ne cikin shirin manyan Kaya da akwati a hannunsu Abban Nusrah Kuma waya ce a hannunsa tuni na wartsake Ina kallon su gabana na faduwa ba Wanda nake so yanzu na jawo jikina yasan sirrin mahaifin sa sama da Hamza Mai Abban Nusrah ke nufi, maganar Abban Nusrah ya katse min tunanin da nake.

"Mota na waje na jiransu Abu ma tana cikin mota zasuje can wajen Nusrah tunda sun yi hutu,duk sai su dawo tare".

Gurnani na fara yi Ina girgiza kaina na hau yafito Hamza,Hamza na k'ok'arin zuwa wajena Abban Nusrah ya daka Masa tsawa akan su wuce su tafi.

Haka suka tafi suna waigena hawaye na zubo min.

Ina Jin muryarsa a kasa ba dama na sauka.

Yaya Abu kuwa da tsoro ta tashi washegari,dan haka ta ringa zuba mafarki,wajen shidda Kabiru yazo ya ringa buga k'ofar su Annur Hamza na bud'ewa ya shigo ganin ta a d'akin ya bashi mamaki ya tambayeta mai take yi a d'akin,ta kada baki tace tsoro take ji dan tabbas Aljannun Sajeeda ne ya mareta,ita tana tunanin ma Malumfashi zata tafi idan an kwana biyu ta dawo.

Kabiru da ta bashi dariya ya girgiza Kai Yana ta manta yau zasuje wa Nusrah dan haka ta shirya karfe tara zasu tafi,idan ta tashi tafiya ta tafi dasu Hamza tunda sunyi hutu,da saurinta ta hau shiri dan gwara taje wajen Nusrah kila zuwa ta dawo ta dan samu nutsuwa,Koda suka gama shiryawa Dubu dari ya d'auko ya bata akan ta rik'e tuni taji wani irin farinciki ya rufeta,dan tasan kudin mallakinta ne.

A haka suka shirya Suka dau hanya Kabiru na daga musu hannu.

Sajeeda

Ina Jin tashin motar su Hamza da na ringa yiwa Addu'a dawowa lafiya,ba jimawa Abban Nusrah ya hawo sama da abincin karyawa.

Sai da ya d'auko baho yamin brush,ya bani shayi da dankalin Ina gama ci.

Daga wayar ta gane wai kungiya zaa kaita a haukatata,tuni ta dage da Addu'a a zuciyarta,ta ringa yiwa Annabi sallati tasan bawa bai Isa ya kaucewa kaddararsa ba,kila tata kaddarar kenan.

Tana ji tana gani ya sabata a kafadarta ya fita da ita ya kaita cikin mota, Addu'oi ta cigaba da yi tana Daga bayan mota tana Jin Yana magana shi kadai,  ji take kamar ta tashi ta Kai mishi shaka ko ta Kama steering din motar, dan bata tab'a sanin Kabiru zai iya rufe ido akan neman duniya ya kauce hanya har haka ba,Ashe duk kudin Nan da yake facaka dashi ba na Allah da Annabi bane,Ashe Kabiru kungiya ya shiga,tuni taji tausayin Sajeeda ya cike Mata zuciya,Ashe

duk halin Nan da take ciki, Kabiru ne sila,ina ma tana da yadda zata tonawa Kabiru asiri,so take ta mik'e daga bayan motar ta hau danna ihu amma jikinta da zuciyarta sunki bata had'in Kai,tana ji tana gani zaa kaita Wai wani kungiya.

Addua kawai take dan tasan Allah maji rokon bawansa ne Allah kadai ne zai tsallakar da ita.

Tana Jin lokacin da suka iso  ya  kinkimeta daga bayan motar idonta a rufe yake, amma tana Jin lokacin da ya kwantar da ita Yana magana da wani,,addua kawai take a zuciyarta maganganun da taji suna yi akan Yesmeen ya matukar girgiza ta,ba iya fyade ma yake so yayi wa Yesmeen ba kasheta suke so suyi,mai Yesmeen ta musu da zafi haka, ko dai itama sirrinsa ta gano shi yasa suke so su kasheta,sai da taji maganar da suke ta gane Ashe Yesmeen  ba makancewa tayi ba tana gani,ashe Yesmeen sirrin Kabiru tasani shi yasa tayi karyar makanta, haka ta kwanta Kamar mataciya har taji an taba kanta da Abu sau uku da kafin a tabata addua kawai take a ranta.

Jin a watsa mata ruwa yasa ta ja dogon ajiyar zuciya ta dan bud'e idonta.

Taji shugaban na yanzu ta samu tabin hankali suje su kaita wajen Tasha bazata tab'a iya tona musu asiri ba idan sun ajiyeta yaje yasan yadda zai nemi Yesmeen ya kawota su kasheta.

Haka suka tayar da ita Suka jata mota,ta ringa yiwa Allah godiya da ba abinda ya sameta.

Dan tasan ita dai a hayyacinta  take,tana Jin yadda Kabiru ke tsalla gudu wai dan ya ajiyeta yaje wajen Yesmeen.

Suna ajiyeta Suka ja motar aguje,sai da ta daina hango motarsu ta mik'e  a hankali tana Jin jiri na daukarta,dan ji take kanta Kamar baa jikinta ba,bata san yadda akayi ta zub'e a kasa ba,sai muryar wasu maza taji a kanta rashin kwari da k'arfi ya hana ta motsawa,a haka suka kinkimeta sukayi chemist da ita,yadda bayan keyarta ya kumbure yasa suka dauka hatsari tayi ta buge a kai,tuni aka mata treatment wayanda suka kaita dayake masu mutuncine Suka biya kudin magani har abinci suka siya mata, da maltina tana ci kuwa ta dan ji kwari kwari,ta roke su akan tana so tayi sallah tafiya tayi gidan da tazo Bata same su ba ba Kuma Wanda tasani a garin,tuni mai chemist yace ta Shiga cikin gidansa dan chemist din nasa a jikin gidansa yake.

Sai da ta rama duk sallolin dake kanta tana ta godewa Allah daya kareta daga sharrin Kabiru,ganin matar nada sakin fuska yasa ta nemi arzikin aron wayarta.

Ta kuwa bata aron wayar ta saka lambar mijinta ta Masa flashing.

Take kuwa ya kirata Yana Jin muryarta ya saki ajiyar zuciya yana "kin bi kin daga mana hankali Mai ya samu wayarki a kashe"

Yaya Asmau kuwa tace Masa kalau take ta Yar da wayar ne ya taimaka ya saka mata kati ta

layin nan yanzu ya Kuma turo Mata lambar Gwaggo,dan tasan idan har ta fada Masa abinda ke faruwa zai iya cewa zai taho a daren,ya Kuma dagawa kansa hankali,a yanzu fadawa Gwaggo halin da ake ciki kawai take so tayi,a samu aje a taimakawa Sajeeda da Yesmeen dan addua kawai take akan Allah ya Kare Yesmeen daga sharrin sa,sosai tausayin Yesmeen ke daiwaniya da ita,Ina ma tana da yadda zata je ta taimaka mata,duk tambaya da ya mata bata iya bashi amsa ba haka ya kashe wayar ya saka Mata katin dari biyar ya turo lambar Gwaggo ta layin

Tana Kiran Gwaggo ta dauka tana Jin muryarta itama ta hau godewa Allah tana Mai ya samu wayarta Mai ya sameta?
Yaya Asmau da ta fita can waje ta hau labartawa Gwaggo duk halin da ake ciki,ba abinda ta rage har yadda ya kaita kungiya dan ya haukatata, Gwaggo ihun sallati kawai take har sai da taji mahaifunsu Sajeeda ya karbi wayar shi ma ta labarta masa tana a taimaka a ceto Sajeeda daga hannunsa a taimaka a ceto Yesmeen.

Hankalin Abban su Sajeeda a tashe ya hau cewa ta taimaka ta kirawa Kabiru Yan sanda

Yaya Asmau kuwa tace bazai yu ba tunda Yana da kudi,zai iya Basu cin hanci,anan baban Sajeeda yace zaiyo shatar mota gobe da safe suzo shi da Gwaggo su dirar masa idan sun iso zasu kirata ta layin su hadu su je gidan.
Da haka sukayi sallama washegari kuwa suna isowa Suka kamo hanyar gidan Kabiru kowane bakinsa d'auke da Addu'a Allah yasa Kabiru bai cutar da Sajeeda da Yesmeen ba, Gwaggo kuwa sai kuka take

Kabiru

Ihu ya fasa da "Shikenan asirina ya tonu"

Yaja da baya jikinsa na wani irin rawa ya zubawa Asmau ido da take kallonsa.

Yaya Asmau kuwa ta saki murmushi tana "Kana mamakin ganina ko?ka dauka na haukace ko ka dauka zaka cigaba da samun nassara a duk abinda ka saka a gabanka na zalinci ko? Kabiru da Allah na dogara ban hada bautarsa da kowa ba,shi yasa ya tsareni ya kareni daga mugun nufinka,Duk abinda kayi jiya Ina kallonka ba Suma nayi ba har kungiyar da ka kaini da kake tunanin an taba kaina saboda na samu tabin hankali Ina cikin hayyacina, Kabiru,na gano sirrinka a yau asirinka ya tonu,dan su Gwaggo ma sun san Kaine ka cutar da Sajeeda

Kabiru da jikinsa ke balain rawa da kafafu zubewa yayi akan gwiwarsa ya sunkuyar da kansa Yana Jin Kamar numfashinsa ya d'auke saboda tashin hankali kukan Sajeeda kawai ke tashi da na Gwaggo da ta rungimeta,Sajeeda kuwa cewa take "Gwaggo mijina uban yayana shi ya nakastamin rayuwa saboda ya samu kudi, Gwaggo ko a mafarki ban taba tunanin Kabiru zai

tab'a min haka ba,umma yayata da muke uwa daya uba daya wai ita take so ta kasheni saboda ta samu ta aure shi,Yaya Abu haka ta ringa saka min guba a abinci wai dan naci na mutu Allah na kareni,Yesmeen na kareni,a yanzu saboda san kudi ta sallamawa Kabiru kanta ya nemeta Wanda nasan dan biyan bukatarsa ya nemeta,mai na musu haka da na cancanci haka daga wajensu,cikin kuka Sajeeda ta hau labarta musu yadda Kabiru ya kwanta da Kare yazo ya kwanta da ita Wanda daga lokacin ta kwanta rashin lafiya,tana Basu labari tana kuka,

Su Gwaggo kuwa Suka  kaure da sallati,  Kabiru kuwa da ke ji dama kasa ta bud'e ya shige ya Kara sunkuyar da kansa Yana Jin kirjinsa na bugu fiye da misali,mai ya rage masa Kuma Babu asirinsa ya riga da ya tonu fakar idonsu yayi,duk da ba riga a jikinsa yayi waje da balain gudu dan bazai iya kallon su ba,Yanzu dama duk tsawon lokacin nan Yesmeen ta fadawa Sajeeda sirrinsa Ashe duk tsawon lokacin nan Yesmeen ta San komai a kansa,Ashe lokacin da ya kwanta da Kare Yesmeen ta ganshi, motarsa ya fada ya samu wani riga a bayan motar ya saka ya tadda motarsa dan bai fiye zare mukullin mota ba a jiki yake bari.

Jikinsa rawa kawai yake ya figi motar dan horn din fitar hankali ya ringa dannawa Mai gadi.

Yana kallon lokacin da Yaya Asmau ta biyo shi a baya tana magana baisan Mai take cewa ba,ta tabbata shugaba bai iya komai ba, tunda gashi Yaya Asmau bata haukace ba gashi ta tona Masa asiri.

Babansu Sajeeda da Gwaggo sallati kawai suke,dan ko a mafarki basu tab'a kawowa Kabiru arzikinsa bana halal bane,

Da ido Suka bi shi a lokacin da ya kwasa da gudu yayi waje,sai Yaya Asmau ce ta bi bayansa tana yazo ya fada mata Inda ya Kai Yesmeen ya bawa Sajeeda takarda ta,

Tana komawa ciki ta nufi d'akin Sajeeda dan ta ga Yaya Abu da itama ta matukar bata mamaki,tana Shiga ta hango ta buya a wajen wadrobe dan tana jiyo muryarsu,da kunya Gwaggo da Babansu su san mai ta aikata,da kunya,wani irin radadi take ji a jikinta,da azabar kaikaiyi,tuni taji hankalinta yayi matukar tashi ta fara tsoron Kar dai ya nemi Sajeeda ne yazo ya kwanta da ita,da kuwa ya cuceta,idonta ya rufe da san kudin shi yasa ma bata nemi ya saka roba ba.

Shigowar Yaya Asmau da ta tsaya tana kallonta yasa tayi saurin sunkuyar dakai

Yaya Asmau kuwa ta fara magana tana "tirrr da ke Abu tirrr yanzu akan kudi Kika Bari mijin kanwarki ya kwanta dake?yanzu akan kudi kike so ki kashe Sajeeda ?dama haka kike Abu"?wallahi kinyi asarar rayuwarki ban taba zaton zakiyi haka ba,Ina tausaya miki dan kin cutar da kanki,akan kudin da ba na halak ba Kika kassara rayuwarki Abu,akan kudin da bana halak ba kikaci amanar kanwarki,Ashe ba dan Allah Kika zauna ba,kina da wani nufi a

Zuciyarki"?kaiconki Abu dan kin kashe kanki da kanki, Kabiru dan yankan kai ne,Kabiru kudinsa na jini ne, Kabiru kudinsa ba na halal bane,dan biyan bukatarsa ya nemeki dan kema ya kassara rayuwarki kamar yadda ya kassara na Sajeeda dan ya samu kudi,

Yaya Abu wani irin ihu ta saki cikin tashin hankali tana "Na Shiga uku na lalace innalillahi wa Inna ilaihi rajiun wayyo Allah na dama dagaske Nusrah take ya akayi Kika sani Asmau"

Tsaki Yaya Asmau tayi ta bar d'akin Yaya Abu kuwa ta ringa zunduma ihu tana ta shiga uku taya zata koma kamar Sajeeda Kabiru ya cuceta.

Sajeeda.

Kuka kawai nake bayan na bawa su Gwaggo labari, mahaifina ma ya kasa motsi saboda mamaki, Gwaggo kuwa sai kuka take tana godewa Allah da na warke Kabiru Kuma baiyi nassarar kasheni ba,Yaya Abu kuwa abinda take nema ta riga da ta samu.

Duk ihun da Yaya Abu ke yi muna jinta, babanmu ficewa kawai yayi daga palon Yana a su fito mu tafi baya San mu Kara ko da second daya a gidan Kar a sake a dauki komai a gidan,Kuma Kar Yaya Abu ta sake ta tako masa gida.

Gwaggo kuwa tuni ta rik'e hannuna dan gidan ma tsoro yake bata Yaya Asmau ta rik'e daya hannun nawa muka yi waje,Mai gadi kallon mu kawai yake har muka bar gidan,bamu yi nisa a tafiya ba Muka ga wani mota ya wuce mu can Kuma motar ta dawo baya.

Cikin ihu naji ance "Ummaaaa"

Muka waiga gabadaya muna kallon Nusrah dasu Hamza,Annur ya taho wajena da gudu hawaye ya hau zubomin da naji yana "Umma kin warke"???......

ASSALAMUALAIKUM AUNTY ZEE MOM MUJAHID TAKUCE

INGATACCEN MAGANIN SANYI MAI WANKO DUK DATTIN MARA DUK WANI ABINDA YA TOSHE MAKI HANYAR SADARWA SHIN NI IMA NE BAKIDA SHI ZAFI KIKEJI YAYIN MUAMALA
RASHIN NI IMA BAKI JIN SHA AWA NE? RIKICEWAR AL ADA ?FITAR FARIN RUWA MAI WARI BUDEWAR GABA TALEWA MALEWA KURAJEN CIKIN FARJI KURAJEN JIKI DAUKEWAR AL ADA RASHIN HAIHUWA

BANGAREN MAZA  RASHIN KUZARI
KANKANCEWAR GABAN NAMIJI SAURIN KAWOWA RASHIN JIN SHA AWA JIN ZAFI YAYIN MU ALA DA MATANKA HMMM KEDAI KISHA KEDA MIJINKI ZAKITASHI MAN ALBARKA KODA YAUSHE KADA KIYI SANYA KICE KIN GWADA MAGUNGUNA KIYI HAKURI KI GWADA WANNAN KANKAT NE BI IZINILLAH

GAME DA MASU NEMAN HAIHUWA KIYI KOKARI KU GWADA ANGWADA ANDACE INA KATSINA INA AIKA KAYA KO INA DA YARDAR ALLAH KUDIN MAGANIN KO WANI GALLON 4K KUMA KEDA MIJINKI ANA SO KOWA YASHA GALLON DAN GIRMAN ALLAH IDAN BAKI SHIRYA BA KARKI BIYO NI YAN FLASHING KUYI HAKURI DAN ALLAH SAI NAJIKU DIN INKUN SHIRYA🤪KUKIRA KAI TSAYE 08162859027

ALBISHIRINKU 🥳🥳 ALBISHIRINKU 🥳🥳🥳🥳 MANYAN MATA
Takunce dai A&Z COLLECTION takara zuwa muku da kayanta masu sauki da inganganci👌👌

Muna da supplement nau,i kala kala

Sannan akwai sabulu Mai suna HALFCAST SOAP hmmm hajiyata duk yadda za,ai karki Bari abaki labarinshi Dan sabulune dayake aiki cikin kwana uku kacal 👌zakiga yadda kalarki zata koma kiyi haske me kyau bana bleeching ba haka Zaki dinga sheki kina haskawa acikin jama,a 🔥🔥🔥
Koda kindaina amfani dashi ba,abunda fuskarki zatai saboda  natural ne Wanda sukai bleeching yabata musu jiki dafuska Kuma kunemeshi Yana dawo dakalar fata baidaya bacan Baki nan fariba 😄
Akwai cream gamasu San suhada set Wai ai hajiyata saikin zama taurariya acikin taurari mudin kika mallakeshi💃💃💃
Kira ko WhatsApp 09037870422

Karku manta muna da supplement kala kala

Na matsi
Na gyaran breast
Na hips
Na slimming
Na fari
Na gashi
Dasauransu

Haka zalika muna :

HADIN MAI  JEGO
HADIN UWARGIDA
HADIN AMARYA

Kuma duka afarashi me rahusa kedai kawai kituntubeni 👇👇
09037870422

Muna garin kano muna tura Kaya ko,Ina cikin aminci 🤝

Sai Allah yakawoku

*WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE 89*

Sajeeda

Kabbara kawai nake a lokacin da ya rungumeni Yana "Ummana kin warke"?

Jikina har rawa yake wajen rik'e shi bansan kalar godiyar da Zan yiwa Allah ba lokaci guda Allah ya warkar dani da dana,cikin tsananin farinciki na fara magana Ina

"Annur yaushe ka fara magana Kai ma"?

Isowar Nusrah gabana da ta zub'e a kasa tana hakki yasa na maida hankalina kanta cikin muryar kuka ta fara magana tana "Mafarki nake yi ko gaske umma kece yau nake gani a tsaye har kina magana garin Yaya Kika warke Gwaggo babba Asmau ku fadamin ba mafarki nake ba umma ce nake ganin ta a tsaye da na dauka Abba ya cutar min da ita, Umma bansan halin da kike ciki ba kenan wallahi bansani ba,sai da Yesmeen ta kirani jiya"

Gwaggo Ina za kuje,dak'yar Abubakar ya barni na taho dan ce masa nayi Umma na balain Jin jiki,kinsan gobene suna"

Sai a lokacin nayi magana Ina "Nusrah har yanzu ba kwarine dani ba,mun fito ne zamu tafi gida,sai dai ku bimu mu tafi,dan ban yarda wani a cikinku ya Kara taka gidan can ba"

"Yanzu dagaske ne Abba kudinsa bana halal bane"?yanzu dagaske ne Abba shine yayi kudi dake"

Murmushin takaici nayi da naga Wai ma kwokwanto take,

Tana k'ok'arin magana Yaya Asmau ta dakatar da ita tana mu tafi kawai.

A hankali Muka cigaba da tafiya dan babana gaba yayi ya barmu a baya.

Ganin yarana a tare dani da suke murnar warkewa ta  yafi komai faranta min,ni nasan karshen Kabiru yazo tunda asirinsa ya tonu,alkadarinsa ya karye tunda har muka warke nida Annur.

Yanzu Kuma Yesmeen ce a Raina tunda Gwaggo tace bata je ba,Yaya Asmau itama sai maganarta take muna Kan hanya tana Kara daga min hankalin maganganun da taji Kabiru nayi da Yan kungiya a kanta,akan zasu kasheta

Tuni na fara kuka wiwi dan zan iya d'aukar komai, matakin da zan dauka akan Kabiru na rabuwa ne,Zan rufe sirrinsa ga mutane saboda yarana bana so laifin mahaifin su ha shafe su,amma indai Kabiru ya tab'a Yesmeen wallahi sai Inda Karfina ya kare har kashe shi zan iya yi, Yesmeen bani na haifeta ba amma kaunar ta a zuciyata take,matsalar ba wani sanin wajen dangin mahaifinta tayi ba,gashi bata fadamin Inda zata gudu taje ba.

Har muka iso Tasha Hankalina baa jikina yake ba,

Mahaifina ya fara laluba Mana motar da zai Kai mu har can,muka samu waje muka zauna.

Ina Jin Gwaggo da Yaya Asmau nata hirar Kabiru Nusrah na kuka,Hamza da Annur sunyi jingum jingum,amma ni zuciyata na wajen Yesmeen.

Wani bakin mota ne ya shigo ya wuce ta gabanmu nabi motar da kallo,dan gaba da mu naga motar ta tsaya,Kamar wacce ake bawa umarni na zubawa motar ido, wani kyakyawan saurayi ya fara fitowa daga motar kafin a bud'e daya bangaren wata sanye da farin hijabi ta saka nikaf itama ta sauko daga motar,

Haka kawai naji kirjina ya buga,sai na zubawa mai nikaf din ido, da ta bamu baya.
Saurayin ya zagayo ta wajen da take tsaye ya hau magana Yana wuwurga hannu Yana nuna

motocin,dake zube a Tasha.

Ni dai ido na zuba musu bansan dalili ba naga saurayin ya nufi wajen da aka jera motocin katsina Dan akan motar na gane motar katsina ce dan an rubuta a jikin wani katako an dora akai.

Mai niqaf din Kuma ta jinjina a jikin motar,ni kaina bansan Mai yasa na zuba Mata ido ba har saurayin ya dawo ya mata magana yayi gaba ta fara bin shi a baya a hankali kamar wacce bata so,har Suka isa wajen motar kallon su kawai nake saurayin kuwa sai magana yake Yana leka fuskarta,haka kawai nake hango Yesmeen a tare da mai niqaf din,irin tsayuwar Yesmeen da tsayinta,bansani ba ko dan Ina tunaninta yasa na fara hango yanayinta a wajen mai niqaf din,suna tsaye idona akanta,da alama a takure take dan saurayin ya dage sai zuba yake idan tayi hanyar motar sai ya sha gabanta sai mika Mata wayar hannun sa yake,nidai ido na zuba musu suna tsaye na Kuma kasa d'auke idona akansu har sai da babana ya dawo Yana mu tashi ga mota can,a hankali na mike Ina k'ok'arin d'auke kaina daga kansu naga ta daga niqaf din ta sama,naga Yesmeen dita ce idan har ba gizo idona ke min ba,Yaya Asmau ce a gefena hakane yasa na damko ta Ina "Yaya Asmau duba min can Kamar Yesmeen nake gani ko idona ne?

Da sauri ta waiga sai ji nayi ta kwalla mata Kira da "Yesmeen"!!!

Yesmeen ta juyo da sauri tare da kallon Inda taji sunanta.

Tabbas Yesmeen ce ba gizo idona ke min ba,a daidai lokacin da ta kwaso da mugun gudu tana isowa gabanmu kamar wacce wuta ya jata ta daskare a tsaye tana kallona bakinta a bud'e.

Ni kuwa hawayen farinciki ya hau wanke min fuska nima Ina kallonta,

Kamar Mai koyon magana tace "Umma kece ko mafarki nake yi?

"Nice Yesmeen ba mafarki kike ba"

Wani Irin cafka ta kawomin ta rungumeni ta fashe da kuka tana "Umma Ashe akwai ranar da zan Kara Jin muryarki,umma ashe akwai ranar da zan ga kin tsaya akan kafafunki,dan Allah karku tasheni idan mafarki nake.

Nima kankameta nayi cikin kuka Ina "Ba mafarki kike ba yesmeen Allah ya warkar dani,Allah yayi ikonsa akaina Allah ya amsa adduar da kike Dade kina min"

Cikani naga tayi ta zub'e akasa tare da yin Sujadda sai kuka take tana "Alhamdulillah ya Allah Alhamdulillah Alhamdulillah Allah nagode maka"

Sai da ta dade a haka daidai da mahaifina sai da idonsa ya ciko da kwalla,

Tana dagowa tana "Umma a yanzu da Kika fara magana Zaki wankeni a wajen Nusrah,tace ni muguwa ce saboda ba ke Kika haifeni ba shiyasa naki fadawa kowa halin da kike ciki,umma ke zaki wankeni a wajensu"

Har ga Allah ji nayi raina ya b'aci na kalli Nusrah dake zare ido na fara magana Ina "Au haka kikace dan bani na haifeta ba shi yasa bata fada muku ba, kunsan abinda Yesmeen tayi min kuwa?so kuke ta fada muku mahaifinku ya kasheta"

"Umma dole naji haushinta kema kinsan yadda nake da ita,idan ta fadamin bazan nunawa Abba nasan komai ba iyakaci na Kira Gwaggo a waya na fada mata da kila baki dade haka ba umma ace duk tsawon lokacin nan Yesmeen tasan abinda ke faruwa sai ta ja bakinta tayi shiru umma dole naji haushinta"

Ina k'ok'arin magana mahaifin mu ya dakatar dani Yana ya isa haka mu wuce ana jiranmu.

Yesmeen kuwa tana ganowa Annur na magana ta Kara fasa ihu tana hamdala tama kasa tsayawa waje daya.

Kuka hade da farinciki haka muka ringayi har
Haka muka je Shiga mota Ina godewa Allah da ban wahala wajen Neman Yesmeen ba,ko Wanda ya kawota tashar bata kara kallon wajen da take tsaye ba har muka tafi.
ta rik'e hannuna Tama kasa cikani sai tambayoyi take min akan ya akayi na warke?Ina Abba ya akayi su Gwaggo Suka zo?

Ta hau bani labarin yadda ta fito taga su Kabiru da yadda ta gudu wasu bayin Allah suka taimaka Mata,ta kwana a yanzu ma dan mai gidan ne ya kawota tashan dan karya ta musu.

Murmushi kawai nake dan da alama Yar tawa tayi saurayi

Sosai nake k'ok'arin danne zuciyata dake san tuna min Yaya Abu da ta cutar da kanta akan kudin,da zaa mutu a bari a gidan duniya,yau akansa ta kassara rayuwarta,tsigar jikina sai tashi yake da na tuna irin wahalar da na Sha.

KABIRU

Yana fita daga gidan ya hau neman Rabiu a karamar wayarsa sai ihu yake Yana "Ka cuceni Rabiu ribar Mai na samu a Shiga kungiya,yau gashi asirina ya tonu,tun ban mori kudina ba,duk wahalar nan da na Sha ko shekara biyu banyi ba,Sajeeda ta gano sirrina,iyayenta sun gano sirrina yarana sun gano sirrina mai ya rage min kuma"

Kuka kawai yake yana cigaba da Kiran Rabiu da bai San adadin miscal din da ya Masa ba.

Yana k'ok'arin ajiye wayar yaji an dauki wayar hayaniyar da yake ji yasa ya kasa Jin Mai ake cewa ya kashe wayar ya sake Kiran wayar.

A madadin yaji muryar Rabiu sai muryar wani yaji Yana "Mai wayar nan yanzu nan wani tirela ya murkushe motarsa ko shurawa baiyi ba,dan trilar ta tsatse shi"

Wani irin ihu Kabiru ya saki tare da taka birki da k'arfi Yana "Rabiun ne ya mutu yanzu kana nufin ya rasu"

Kashe wayar yayi ya fito daga motar a kidime kamar sabon mahaukaci haka ya ringa zunduma ihu dan ko a yau haka Suka ringa waya dashi,yana fada masa ya samo tsalalliyar yarinya zai je ya kwashe arzikin ta.

Ya ringa zuga shi akan ya tabbata ya nemi Sajeeda ta baya yanzu idan ya samu yayi wanan aikin,sai su tafi Saudiya karshen wata suje su rage zunubi.

Tafiya kawai yake baisan Inda ma yake cilla kafarsa ba sai ihun magana yake shi kadai Yana asirinsa ya tonu, Rabiu Kuma ya mutu,Taya akayi shugaba ya bari Rabiu ya mutu,tafiya kawai yake cikin kuka,ya dauki hanyar kungiyarsu, tafiyar kusan minti ashirin ya karaso dashi kungiyar.

Ko iso bai tsaya anyi Masa ba,Bai Kuma shiga ta baya kamar yadda Suka Saba ba,Yana Shiga ya ga shugaban a zaune fuskarsa kamar a kone ya Sha bakakken Kaya fuskarsa sam ba annuri, kabiru na k'ok'arin magana shugaban ya daka mishi tsawa Yana "Karka sake kace min komai,dan Ka jawowa kungiya babbar asara,kalli Nan"?

Ya nuna mudubin dake jikin bango sai ga mutane a cike a titi, Kabiru yayi saurin kau da kansa jikinsa na balain d'aukar rawa da ganin Rabiu a tatse kamar ba mutum ba"

"Rabiu ya mutu Kabiru,duk aikin da aka ce kayi baka yi ba saboda duk ka jawo an samu matsala,hatsabibiyar yarinya nan jiya a garin tab'ata na kone a fuskata"Kabiruuu dole a dauki mataki mai tsauri a kanka,kaje ka kawo Mana jinin mahaifiyar ka,kafin ka kawo Mana ita ka nemeta idan ba haka ba Kabiru da jikinka zamu yi amfani"

"Ihuu Kabiru ya saka Yana "Bazan iya kawo mahaifiyata ba,taya Zan nemi uwar da ta kawoni duniya na hakura da yin kudin,ku cireni a kungiya na fasa,dan ba ribar da naci a Shiga kungiyar nan idan Banda tashin hankali da na jefa kaina Ina zaune cikin rufin asiri,na dage sai nayi kudi,gashi baa je ko'ina ba asirina ya tonu,matata ta San sirrina sirikaina sun San komai,yarana ma haka Mai ya ragemin babu, kace zaka min aikin da Yar uwar matata zata haukace sai gashi bata haukace ba,na gaji bazan iya ba na gaji "

"Idan aka shigo kungiya baa fita Kabiru,zaa maka sausauci idan baka so kungiya tayi amfani da jininka ka dauki karya daya ka kaita can wajen mahaifiyar ka ka ajiye idan dare yayi ka sadu da ita ka kawomin gawarta,idan ba Haka ba Kabiru nan da kwana biyu kungiya za tayi amfani da jininka dan duk asara ka jawo mana"

Kabiru a haukace ya saki ihu Yana ya gaji fita zaiyi a kungiya bazai iya ba.

Shugaba ya daka Masa wani irin tsawa ya janyo wani kaifaffen wuka Yana "kaje kayi abinda nace idan kaki ta wanan mudubin Zan kasheka da wukar Nan idan ka shirya mutuwa toh"

Kuka kawai Kabiru ya ringayi ba abinda yake tsoro a yanzu sama da mutuwa,bazai so ya mutu a halin da yake ciki ba,zai so ya nemi yafiyar Allah dan yayi mugun nadamar halin daya jefa kansa,har gwara Rabiu ya dan mori rayuwarsa shi fa ko shekara biyu baiyi ba,sai a yanzu ya ringa tuno yadda ya ringa samun matsala idan aka bashi Abu yayi,kila Allah baya San shi da arzikin Haram ya dage sai yayi.

Haka yaje ya kunto karyar da shugaban ne ya nuna Masa Wanda zai dauka.

Ya dauki karyar yayi gida dan gobe da sassafe zai dau hanyar garinsu,baisan Mai yasa shugaba yace sai ya Kai karyar gidan mahaifiyar sa ba idan asirinsa ya tonu fa.

Mutuwar Rabiu ya tsaya Masa a zuciya Bai samu yaje ya rage zunubin ba Allah ya dau ransa.

Koda ya Isa gida daure karyar yayi ya nufi cikin gidan,dan yasan su Sajeeda sun tafi bazasu tab'a zama ba,da wane ido zai kalli yarensa da wane ido zai cigaba da kallon mutane.

A hankali ya tura k'ofar palon shap ya manta da wata Abu.

Sai da ya ganta a bararraje a kasa ta wangale kafa tana ta susa da hannu biyu,tana ganinsa ta mike tayo kansa tana "Allah ya tsine maka albarka Kabiru Mai na maka zaka min irin wanan cutar,dama kudinka bana halal bane,yanzu yadda Sajeeda ke fitar da ruwa mai doyi haka Zan ringa fitar da ruwa ka kassara min rayuwa kenan?Allah ya Isa tsakanina da Kai ka cuceni"

Kabiru tureta yayi ya fara k'ok'arin Hawa sama Yana "Ki biyoni ki karbi miliyan daya da Rabin da na Miki alkawari ai bazaki samu kudi a banza ba"....

ASSALAMUALAIKUM AUNTY ZEE MOM MUJAHID TAKUCE

INGATACCEN MAGANIN SANYI MAI WANKO DUK DATTIN MARA DUK WANI ABINDA YA

TOSHE MAKI HANYAR SADARWA SHIN NI IMA NE BAKIDA SHI ZAFI KIKEJI YAYIN MUAMALA
RASHIN NI IMA BAKI JIN SHA AWA NE? RIKICEWAR AL ADA ?FITAR FARIN RUWA MAI WARI BUDEWAR GABA TALEWA MALEWA KURAJEN CIKIN FARJI KURAJEN JIKI DAUKEWAR AL ADA RASHIN HAIHUWA
BANGAREN MAZA  RASHIN KUZARI
KANKANCEWAR GABAN NAMIJI SAURIN KAWOWA RASHIN JIN SHA AWA JIN ZAFI YAYIN MU ALA DA MATANKA HMMM KEDAI KISHA KEDA MIJINKI ZAKITASHI MAN ALBARKA KODA YAUSHE KADA KIYI SANYA KICE KIN GWADA MAGUNGUNA KIYI HAKURI KI GWADA WANNAN KANKAT NE BI IZINILLAH

GAME DA MASU NEMAN HAIHUWA KIYI KOKARI KU GWADA ANGWADA ANDACE INA KATSINA INA AIKA KAYA KO INA DA YARDAR ALLAH KUDIN MAGANIN KO WANI GALLON 4K KUMA KEDA MIJINKI ANA SO KOWA YASHA GALLON DAN GIRMAN ALLAH IDAN BAKI SHIRYA BA KARKI BIYO NI YAN FLASHING KUYI HAKURI DAN ALLAH SAI NAJIKU DIN INKUN SHIRYA🤪KUKIRA KAI TSAYE 08162859027

ALBISHIRINKU 🥳🥳 ALBISHIRINKU 🥳🥳🥳🥳 MANYAN MATA
Takunce dai A&Z COLLECTION takara zuwa muku da kayanta masu sauki da inganganci👌👌

Muna da supplement nau,i kala kala

Sannan akwai sabulu Mai suna HALFCAST SOAP hmmm hajiyata duk yadda za,ai karki Bari abaki labarinshi Dan sabulune dayake aiki cikin kwana uku kacal 👌zakiga yadda kalarki zata koma kiyi haske me kyau bana bleeching ba haka Zaki dinga sheki kina haskawa acikin jama,a 🔥🔥🔥
Koda kindaina amfani dashi ba,abunda fuskarki zatai saboda  natural ne Wanda sukai bleeching yabata musu jiki dafuska Kuma kunemeshi Yana dawo dakalar fata baidaya bacan Baki nan fariba 😄
Akwai cream gamasu San suhada set Wai ai hajiyata saikin zama taurariya acikin taurari mudin kika mallakeshi💃💃💃
Kira ko WhatsApp 09037870422

Karku manta muna da supplement kala kala

Na matsi
Na gyaran breast
Na hips
Na slimming
Na fari
Na gashi
Dasauransu

Haka zalika muna :

HADIN MAI  JEGO
HADIN UWARGIDA
HADIN AMARYA

Kuma duka afarashi me rahusa kedai kawai kituntubeni 👇👇
09037870422

Muna garin kano muna tura Kaya ko,Ina cikin aminci 🤝

Sai Allah yakawoku

*WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE 90*

Yaya Abu kuka kawai take ta bishi sama tana Masa Allah ya isa, Kabiru kuwa ko kallonta baiyi ba ya shige d'akinsa  itama ta bi bayansa tana "ka bani kudin naje na nemawa kaina magani bazan zauna har sai na koma kamar Sajeeda ba,dan ita bata san cewar Kaine ka yi kudi da ita ba,batasan cewar Kaine ka Mai data haka ba,dan da ta sani da tuni ta nemawa kanta magani,tunda ni na gano amfani kayi dani dan biyan bukatar ka Saboda rashin tsoron Allah ka bani kudina na bar maka gidanan,wallahi da nasan amfani za kayi dani da ban dawo gidanan ba,na dauka Kai mutumin arziki ne"

"Ke din ta arziki ce Abu?kina yayar matata kika sallama min kanki saboda kudi,kema ai ba matuniyar arziki bace tunda har Kika so ki kashe Sajeeda saboda ki Aureni,haka kawai Zan baki miliyan daya da rabi a cikin awa daya saboda jikinki na gwal ne? Abinda Kika nema Kika samu zan Baki sama da miliyan daya da rabi na Kara Miki miliyan daya kije ki dage da Neman

maganin"

Wani irin ihu Yaya Abu ta fasa tana "Allah ya Isa Kabiru Allah ya tsine maka albarka Allah ya tona maka asiri,yadda ka cutar dani,wallahi sai Allah ya wulakanta ka,ba iya ta gaba ka nemeni ba har ta baya saboda Kai mugu ne,wallahi sai na barbazaka a ko'ina sai na tona maka asiri na fadawa duniya kai dan mafiya ne ka bani kudin na bar maka gidanan"

Kabiru kallonta kawai yake,zuciyarsa na raya Masa abubuwa da  yawa,duk da asirinsa ya tonu,bazai so mutane su san halin da yake ciki ba,duk da yasan kila su Sajeeda na iya fadawa mutanen garinsu,sai Kuma yake Jin da wuya su tona Masa asiri ko dan yaran dake tsakanin su,idan har sunansa ya b'aci kamar sunan yayansa aka b'ata,yasan salihar zuciyar Sajeeda zata iya yafe Masa Koda bazata dawo gidansa ba.

Tunanin da ya darsar Masa a zuciya yasa ya mik'e ya nuna Mata drawer akan ta kirga miliyan uku,ta fitar Masa a d'aki.

Daga haka yayi waje ya barta duk da uban kaikaiyin da take ji,cikin murna ta nufi wajen drawer,dan da kudin nan zata nemawa kanta lafiya duk Inda ta bawa likitoci dubu dari biyar tsaf zasu wanke mata gabanta da bayanta sauran kudin Kuma ta siyi karamin gida tunda Babansu yace Kar ta taka taje gidan,gabanta faduwa yayi jikinta ya kwashi rawa a lokacin da taga bandir bandir din Dubu Dubu cike a cikin drawer,jiki na rawa ta cire zanin ta,dan da under wear a jikinta,ta hau zuba kudin a cikin zanin ta banda Kabiru zai gane  da ta kwashe duk kudin,tasan bandir goma miliyan daya ne dan haka bazata tsaya daukar miliyan uku ba biyar zata dauka dan ba lailai ya  gane ba, duk da Jan kyallen da ta gani daure a cikin Abu Mai gashi gashi akan kudin haka ta ringa zuba kudin a  cikin zaninta tana murna.

Kabiru

Yana fita daga d'akin ya sauka kasa ya Kira shugaba a waya dan kila idan yayi wanan dabarar shugaba yace ba sai ya kai karya wajen mahaifiyar sa ya kwanta da ita ba.

Shugaban na dagawa Kabiru yace "Shugaba zan iya kawo jinin wata ayi amfani dashi ba sai na nemi karyar nan ba Ina tsoron mahaifiyata ta gani,Ina tsoron asirina ya tonu,bansan dalilin daya sa ka dage sai dai na Kai karyar gidanta kafin na iya saduwa da ita,bani da saa a duk abinda akace nayi,bana san mahaifiyata tasan halin da na jefa kaina a ciki,ka taimaka na kawo jinin nan ba sai naje ba"

"Idan ka kawo jinin a yanzu zaayi maka aiki da zaa rufe bakin matarka da duk Wanda Suka San

sirrinka,amma dole ka Kai karyar nan can gidan mahaifiyar ka ka sadu da ita,idan kasan akwai jinin da zaka iya kawowa ka kawo Mana yanzu Nan"

Kabiru gyada kansa yayi ya kashe wayarsa dan yasan Abu zata iya tona Masa asiri kamar yadda ta fada tunda sallamamiya ce gwara kawai ya bada jininta.

Saman ya koma Yana tura k'ofar sukayi kicibis a bakin kofa ta rungume zaninta a hammatar ta.

Kabiru ya saki murmushi Yana "Hajiya Abu wanan runguma da kikayi wa zani haka har nawa Kika dauka Haka"

Yaya Abu hade rai tayi ta sake Kankame zanin a jikinta tana " ka bani hanya na wuce dan bazan kwana a gidanan ba"

"Nima mukulli zan dauka na fita sai na rage Miki hanya

"Ba sai ka rage min hanya ba cuta ce ka riga da ka cutar dani"

Kabiru hanya ya baya ta fita daga d'akin da sauri,tana murna da bai karbe zanin ya duba kudin da ta kusan kwashe masa gabad'aya da tabbas kudin haram ne na jini,amma haka za tayi amfani dashi,d'akinta ta shige ta saka doguwar riga ya dan Debi Kaya kala biyu da duk a gidan Kabiru ta siye su,kaikaiyin da taji da danshin da taji a bayanta yasa ta shige bandaki ta hau wanke jikinta tana tsinewa Kabiru.

Tana tsoron ta koma kamar Sajeeda babban burinta yanzu gari ya waye ta Kai kanta asibtin kudi,ta wangale musu su wanke Mata koina ta basu kudin.

K'ofar da Kabiru ya turo yasa ta tsaya tana kallon shi ji take kamar taje ta rufe shi da duka.

Kabiru kuwa yace mata zai fita Kuma kulle gidan zaiyi tazo suje ya sauketa a hanya ko hotel ne ta kwana.

Yaya Abu Jakarta ta dauka tana zabga Mai harara,ta tusa daya hannnun nata a zaninta tana susa,dan.kaikai Kamar ta cire zanin ta ta Yar.

Ahaka tabi bayansa ta Shiga motarsa yaja Suka tafi.

Suna zuwa titi tace "Ka saukeni anan"

Kabiru ko kallonta baiyi ba ya kulle k'ofar motar ya cigaba da tafiya

Yaya Abu kuwa cikin masifa ta hau magana "baka ji Mai nace bane ka saukeni dalla ko baka jine"?

"Hakuri zakiyi zan saukeki ni bansan Mai yasa kike Jin haushina ba,zan karbi kudi a wajen wani abokina Naga kin kwashe min kusan Rabin kudin nawa,idan na karba sai na Kara Miki sai na saukeki tunda kin dage"

"Dole ai ka Kara min tunda kasan ka cuceni"

Daga haka taja tsaki tana murnar yadda tayi kudi lokaci guda  bata damu da kudin haram bane,tunda baa rubuta a jikin kudin ba,so take ta fara samawa kanta lafiya kafin ta san Mai za tayi da kudin, tana da yaqinin zata warke tunda zata Kai kanta asibiti da wuri.

Kalle kalle take har Suka iso.

Kabiru ya Shiga ciki Yana ta jira shi a mota yanzu zai fito.

Da ido ta bishi har ya shige haka kawai taji gabanta ya yanke ya Fadi,ba dai kabiru kawota yayi ya yankata ba,sai a lokacin hankalin ta ya dawo jikinta dan kudin da ta gani ya rudata.

Tuni taji hankalinta yayi mugun tashi dan sai a yanzu ta tuna ai Kamar bayan gari ya kawota Kuma gidan Kamar shi kadai ne ba wasu gidajen.

Hankali a tashe ta hau k'ok'arin bud'e motar,a daidai lokacin da ta ga wasu sanye da Jan zani a kugu su biyu sun nufo wajen motar take,gefensu Kuma Kabiru ne ihu ta fara zunduma tana azo a taimaka Mata,a daidai lokacin da suka iso Kabiru ya bud'e motar masu sanye da Jan zanin Suka jawota suka daga ta sama,ta fara ihun "Kabiru mai nayi maka kake so ka kasheni innalillahi wa Inna ilaihi rajiun ku saukeni Kabiru idan dan ka bani kudinka kake so ka kasheni dan girman Allah ka dauki kudinka bana so Kabiru nice fa Abu mai na maka da zafi haka kake so ka kasheni?

Ihu kawai take har suka direta a wani daki suka fita Suka barta,ihuu kawai take tana "Baba kana Ina Gwaggo ku yafe min tun baaje koina ba na fara ganin ba daidai ba,Kabiru na tuba ka bar kudin dan girman Allah ka maidani titi,wallahi ba Wanda Zan fadawa karka min haka Kabiru?

Shigowar shugaba da bakakken Kaya da wani Kare daya dallaro harshensa waje yasa ta saki ihu taje ta manne da bango, Kabiru kuwa dake bakin kofa ya fara magana Yana "Mai gida burina sirrina ya rufu a rufewa kowa baki"

Shugaba murmushi ya saki Yana "zaka iya tafiya ka dau hanya goben nan karka wuce gobe karfe daya zamu yi amfani da jinin ko ka isa can ba mai iya maka magana "

Ihu Yaya Abu ta saka tana "ku rufa min asiri da jinina zaku yi amfani innalillahi wa Inna ilaihi

rajiun kuyi min rai karku kasheni, Kabiru nice fa Abu yayar Sajeeda Mai na maka da kazo ka bada jinina mai yasa baka bada na Sajeeda ba"

Kabiru ko kallonta baiyi ba yayi waje shugaba ya fita ya rufe k'ofar

Ta tafi da gudu tana bubuga k'ofar kuka kawai take kamar ranta zai fita "kaicona na cuci kaina a garin san kudi,na jawowa kaina mutuwa wane kaddarar ne ya kaini gidan Kabiru shikenan yanzu mutuwa zanyi"

Kuka kawai take tana hararo yadda zasu yankata.

Kabiru

Ko kad'an baiji komai ba har ya baro kungiyar dan yasan ba mai tab'a zargin Wai shi ya d'auke Abu,haka kawai yaji yayi mugun tsanarta,ko shi aka bawa wukar zai iya kasheta,babban burinsa a yanzu ya samu Yesmeen ko da a gaban mutane ne wallahi sai ya rabata da ranta,a rayuwarsa bashida babbar makiya sama da Yesmeen duk wanan masifar ita ta jawo.masa.

Koda ya koma gida haka ya zauna yayi zuru Yana tunanin Rabiuu har ga Allah so yake ya bar kungiyar ya gaji yayi nadama,har tsawon wane lokaci zai dauka Yana aikata abubuwa dan asirinsa ya rufu da Yama riga da ya tonu,yanzu gobe idan mahaifiyarsa ta Kama shi fa Mai zai ce Mata.

Idan yaje gobe Yan uwa Sajeeda suka gan shi fa

Yadda yaga rana haka.yaga dare bai runtsa ba.

Karfe bakwai na safe ya dau hanyar garinsu da Kare a Bayan mota baisan ma mai zai cewa mahaifiyar sa akan Karen ba.

Zuciyarsa cike take da zullumi.

Tafiyar awani ya karaso dashi har k'ofar gidan mahaifiyar sa da ta koma sabon gidan da ya Gina mata.

Da Karen ya shiga cikin gidan

Gabansa na dukan uku uku,a tsakar gidan ya samu mahaifiyar sa a tsaye wasu almajirai a tsugunne a gabanta,tana ganinsa ta saki baki tana kallonsa da Karen da yake ja da daya hannunsa tama kasa amsa sallamar da yayi Mata.

"Wanan Karen fa Kabiru daga Ina haka ka taho da kare"

Mahaifiyar sa tace a daidai lokacin da ya Isa gabanta ya tsugunna Yana gaisheta

Bata amsa ba ta Kara jefa Masa tambayar "Wanan karen fa Kabiru kasan ko kad'an bana San Kare Mai ya hadaka da kare Kai ba mafarauci ba"

"Hajiya akan hanyar tahowa nan na siya wallahi barayi ne suka addabeni shi yasa idan na kaita gida barayi zasuji tsoron shigowa.

"Tun kana Abujan baka tsaya ka siyi Karen ka Kai gida ba sai da ka d'auko hanya zaka siya"

Kabiru Kai ya hau sosawa ya dauki Karen yayi bayan gidan Yana "yunwa nake ji hajiya akwai abinci.

Yana zuwa ya daure Karen ta wuyansa

Ya koma ciki,Yana shiga yaga mahaifiyar sa ta kwanta kamar Mara lafiya

Cikin mamaki yace "Hajiya lafiya kuwa na ganki haka"?

"Wallahi Yanzu nan naji kaina ya sara min zazzabi ya rufeni ji nake wuyana a shashake ma"

"Sannu hajiya Allah ya sauwake ya baki lafiya kina da pcm na dauko miki ki Sha"?

Eee akwai a gaban mudubi d'auko min,sai ka Shiga kitchen akwai abinci a flask.

Kabiru dakinta ya Shiga ya d'auko Mata pcm din da ruwa ya kawota dak'yar ta karba ta Sha tana rik'e wuyanta.

Kabiru ya shiga kitchen ya debo abinci ya dawo palon ya zauna ya fara cin abincin ganin tana ta wash wash yasa yace "Hajiya ko dai asibiti Zan Kai ki"?

Girgiza Masa Kai tayi idonta a rufe,a haka ya zuba mata ido Yana jera mata sannu.

Ba jimawa yaga bacci yayi awon gaba da ita.

Sai yaji inama a yanzu zai iya zagayawa baya ya nemi karyar tunda bacci ya d'auke ta,amma

ba wanan damar saboda sai karfe daya na dare aka ce ya kwanta da Karen,kila yanzu ma ya gama da jinin Yaya Abu ya tabe baki Yana kwadayin ta ne ya jawo Mata.

Bacci bacci yaji ya fara ji shi ma hakane yasa ya tashi ya Shiga daya d'akin da ya zama d'akin Baki.

Yana kwanciya bacci yayi awon gaba da dashi.

Mafarki

A kwancen da yake yaji an turo k'ofar hakane yasa ya bude idonsa a hankali yaga mahaifiyar sa ta shigo da igiya a daure a wuyanta cikin b'acin rai ta fara magana tana "Kabiru mai nayi maka kake so ka kasheni saboda me zaka daureni, Kabiru ka kunceni Kabiru ka kunceni Kabiru ka kunceni"

A firgice ya tashi ya hau kalle kalle sai da ya dau tsawon mintuna ya gane mafarki yake,mik'ewa yayi da sauri yayi waje dan sai yake ganin kamar ba mafarki yake ba a gaske ne mahaifiyar sa ta shigo.

A kwance take har lokacin akan dogon kujera,ido ya zuba mata yana tuno mafarkin da yayi da ita Mai ke Shirin faruwa ne Mai yasa zaiyi mafarki da mahaifiyar sa tana a kunceta

A hankali ya fita waje,ya zagaya bayan gida Inda ya daure Karen

Yana zuwa yaga Karen a kwance Kamar yadda mahaifiyar sa ke kwance,gabansa yanke wa yayi ya Fadi ya hau tuna Sajeeda da yadda yayi amfani da Kare a madadinta.

Cikin faduwar gaba ya karasa wajen Karen Yana zuwa ya tsugunna a gaban Karen ya kunce daurin wuyansa.

Ya mik'e ya koma ciki ga mamakinsa Yana komawa ciki yaga mahaifiyar sa ta mike tana tattaba wuyanta tana ganin shi ta fara magana tana "Kasan ji nayi Kamar an shake min wuya mai ke Shirin faruwa dani ne"?

Kabiru da jikinsa ya dauki rawa kasa ce Mata komai yayi mahaifiyar sa kuwa ta mik'e tana kila iska ne bata ga ta zama ba bari ta d'auko Qur'anin ta daga haka tayi d'akinta.

Kabiru yayi waje da balain sauri hankalinsa a balain tashe sai a yanzu ya gano shugaba so yayi ya cuce shi ya yaudare shi ya nemi mahaifiyar sa, taya zai cutar da mahaifiyarsa?taya zai nemi mahaifiyar sa jikinsa rawa kawai yake ya d'auko wayarsa a daidai lokacin da Kiran shugaban ya shigo wayarsa.

Rai a balain bace ya daga wayar Yana k'ok'arin magana shugaban yace "Matar da ka kawo jiya ta gudu,bansan ya akayi ta tsere ba dan haka ka kawo mana wani Jinin"

"Bazan kawo ba ka kasheni kawai dan Nagaji da wanan masifa ba abinda kasani,tunda har ka bari Abu ta tsere nasan asirina ya gama tonuwa,har ni zaka yaudara kace na kwanta
Da mahaifiyata a siffar Kare,Allah ya tona maka asiri wallahi wallahi bazan kwanta da Karen ba na gaji ba abinda zaka iya yi na bar kungiyar na daina yi kayi duk abinda zaka yi"

"Nan da awa ashrin zamuyi amfani da jininka"

"Kayi amfani dashi a yanzu dan na gaji da na kwanta da mahaifiyata gwara ka kasheni mugu azzalumi Kun cuceni Allah ya Isa ban yafe maka ba"

Kiit yaji ya yanke wayar.

Yana k'ok'arin sake Kira yaji muryar mahaifiyarsa a Bayan sa da.....

ALBISHIRINKU 🥳🥳 ALBISHIRINKU 🥳🥳🥳🥳 MANYAN MATA
Takunce dai A&Z COLLECTION takara zuwa muku da kayanta masu sauki da inganganci👌👌

Muna da supplement nau,i kala kala

Sannan akwai sabulu Mai suna HALFCAST SOAP hmmm hajiyata duk yadda za,ai karki Bari abaki labarinshi Dan sabulune dayake aiki cikin kwana uku kacal 👌zakiga yadda kalarki zata koma kiyi haske me kyau bana bleeching ba haka Zaki dinga sheki kina haskawa acikin jama,a 🔥🔥🔥
Koda kindaina amfani dashi ba,abunda fuskarki zatai saboda natural ne Wanda sukai bleeching yabata musu jiki dafuska Kuma kunemeshi Yana dawo dakalar fata baidaya bacan Baki nan fariba 😄
Akwai cream gamasu San suhada set Wai ai hajiyata saikin zama taurariya acikin taurari mudin kika mallakeshi💃💃💃
Kira ko WhatsApp 09037870422

Karku manta muna da supplement kala kala

Na matsi
Na gyaran breast
Na hips
Na slimming
Na fari
Na gashi

Dasauransu

Haka zalika muna :

HADIN MAI  JEGO
HADIN UWARGIDA
HADIN AMARYA

Kuma duka afarashi me rahusa kedai kawai kituntubeni 👇👇
09037870422

Muna garin kano muna tura Kaya ko,Ina cikin aminci 🤝

Sai Allah yakawoku

*WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE 91-95*

"Zanje wajen Mallam na dawo ya nagan ka haka a firgice lafiya kuwa"?

Kabiru da numfashinsa ya kusa d'aukewa saboda tashin hankali dan ya d'auka taji  wayar da yake ajiyar zuciya ya saki a hankali ya fara share zufar da ke keto masa Yana "Ba komai hajiya"

Ido mahaifiyar tasa ta zuba Masa tana karantar sa,har ga Allah ta kasa gane Kan Kabiru,tana yawan munanan mafarki a kansa,bata San dalili ba,gani take Yana cikin damuwa amma bayaso ya fada mata.

"Sai kin dawo Hajiya"

Kabiru yace da sauri Yana nufar cikin gidan dan kiran shugaban ne ya Kara shigowa wayarsa gabad'aya hankalinsa a tashe yake.

Yana shiga ciki ya dauki wayar kirjinsa na bugun uku uku, shugaban ya fara magana da "ka bijire wa kungiya duk abinda akace kayi baka yi ba, karka manta idan aka Shiga kungiya baa fita,amma tunda taurin kai zaka gwada mana, bazamu kasheka ba zamu bar ka a raye yadda zaka ringa neman mutuwa da kanka ka gaggauta bawa kungiya hakuri,ka aiwatar da abinda Muka saka ka,idan ba haka ba zakayi mamakin abinda zai biyo baya"

"So nake kuyi duk abinda zaku yi dan na rantse da Allah na bar kungiyar kenan har abada ko da Wasa bazaka Kara ganina ba,ka fadamin ribar mai naci a Shiga kungiyar idan ba lodin tashin hankalin da kuka ringa jefani ba,kuka saka na Kauce hanya na daina ibada duk wani nauin manyan zunubi ba wanda ban aikata ba Kun cuceni Allah ya Isa ban yafe ba kuyi duk abinda zaku yi dan bazan Kara yarda ku jefani a cikin wani tashin hankalin bayan Wanda nake ciki ba"

"Zaka gani"

Shugaban yace tare da kashe wayar

Kabiru kuwa yayi wurgi da wayar hannunsa Yana Jin kansa kamar ya rabe biyu,

Ya kwanta flat a kasa ya fashe da kuka Yana "kaicona ya Allah ka yafe min nayi nadamar abinda na aikata"

Kuka yake Kamar ransa zai fita yayi nadamar jefa kansa a  cikin masifa da balai,baisan Mai ya Kai shi Shiga kungiya ba,bai rasa ci ba bai rasa Sha ba, matarsa bata tab'a nuna gajiyawarta a hidima da gidan ba,hasali ma bata bari ma ya nuna damuwar rashin kudinsa,tunda ya Aureta har Suka hayayyafa ta bawa yaransa tarbiyya daidai gwargwado,amma saboda idon sa ya rufe da san yayi kudi ya fara ganin bai dace ace Sajeeda ke hidima da gidan ba,yaransa zasu iya Raina shi dan zai iya cewa sun ma raina shi dan ba Mai cewa ya mishi Abu da sun tashi wajen Sajeeda suke tafiya suce Abba ba shi da kudi, tun ranar da Yana daki a kwance dan ko ya fita ba abinda zai samo tunda ba Wanda yace yazo ya masa gyara,yaci abincin Rana kenan da Yana ci Sajeeda na gefensa tana jansa da hira ko kad'an bataso tagan shi cikin damuwa,sai da ya gama ci ta dauki kwanun tayi waje tana ya kwanta ya huta,Yana kwanciya ya jiyo muryar Hamza yana ta  siya masa littafi budar bakin Annur sai cewa yayi kaje ka fadawa Abba ya siya maka,sai Hamza yace ai Abba bashida kudi shi yasa nace umma ta siyamin.

Runtse idon sa yayi dan har ga Allah ransa ya sosu,yanzu haka zai zauna komai sai dai Sajeeda tayi,haka zai zauna yaransa na Masa kallon fakiri a ranar ko runtsawa baiyi ba ya hau tunanin ta hanyar da zai samu kudi ta k'arfi da yaji,dole ya nemi kudi,ko dan ya dawo mai gidan.

Tunda ya dasa tunanin samun kudi a ransa ya fara tunanin ko fashi da makami zai fara Yana so

yayi kudi idan ya shigo gidan yaransa su zagaye shi kowane na fada Masa matsalarsa.a cikin wanan halin watarana yana cikin tafiya yaji ana ta masa horn Yana juyawa yaga tsohon abokinsa ne Rabiu da suka yi makaranta tare.

Jiki na rawa ya Shiga motarsa Yana mamakin yadda Rabiu ya Zama Mai kudi,dan kayan jikinsa da motar sa kawai ya nuna kudi sun zauna,a ranar Rabiu ya danka Masa kyautar dubu dari,ya bashi lambar wayarsa,akan ya kirashi,yayi nadamar haduwa da Rabiu,dan daga kiransa akan ya Masa hanya yayi kudi,ya dorasa akan mumunan hanya Wanda da fari sai da ya bijire yace bazai iya ba, Rabiu ya hau wanke shi da kudade da har sai da ya kwadaita masa yaji zai iya komai dan ya samu kudin,yau ribar mai yaci a Shiga kungiyar matarsa Mai kaunarsa mai rufa Masa asiri,ya butulce mata yayi amfani da ita ya kassara mata rayuwa,tunda yake bai tab'a aikata zina ba sai gashi da girmansa da yayansa ya hau neman Mata,ya kwanta da Kare yaje makabarta yasa layya a bakin gawa,ya daina sallah gabadaya duk a Kan kudin da zai iya mutuwa ya bari Kamar yadda Rabiu ya tafi cikin kiftawar Ido,Allah  ya dauki ransa,mai ya Kai shi jefa kansa a cikin wanan masifa yanzu ya ma Zama kafiri tunda baya sallah,taya zai nemi yafiyar Allah daga Ina zai fara.

Kuka kawai yake har Yana Jin zazzabi na neman rufe shi.

A haka mahaifiyarsa ta shigo ta sameshi.

Hankali a tashe tayi kansa tana "Kabiru Wai Mai yake damunka Mai kake boye min Kabiru yanzu da na fita akace Sajeeda ta dawo gida ni bangane mai ke faruwa ba, Kabiru kana da sama dani ne Mai ke faruwa ne ka fadamin ni mahaifiyar ka ce zan iya maka addua ko na taimaka ma da shawara"

Kabiru kuka kawai yake dan bazai tab'a iya bude baki ya fada mata abinda ke faruwa ba,ya faro kuruciyarsa da kyau,tsakiyar rayuwarsa da kyau wai sai da yaje matakin karshe ya kauce ha ya saboda san zuciya da san abun duniya ko da asirinsa bai  taba tonuwa ba ace duk abinda yake so Yana samu dole watarana ya mutu ya bar duk abinda ya tara dan baza'a bine shi da komai ba sai kyawawan ayyukan sa.

Mahaifiyar sa kuka ta saka masa tana ya fada mata damuwarsa dan bata san Mai yasa gabanta ke faduwa Kamar akwai abinda zai same shi ba ya fada Mata koma menene ita mai rufa masa asirine"

Kabiru da ya fara Jin Kamar ana cire Masa Abu a jikinsa ya bud'e bakinsa dak'yar Yana "Kiyimin addua kawai Hajiya adduar ki nake bukata"

Hajiya na k'ok'arin magana sai ga wasu sun shigo aguje suna motarsa ta Kama da wuta.

Hajiya ta mike hankali a tashe Kabiru kuwa ya rufe idonsa dan yasan duk sai sun karbe abinda

Suka bashi.

Kiran da ya shigo wayarsa yasa ya dauka makocinsa ne yace gidansa ya Kama da wuta.

Bai ce komai ba ya kashe wayar.

Tuna gidan da ya ginawa mahaifiyar sa ma da kudin kungiya ne yasa ya mik'e a zabure Yana "Hajiya mu bar gidanan yanzu Nan kizo mu fita karki d'auki komai"

Hajiyarsa na k'ok'arin magana yaja hannunta da sauri suka fita.

Suna fita gidan ya Kama da wuta kamar an jefa bomb

Hajiyarsa ta fara ihun sallati tana neman fita a hayyacinta.

Kabiru kuwa ya hau Jan hannunta dan mutane sun fara k'ok'arin kawo agaji Wai zasu kashe motar dake taci da wuta da gidan.

A takaice Kabiru tsohon gidan da mahaifinsa ya gina Suka koma gabad'aya ji yake kamar ya yanke Jiki ya Fadi,mahaifiyarsa kuwa sai tambayarsa take akan ya fada mata mai ke faruwa.

Amma Kabiru yaki magana Dan yanzu yasan zasu iya kashe shi a kowane lokaci so yake ya nemi Sajeeda ya nemi yafiyarta so yake ya sake saka yaransa a idonsa amma ji yake bazai iya ba dan jikinsa ba kwari haka ya kwanta idonsa a rufe Yana Jin zuciyarsa kamar ana hura masa wuta saboda zafi,a karshe dai yasan kashe shi  zasuyi Mai zai cewa Allah,yasan tun a kabarinsa zai fara girbar abinda ya shuka.

Mahaifiyarsa haka ta saka shi agaba sai kuka take,duk abincin da ta kawo masa baici ba Yana kwance idonsa a rufe kwmar matace ya kira Saifullahi Yana Jin muryar sa ya kashe waayar duk yaran ba Wanda bai Kira ba amma ba Wanda ya d'auki wayarsa,ya Kira lambar Sajeeda a kashe,Ina ma da yadda zasu yafe masa.

A Haka mahaifiyar sa ta kwanta a gefensa tun tana zaune har sai da ta kwanta bacci yayi awon gaba da ita.

Wajen karfe uku yaji wani irin iska ya shigo d'akin kafin ya gane Mai ke faruwa sai yaji ana ta Kiran sunan sa Kamar daga nesa,kamar Wanda ake  bawa umarni ya mike Yana jin jikinsa na d'aukar wani irin zafi,gabansa ya mik'e Yana harbawa.

Waje ya fita yana jin magana a kunensa,kamar zai haukace ya hau fara gurnani shi kadai Yana dube dube,nesa da gidan ya hango wani katon karya bai yi wata wata ba yayi Kan Karyar,Yana zuwa ya damketa Karyar na cizonsa jikins na jini,haka ya hau saduwa da karyar,Yana

gurnani,Yana Jin jikinsa na d'aukar wani irin zafi.

Ji yake jikinsa Kamar ya Kama da wuta a jikin karyar ya fara k'ok'arin zare jikinsa daga jikin karyar da ta daina motsi,sai yaji Kamar an like jikinsa da Gam,ya kasa zarewa,idan yaja da k'arfi sai yaji Kamar numfashinsa ake zarewa, tuni ya fara ihu,a wanan halin aka fara kiraye kirayen sallah asuba.

Mutane suka fara fitowa dan su tafi massallaci,Suka ga Kabiru a durkushe jikinsa a jikin karya,sai gurnani yake Yana ihu Kamar ta karyar.

Tuni wasu Suka kasa zuwa massallacin Suka zagaye shi suna sallati,kad'an daga ciki Suka gano ai Kabiru ne, sallatin da ake ta zubawa yasa mahaifiyar sa fitowa da gudu,tana zuwa taga halin da Kabiru ke ciki ta yanke Jiki ta fadi,tuni mutane Suka taru suna kallon Kabiru dake Haushin Kare da Kuma alama jikinsa ya manne da na Karyar da bata motsi,abinka da karamin gari,tuni labari ya Kai ko Ina,a wayanda suka zo ganinsa har da mahaifin Sajeeda da hankalinsa ya yi matukar tashi,dak'yar ya koma gida dan tunda yake bai tab'a ganin abinda ya girgiza shi haka ba.

Sai manya a cikin garin ne Suka d'auke Kabiru da karyar dan har yara sun fara jifansa.

A takaice sai da mallamai Suka zo da karfin Addu'a aka iya raba Kabiru da jikin karyar, Kabiru kuwa sai haushin kare yake,jikinsa ya fara komawa na Karyar,sai susa yake Yana ihu,yana k'ok'arin cizge gabansa dake ta jini, tuni aka yanke a daure shi dan jiwa kansa ciwo yake,sai dai suna k'ok'arin Kama shi ya ture su ya diba a guje a tsirara Yana Haushin Kare.

Allah ya tsare Mana imaninmu ya hanemu da kauce hanya alfarmar Annabi Muhammad sallalahu alaihi wa salam.

Mahaifiyarsa kuwa jininta wani irin Hawa yayi Wanda sai da aka kaita asibiti aka bata gado.

Sajeeda...........

2nd to the last page in Sha Allah munzo gangara ko?

*AYYIRIRIRI AHAYYE CHAS 💃💃💃 sunan wata waƙa wai ita LUWAI*
_Ana tayi muna tayi manyan mata dai da gaske sun dage sai sun zama kalar gaban mota kalar camera tare da gudummawar Mg's skin care Hajia ta kina ina ake ta wannan harkar arziƙin mata nata glowing suna faranta zuciyar mazajensu da laushi da santsin fatar su ke kina nan kina fama jiki duk kirci😱😱?_
Ah haba madam yunƙuro ayi tafiyar nan dake ki shiga ki wataya acikin shahararrun matan

nan da ko'ina ake fatan gani  dan an daɗe ana jin su watau *team glow by Mg's*
Macen da ta isa itace mace karki bari ki zama cikin irin muna matan nan da suka rako mata duniya kuna tafe da mijinki yana kallon wata har miyau na zuba tsabar haɗuwarta da kyan fatarta
Mg's skin care sune sirrin duk wata macen da ta isa a ɗaga kai a kira da suna mace wacce ba'a jin kunyar shiga taro da ita daga nan har villah kizo/kuzo mu haɗe a wannan ƙasaitacciyar tafiyar ta Mg's skin care domin sune na gaban gaba sune suka ciri tuta indai a harkar gyaran skin ce hajiata kiyi wani fresh  kiyi smooth wow🥰🥰🥰kina tafe kina walwali idan fa kina amfani da *Mg's skin care* ba kya buƙatar ko wanne irin mai product ɗinmu katt ne duk matsalar fatarki muna da maganinta uhmm inata miki labari  nace  ba sister shin  meye matsalarki ta gaban goshin ƴallaɓai?
Acne?, pimples? spot?, strech marks?, sunburn?.
to hutas bi'izinilLah muna da maganin matsalarki kina ganin mata a tiktok fuska luwai lumus kice dama ni ko? to in dai kina tare da *Mg's* matsalarki tazo ƙarshe  bama cika baki gaskiya itace takenmu haka nan kuma siyen nagari mai da kuɗi gida *MG's skin care gagarabadau*
Price ɗinmu daidaitacce ne  sannan kuma dai dai da aljihunku

*Soap price:4k*
maiso yy mgn
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391
Instagram:glow_with_mgs
Facebook: mg's skincare

Masu bukatar cream Shima munadashi harda ma complete set nagyaranjiki
Small 14k
Babba 16k

Munatura Kaya kowani gari dayardar Allah Amma delivery is not free
Sanan Kuma akwai kit
Karami 12k Abubuwa  6 ne aciki😱😱😱 wannan garaɓasa har ina?
Soap
Body cream
Face cream
Scrub
Cleanser
Oil
*BE PART OF THE GLOW TEAM KARKU BARI A BAKU LABARI

**WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE 96-*

Sajeeda

Nayi kuka Kamar raina zai fita a lokacin da labari ya iskemu akan halin da Kabiru ke ciki,na kasa yarda wai uban yayana ne ya haukace yake Haushin kare

Babana ma kuwa har da zazzabin sa dan da alama abinda ya gani ya tayar Mai da hankali,jikinsa sai rawa yake Yana zuba sallati,yana "Akan neman duniya akan kudi Kabiru ya cutar da kansa haka"??

Yarana kuwa daki suke shige suna ta rizgar kuka,Hamza da Annur da suke je Suka ganewa idonsu halin da yake ciki akan bola,dak'yar aka dawo dasu suma suna ta kuka, tuni aka cika gidanmu  wanda rabinsu  gulma ne ya  kawo su,daga ni har yarana  haka muka kulle  kanmu a daki, a ranar sai da jinina ya hau,dan sai da aka Kai ga Kaini asibiti shekara ashirn da hudu ba wasa ba hankalina ya tashi da halin da Kabiru ke ciki, bansan Mai ya kawo shi garin nan ba,bansan ya akayi asirinsa ya tonu a bainar jamaa a garin da aka haife shi kowa ya san shi ba.

Nusrah ma sai da aka bata gado wai ana ta kiranta a waya wai an samu wasu sun masa video sun yada a duniya a tsirara yana Haushin Kare,da zuciya na bugawa da na nida yarana ya buga,wai bamu muka aikata ba Amma muke Jin wanan kunyar,wai iya kunyar duniya kenan Ina ga anje lahira,da zaka tsaya agaban Allah,mai yasa Kabiru yazo garin nan yazo ya tona min asiri,dan tamkar ni ya tonawa asiri tunda ya shafa min bakin fenti da yarana.

Daidai su Saifullahi haka suka ringa Kira a waya,bazan iya jure wanan tashin hankali da abin kunyar da Kabiru ya jawo mana akan neman duniya ba,hakan ne yasa na nemi iznin mahaifina akan zan koma garin kano nida yarana dan mutane da gangan suke zuwa su zauna a gidan suna so sugani ko suga yarana,ni kaina abin kallo na zame musu,yaya Asmau ce ta ringa tausa ta,ba abinda ya rage kowa yasan halin da muke ciki, mahaifina Kuma yace nayi zamana anan din bai yarda naje ko'ina ba,tuni na mika lamarina wajen Allah,duk da ba wai gama warkewa nayi ba,haka na daure na ringa kwantarwa da yarana hankali,dan a karshe unguwar muka bari muka koma wani unguwar wajen dangin mahaifina,Nusrah tayi wani irin rama gata da danyen

jego a jiki,tashin hankalinta nasan bai Wuce mijinta da bai tab'a kiranta a waya tunda tazo garin ba idan itace ta kirashi kuwa baya dauka,tun tana boye min sai da na gano,na hau kwantar mata da hankali wanan Yana cikin kaddararmu bamu isa mu kauce masa ba,nasan abinda Kabiru ya aikata sai yayi balain shafar yarana,kila Mijin Nusrah sai ya rabu da ita,tunda bazai kasa samun labari ba tunda har a gidan radio an bada labarin Wanda jikinsa ya makale a jikin Kare yake Kuma kukan karen,dan a yadda naji har daga wani wajen ake zuwa ganinsa, gashi an kasa Kama shi balle a killace shi,mahaifina balain tausayin shi yake ji,kamar yadda nima naji Ina tausayinsa,a da na dauka bazan tab'a iya yafe Masa ba,a da na dauka da zan ga abinda zai cutar dashi kau da kaina zanyi sai gashi na tsinci Kaina da tausayin halin da yake ciki,Wanda ni nasan Allah ne ya tona Masa asiri,da asirin nasa ma ya tashi tonuwa sai ya tonu a bainar jamaa,duk wanan masifar da ya jefa kansa akan neman duniya ne,ga Inda Neman duniyar yayi dashi,mun gina rayuwar mu cikin kwanciya hankali da soyayya san zuciyarsa ya Kai shi neman kudin haram ya jefa kansa a masifa ya saka mu a tashin hankali duk abinan ko shekara uku baiyi ba.

kwana biyu da komawar mu gidan kanin mahaifina Saifullahi da Fahad suka zo daddare,rabona dasu shekara daya kenan da watani,yarana sun zama Samari sosai,haka muka rungume juna muna kuka.

Sai tambayoyi suke min da banida amsar tambayar su,akan abinda ya samu Kabiru har ya haukace,a takaice a daren Suka bi dare da rakiyar su Annur Suka gano Kabiru da ke saman bola Yana tsince tsince,sai da suka dawo cikin kuka Suka hau bani labarin yadda jikinsa ya koma kamar na Karen, fuskarsa ce kawai bata canza ba,wai Yana ganinsu ya daina haushi ya zubo musu Ido yana kallon su.

A ranar dagani har yarana sai da muka ci kuka muka gode Allah.

Annur sai cewa yake a dauko shi a Kai shi asibiti yarana ma balain tausayin shi suke, Saifullahi sai cewa suke Ina ma ace sun gano da kila basu bari yayi nisa ba,anan suke bani labarin yadda komai nasu ya kone,har da na Yaran abokin Kabiru Rabiu sai a wajensu nake Jin wai ya rasu,yayansa kamar su haukace da suka ji rasuwarsa,Suma sun gano kudin nasa bana halal bane.

Saifullahi cikin kuka ya ringa bani labarin yadda ya ringa kawo zargin mahaifunsu daga baya sai ya watsar dan gani yake bazai taba kauce hanya dan ya samu kudi ba.

A takaice Saifullahi shi ya nemo Mana gida a Kano ya roki mahaifina akan Yana so mu koma can,dan idan muka bar garin zamu dan samu nutsuwa,idan an kwana biyu zai san yadda zai yi yasa azo a dauki Kabiru,dan yana da kudin da ake biyansa na zanne da yake tarawa, dan kaf makarantar su ba Wanda ya Kai shi iya zanne wanda har masu kudi nemansa suke dan ya musu zannen da ya ringa shigo Masa da kudi.

Mahaifina albarka ya sawa Saifullahi dan da Kabiru baiyi gaggawa ba da ya samu kudin ta

hanyar Saifullahi dan da dukan alamu Saifullahi shi zai zama silar da zasu yi kudin.

Yaya Abu

Tunda Kabiru ya fita ya barta a d'akin da aka kaita ta ringa rusa ihu,tana nadamar biyo kabirun da tayi,sai a yanzu ta fara nadamar zuwa ma gidansa,yau gashi garin kwadayin ta bayan nemanta da yayi ta gaba da baya,da a yanzu ruwa zubo mata kawai yake Yana bin kafarta mai balain wari,duk haka bai ishe sa ba sai ya kawo ta an yankata,sai a yanzu take nadamar duk Abubuwan da ta aikata,kila hakkin Sajeeda ne ma ya Kamata,kila muguntar da tayi ne duk yake dawo mata, Ina ma tana da yadda zata tsira da ranta wani irin sanyi take ji dan zazzabi ne ya rufeta tana Jin kamar karfin Jikinta na raguwa,kaikaiyi da zugi kawai take ji tun tana iya kuka da k'arfi har sai da ta koma kukan zuci,shigowar shugaban a tsirara da wani tukunyar kasa dake ci da wuta yasa ta mik'ewa a zabure tana ya mata rai,Kar ya kasheta,bai ko saurareta ba ya ajiye tukunyar kasar,ya Ciro wani abu.kamar fifiken kaza daga tukunyar kasar ya nufo wajen da ta manne da bango ya hau shafa goshinta Yana gwarancin da bata gane ba, ihu kawai take tana sallati,idan tayi sallati sai ya buge bakinta,a haka ya Kara ficewa daga d'akin,Yaya Abu kuwa ta zub'e a kasa ta hau Kiran sunayen Allah dan da iliminta sarai,kawai shagala yasa bata wani maida hankali,zata so ta nemi yafiyar Iyayenta kafin ta mutu,zata so taga Sajeeda ta nemi yafiyar ta zata so taga Yarta kafin ta mutu, tun tana iya Addu'a da k'arfi har sai da taji numfashinta na neman d'aukewa.

Haka ta kwanta tana Jin azabar radadi a jikinta,ga zazzabi mai zafi,da ace bata biyo Kabiru ba da kila ta samu ta tsira Koda babu kudin.

Tana nan a kwance taga shugaban ya dawo da wasu maza uku da ido ta ringa binsu dan bata da karfin motsawa sai hawaye dake zubo Mata,umarni ya bawa daya daga cikinsu akan ya dagata ayi mata aski a fita da ita dan karfe biyar zai yanka ta.

Mik'ewa tayi cikin tashin hankali da taji yankata zaiyi tuni ta nemi rashin lafiya da take ciki ta rasa ta hau ihu tana Kiran sunayen Allah akan yazo ya taimaka mata,tana ji tana gani suka ririketa Suka Mata kwal kwabo,suka daga ta sama suka fita da ita waje bayan sun bade kanta da wani abu da take tunanin Hoda ne.

Kashi da fitsari haka ta ringa saki saboda akwai tashin hankali Wai kaga mutuwa da idonka,wayanda zasu kashekan ma basu San Allah ba balle suyi imani, a wani karamin daki suka ajiyeta dake d'auke da kwarangwal din kawunan mutane,suna ajiyeta suka fice daga d'akin.
Yaya Abu da take Jin Kamar ta mutu ma tun kafin a kasheta ta fara sallati tana neman hanyar da zata gudu,kamar ance ta kalli bakin k'ofar ta hango abu kamar mukulli jiki na rawa ta karasa bakin kofa tana zuwa ta dauki mukullin Kamar Wasa ta zura a k'ofar taga ya bud'u.

Ta bud'e k'ofar a hankali ta fito, batasan ma wajen da suka ajiyeta ba dan kamar bayan gidan ne, ga karnuka nan sunfi hamsin da aka daure,tuni ta fara neman hanyar da zata bi ta gudu,sai

dai duk Inda taso ta samu hanya bata samu ba,waige waige ta hau yi ta hango wani drum a kife a wajen katangar,da balain sauri ta danne drum din har tana kurjewa a kafa ta daka tsalle ta hau katangar ta dira,tana dira ta sa gudu,duk da batasan Ina ta nufa ba haka ta ringa tikar gudu,kayoyi na soke Mata kafa ko damuwa batayi da ta tsaya ba,sai da ta fara Jin jiri,da rashin k'arfi tun tana daurewa har sai da duhu ya gifta mata ta yanke Jiki ta Fadi .....

Kuyi hakuri,wallahi wayata ta samu matsala sai da ya goge gabadaya wajen tara na sake typin gobe dai zan gama in Sha Allah naso a yau na gama
*WANAN NOVEL DIN NA KUDI NE NA HADA KU DA FIYAYYEN HALLITA ANNABI MUHAMMAD SALLAHU ALAIHI WA SALAM KARKU MIN SHARING NOVEL IDAN BANA KALLON KI ALLAH YANA KALLON KI KUDIN KARATU KIKA BIYA BANA MALLAKA BA IDAN KIKA FITAR NA BAR KI DA ALLAH GA MAI BUKATA SAI TA BIYA 500 ZUWA WANAN ACCT DIN 2029764071 FIRST BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08068484400 SAI A TURO DA SHAIDAR BIYA TA WANAN LAYIN 08033719070 KO WANAN LAYIN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA SU NEMI WANAN LAMBAR +227 96 82 89 84*

*PAGE* *97-100*

Yaya Abu

Bata Kara sanin inda take ba,bata San tsawon lokacin da ta dauka a sume ba,sai muryar mutane taji a kanta,Inda ta bud'e idonta a hankali tana kallon sama sai da ta dau tsawon lokaci ta tuna abinda ya faru da ita,ta fara k'ok'arin mik'ewa zaune dan taga Inda take,sai dai sam jikinta yak'i bata had'in kai,dan ji take jikin nata ya mata wani irin salaf kamar an kwashe komai na jikinta ga Abu da taji Yana zubo mata da ko daga kwancen da take tana shako warin,sai ta hau hararo yadda take kyankyamin Sajeeda take fesa turare idan zata Shiga dakinta,ta hararo yadda take yiwa Sajeeda idan ta b'ata waje,idan ma taimaka mata za tayi haka zata ta mata da mugunta,Ashe itama watarana zata wayi gari ta zama tamkar Sajeedan zata iya cewa ma tafi Sajeedan dan ita kadai tasan mai take ji,bata San Mai ya hau kanta ta bawa Kabiru kanta ba,batasan Ina kunya da tunanin ta ya tafi ta bar Kabiru ya nemeta ba,duk ba wani abu ya jawo mata haka ba sai San kudinta,yau da ace ta ji maganar Nusrah da kila bata tsinci kanta a wanan halin ba, gashi dai tana ganin yadda Kabirun ke wadaka da kudi,amma rufewar da idonta yayi yasa ta kasa yarda kudinsa bana halal bane, rufewar da idonta yayi yasa ta so kashe Sajeeda duk saboda ta samu abin duniyar da yau a garin kwadayinta gata a kwance bama tasan Inda take ba,da yanzu tuni an yanke mata kai,yau da ta samu taci galaba a kashe Sajeeda da ya zata yi Ina zata Kai wanan nauyin,ta tuna yadda Babansu yace Kar ta sake tazo Masa gida,ta tuna yadda tayiwa babba yalwa rashin kunya akan tace tazo su tafi gida bai dace ta zauna a gidan Sajeeda ba,Ina ma lokacin tabi su babba yalwan ta tafi da kila duk bata tsinci kanta a wanan halin ba kuka ta fashe dashi,tana tuno yadda Sajeeda bata iya magana,da

yadda take buga kanta a bango idan tana san tayi magana,yanzu ma batasan Inda take ba,kuka kawai take a daidai lokacin da taga wata mata ta tsaya a kanta tana "Mama kizo kiga ta farka"

Sai a lokacin ta kalli Yar budurwa yarinya da ke sanye da daurin kirji, ta toshe hancinta da hannu biyu ga wani tsagu a fuskarta hausar ma da tayi Kamar ba bahaushiya ba,yadda ta toshe hancinta yasa taji wani irin kuka ya taho mata Ashe haka Sajeeda ke Jin ciwo idan ta toshe hancinta, isowar wata dattijuwar Mata da itama ta toshe hancinta tana gurgurarren hausa da "Ai kuwa ta farka bari babanku ya dawo a gaskiya gwara ya maidata Inda ya d'auko ta dan bazai yu mu zauna da ita tana wanan warin ba,na gaji da kwashe kashin dake zubo mata,ni kamar har tsutsa take fitarwa tunda nake ban taba ganin mai irin lararta ba"

"Wallahi mama warin fa har daki tunda ta farka a tambayeta Ina ne gidansu sai a kaita dan gaskiya da cutarwa zamanta a gidanan.

Yaya abu da ido kawia take binsu hawaye na zubo mata daga maganarsu ta gane tsinto ta mai gidan yayi,so take ta bud'e baki tayi magana amma ta kasa so take tace su taimaka mata su kaita garinsu amma ta kasa magana numfashin da take ma dakyar takeyi,yanzu shikenan bazata iya magana ba,da ido ta ringa bin su tana Jin datijuwar na rokon Yar budurwa akan ta kaita bandaki a dan wanke mata jiki,yarinyar ta hade rai,a haife ma ta haifi yarinya,haka ta figeta ba ko tausayi,ta ajiyeta a bandakin ta debo ruwa ta hau watsa mata daga nesa tana toshe hanci,tuni taji wani irin radadi da azabar kaikaiyi ta fara girgiza Kai tana tuno yadda itama ta tab'a figar Sajeeda tayi mata yadda yar budurwar yarinya nan ta Mata,lailai ta yarda sharri dan aikene,Sajeeda bata da hakkinta gashi tun a gidan duniya an samu mai rama Mata,ta hau gurnani tana "Sajeeda ki yafemin na samu sauki a rayuwata nayi nadamar Abubuwan da na Miki,baba ka yafemin Gwaggo kimin addua kaicona"

Kuka kawai take Yar budurwa na daka mata tsawa tana cudata da tsintsiya daga nesa,dan bazata iya ma matsowa kusa da ita ba.

Koda ta gama wani wajen ta maida ta,ta dauko wani.kaya ta zura mata, duk rai a hade take.masifar babanta ya jawo musu balai ya rasa wa zai kawo gida sai Mai larura,abincin ma a wulakance ta bata tana tura mata cokalin bakinta Kamar zatayi amai,tana gama bata ta bar d'akin a fusace tana bazata yarda ta kwana ba indai kuwa babanta bai maidata ba a yau wallahi guba zata saka mata taci ta mutu.

Wani irin tsoron Allah ne ya shigeta,da taji abinda yarinyar tace,duk wani mugunta da tayiwa Sajeeda yau gashi Yar cikinta na Mata har tana kirarin zata kasheta,Ashe duk abinda take Allah Yana kallonta lokaci ya bata ta gama duk abinda za tayi,Allah kadai yasan irin kararta da Sajeeda ta kaiwa Allah da har ta fara ganin irin wanan sakayya.

Kuka kawai take dan har ta sake Bata kayanta wari ya dume d'akin.

Har ga Allah da ace tasan idan ta mutu Aljanna zata tafi da ta roki Allah akan ya dauki ranta da wanan rayuwar kwanci tayar din,ashe baka yiwa bawa gori da halin da ya Shiga ciki,idan har kayiwa bawa gori da jarrabtar da Allah ya Masa,zaka iya wayar gari kaima a jarrabce ka kamar yadda itama kwadayinta ya kaita ga Shiga halin Sajeedan,kafin ta mutu tana bukatar Neman yafiyar Sajeeda da Iyayenta,kafin ta mutu tana bukatar ta nemi yafiyar Yesmeen, Yesmeen da bata Mata komai ba ta Dora Mata Karan tsana.

Tana daki ta ringa jiyo muryar dattijuwar na yiwa wani Wanda take kyautata zaton shi ne maigidan akan ayau take so a fitar da ita daga gidan tunda ta farka, yadda taji muryarsa na rawa yasa ta tuna nata mijin da take juyawa da tana tunanin har da bakin cikinta ya Kashe shi.

Ido ta zubawa k'ofar a lokacin da ta ji sun nufo d'akin mutumin na zuwa ya rike hannunta matarsa ta Taya shi Suka yi waje da ita.

Suna zuwa k'ofar gidan matar ta saketa tana "Yayi maza ya kaita bakin titi"

Ta rufo k'ofar.

Mutumin da alama.yana tausayin ta.

Haka ya nade rigarss duk da warin da take haka ya kinkimeta dan tuni ta dawo sirriya Kamar Mai cutar kanjamau.

Da alama gidan nasa a wajen gari yake dan sai da suka yi tafiya Mai nisa Yana yi yana ajiyeta yana sosa hanci da wari ya saka ya ringa haka,karar motocin da take ji yasa ta gane sun kusa titi.

Hawaye ne ya hau zubo mata dan idan ya ajiyeta bata san waye zai taimaka mata ba,Yana kuwa zuwa bakin titi ya ajiyeta yana "da ace kina iya magana da kin fadamin wani naki na neme shi na Kai ki,a yashe na tsince ki a daji da naje saro itace,nan wajen gari kike hanyar barin garin Abuja bansan Mai ya kawo ki Nan ba,har ga Allah naso na taimaka miki,amma naga hakan na Neman haddasa min matsala da mai d'akina Allah ya baki lafiya ya kawo Mai taimaka miki"

Girgiza Kai Yaya Abu ta hau tana gurnanin Kar ya tafi ya barta ta taimaka Mata.

Sai dai tana ji tana gani ya juya ya fara tafiya haka ta kwanta a titi tana sharbar kuka,ta dauka zata ma iya daga hannunta sai dai ta kasa,haka ta kwanta a kasan tana Kiran sunayen Allah dan yanzu bata da mataimaki sai Allah.

Sajeeda

Tunda muka dawo garin kano muka dan samu nutsuwa, Saifullahi shi ya ringa Kai kawo,bansan yadda yayi ya d'auko mahaifinsa a Kai shi asibitin mahaukata ba,sai da ya dawo yake fadamin,hawaye cike a idonsa ya hau rokona akan na yafewa Babansu iya halin nan da yake ciki kawai ya isa yasa a yafe masa dan tun a gidan duniya Allah ya ke hisabi,wani zai iya dadewa Yana sabawa Allah bai samu ya tuba ba har Allah ya dau ransa kamar yadda Allah ya dauki ran Rabiu a lokacin da bai tab'a tunanin ba,Wanda sai da ya mutu wasu da yawa Suka san halin da ya jefa kansa da arzikin sa ya fara konewa, Wanda ya na da tabbacin shi ne ya jawo mahaifunsu ya Shiga wanan kungiya,kila Allah Yana san mahaifin su da rahama shi yasa ya tona Masa asiri a gidan duniya kowa yasan halin da jefa kansa a ciki,na tuna baya da ba haka yake ba, mahaifunsu nagartacen mutum ne,haduwa da mugun aboki da San zuciya ya Kai shi ya baro"

Hawaye kawai ke zubo min dan duk maganar da yayi ba karya tun kafin ma ya rokeni akan na yafewa Kabiru na yafe Masa dan Allah Yana San masu yafiya,nima zanso ya yafemin kura kuraina,ko iya warkar dani da yayi a lokacin da na fid da rai da rayuwa na fara kawowa kaina mutuwa Allah ya mikar dani, cikin ikonsa ya nuna min tsafi karya ne,raina a hannunsa yake ba a hannun kowa ba shi yake azurta Wanda yaso ya Kuma talauta Wanda ya so Allah shi buwayi ne gaggara misali,yayi min niimar da zan dawwama ina gode masa dan bana Jin ko duk kudin duniya zaa hada dan a nema min magani zan iya samun sauki,cikin ikonsa ba tare da an sha wahalar komai ba ya warkar dani,iya wanan kawai ya Isa yasa na yafewa Kabiru da Yaya Abu da naji kwana biyu ta tsaya min arai,bansan inda take ba dan bata je gida ba

Nasan duk Inda take tana nan tana Shan wahala har ga Allah balain tausayinta nake ji,dan ko makiyina bana Masa fata ya Shiga halin da na Shiga balle jinina da muke uwa daya uba daya,cikin sheshekar kuka nacewa Saifullahi na yafewa Kabiru duniya da lahira yamin godiya ya kalli kanensa ya musu nasiha yace su ringa yiwa abbansu Addu'a,yayi wa Yesmeen godiya irin daiwaniyar da tayi dani.

Ya maida kallonsa Kan Nusrah da ke rik'e da jaririyarta tabi ta rame Kamar ba ita ba,ya Kira sunanta ya fara magana Yana "Bawa bai Isa ya tsallaka kaddarar sa ba Nusrah hakuri zakiyi haka Allah ya kaddara Mana,banso na cigaba da miki b'oye b'oye mijinki ya aiko Miki da takardar ki saki biyu ya Miki yace bazai iya cigaba da zama dake ba idan kinyi yaye zai zo ya dauki yarsa"

Jarumtaka na aro na yafa na hau sallati a zuciyata,abinda nake ta gudu kenan amma ba yadda zamuyi

Na daure na fara magana Ina "Nusrah kice alhamdulillah"

Nusrah take tabi umarnina tayi hamdala Banga alamar tashin hankali a tare da ita ba cikin kwantar da murya na fara magana Ina "Aure rai ne dashi Nusrah Allah yayi aurenki dashi ya Kare Koda ba ta silar mahaifin ki ba,in Sha Allah yadda Kika godewa Allah da wanan jarrabawa

Zaki gode masa da k'ofar da zai bude miki,dama baya kaunarki dan da yana kaunarki bazai rabu dake akan laifin da ba ke Kika aikata ba,dan kila da bai sakeki ba haka zai addabi rayuwarki da gori har ki kasa samun kwanciyar hankali,Allah yasa hakan shi yafi Miki alkhairi"

"Ameen umma wallahi banji komai ba dan dama na dade Ina ji a jikina zamu rabu din Allah ya bani wanda ya fishi"

"Ameen "nace Ina Jin sanyi a zuciyata ban tab'a kawowa zata iya wanan dauriyar ba Saifullahi ya cigaba da musu nasiha da hakuri da irin kalubalen da zasu fuskanta a gaba,na tsangwama da gori daga mutane,Yana rokon su akan Kar su sake su damu,dan ba Wanda ya rubuta kaddarar sa da hannunsa ba Kuma abinda baya wucewa watarana zai wuce kamar baayi ba.

Godiya na ringa yiwa Allah da ya bani Saifullahi da nake mamakin hankali da  nutsuwar sa,yau gashi har dani yake yiwa nasiha a karshe ya gargadi kanennsa da kusantar haram,na dauka idan Yara suka fita waje lalacewa suke sai gashi nawa yaran Allah ya dafamin a tarbiyarsu a nutsen su suke ba mai yarda ma Nusrah ta girmeshi duk da shekarun da ta bashi daya da wata biyar ne.

Allah ya bani yaron da ko faduwa nayi na mutu zai iya kula da kannensa,dan Allah ya Buda masa kwakwalwa baiwar zanen da yake dashi yasa kudade suke shigo masa.

Tuni ya dauki nauyin gidan,Ya maida Yesmeen makaranta,ban taba binsu asibiti dubo mahaifinsu ba,dan duk sati haka suke zuwa asibti duba shi,a fadar su daure shi ma ake ya daina Haushin karen Yanzu Amma indai ya gansu haka zai zubo musu ido Yana kallonsu.

Nidai ba abinda nake iya cewa Ina dai yi Masa addua a zuciyata,

Yanzu na dan dawo da jikina Ina Shan magungunan da Saifullahi ke siyomin,matsalata daya har yanzu Ina fitar da ruwa mai doyi, watakila wanan shine kaddarata,bazan warke gabad'aya ba,taya ma Zan warke gabadaya an sadu da kare an zo an sadu dani,da wuya na warke.

Alhamdulillah komai na dan tafiyar mana  daidai,dan Nusrah itama ta koma makaranta da taimakon Saifullahi dan Saifullahi yasan manyan mutane,idan ta tafi makaranta sai ta barmin takwarata.

Yesmeen kuwa tsallake aka mata dan tana da k'ok'ari sosai ban kawo tana zana jarrabawar gama secondary zata ci ba,sai gashi ta fito da sakamako mai kyau.

A irin wanan lokacin gwaggo da Yaya Asmau Suka kawo.mana ziyara.

Sunji dadin yadda suka ga nida yarana,duk da gori da tsangwama da muke fuskanta a wajen

wayanda basu da ilimi hakan bai saka mun ki walwala ba.

A Daren ranar kwana muka yi muna hira da Gwaggo muka yi ta zancen Yaya Abu da Gwaggo ke cikin damuwa saboda ita,dan tace ko bacci batayi tafiso tasan halin da take ciki saboda tasan irin addua da zata ringa yi mata hannun ka baya rubewa ka cire ka Yar.

Har ga Allah nima kwana biyu tana raina, dan idan inaso na tunata sai na tuno halinta mai kyau dan bazai yu nace bata da hali Mai kyau ko guda daya bane.

Ni na ringa kwantarwa da Gwaggo hankali Ina ta cigaba da Addu'a in Sha Allah zamu gano Inda take Addu'ar iyaye na tasiri akan yayansu.

Yaya Asmau ce ma naga bata wani damu ba,wajen Sha biyu muna hira da ita nake fada mata yadda na ke neman maganin da zai warkar dani na daina zubar da ruwa mai doyi dan yanzu shi kadai ne matsalata.

Tambayata tayi ko na gwada na gargajiya na girgiza Mata Kai sai tace mai zai hana na nemi maganin wata a katsina maganin ta nada kyau,tasan wacce itama ta ke fitar da ruwa mai wari a gabanta tana Shan maganinta ta warke ,jiki na rawa nace ta hadani da matar da tayi amfani da maganin ta na tambayeta naji,sai tace min bata da lambarta amma zata Kira wata ta turo mata lambarta,sosai naji sanyi a zuciyata dan zanji dadi yau na wayi gari ruwan nan ya daina fita a gabana.

Kwana biyu kawai Suka yi da suka zo tafiya ta bani lambar matar da tayi amfani da maganin.

Koda na kirata ban samu ta dauka ba sai da yamma ta biyo Kiran Muka gaisa da ita na fada mata yadda akayi na samu lambarta da taimakon da nake so tamin,cemin tayi Kar na damu yanzu nan zata turo min lambarta matar a katsina take maman mujahid maganinta na da balain kyau ko da baka discharge maganinta na fitar da dattin Mara
08162859027 bari ta Tiromin lambarta na kirata na Mata bayani.

Godiya nayi Mata Ina kashe wayar sai gashi ta Tiromin lambarta 08162859027.

Duk da munyi waya da ita ta bani tabbacin zan warke idan har na Sha maganin ban yarda ba Zan dai gwada naga ko zan dace.

Sai da Saifullahi ya dawo ya tura mata kudin,yace min akwai abokinsa zai taho daga katsina zai taho min dashi ya hau bani labarin yaje wajen Babansu ya dubo shi a asibiti da alama yana dan samun sauki,dan sai kallonsa yake Kamar ya gane shi,ce masa nayi Allah toh ya bashi lafiya dan zanso ya samu lafiyar ya gyara lahirarsa daya bata, zanso ya samu lafiya ya gyara kura kuransa,a yanzu babban burina naga Yaya Abu nasan tana cikin mawuyancin hali dan ba dama

na kwanta sai nayi mafarki da ita,kwana biyu a tsakani Saifullahi ya zo da dalaleliyar motar da aka masa kyautarsa a wani company kera motocin da ya musu zanen da suka yaba duk da sun biya shi kudinsa sai da suka hada da masa kyauta,banda Ina ganin labarai nasan Saifullahi da guminsa yake samun kudi,da tuni na tsorata dan har ga Allah ba abinda ke bani tsoro sama da kudi,nafisan rayuwa rufin asiri,amma Allah ya kaddara Saifullahi Yana da rabon arziki Wanda da babansa baiyi gaggawa ba da a yanzu tare zamu ci arzikinsa cikin rufin asiri,kwana uku nayi Ina Shan maganin da na siya  a wajen maman mujahid na fara ganin canji a jikina,dan ruwan ya rage zubo min na Kuma ji dadi sosai,dan har kudi na sake tura mata akan a Karo min jarka biyu.

Ina zaune a palo Ina duba wani littafin addu'oi da Yesmeen ta mallaka naji dirin motar Saifullahi dan Yana cigaba da makaranta anan buk dan har ya kusa kamallawa,su Annur kuwa suna level one tare da  Yesmeen dan ban da Yesmeen ta bar zuwa makaranta da yanzu tana level 3,Yana shigowa ya zauna sai da ya gaisheni ya hau cemin gobe zai tafi Abuja akwai aikin da zaije yayi jibi zai dawo na Masa addua.

Murmushi na saki Ina sai dai na Kara Masa addua Amma kullum a cikin adduata suke bakina bai tab'a yankewa da musu Addu'a gabad'aya ba,a yanzu sai naji banida burin da ya wuce naga ma Saifullahi yayi aure dan ba Mai kallonsa ya dauka bai Kai talatin ba, saboda yadda ya girma, duk wani rufin asiri Allah ya mishi dan har gini yake Mana, wani mallamin su Nusrah ya makale mata akan Yana santa kamar yadda wani Saeed ya makalewa Yesmeen Yana kaunarta Saeed shine Wanda mahaifinta ya taimakawa yesmeen a lokacin da ta gudu,har nan yake biyota Amma Yesmeen Taki bashi fuskar a fadarta bata san Mai kudi ita dai talaka zata aura,dariya take bani dan nasan tsorata tayi ta dauka kowane Mai kudi ta hanyar da Kabiru yayi kudinsa suke kudinsu.

Ba na so na matsa mata shi yasa na rabu da ita amma babban burina naga na aurar da su biyun dan tuni tsohon mijin Nusrah yazo ya karbi yarsa.

Allah Kuma ya dubeta tana fara zuwa makaranta Allah ya mata farin jinin samari dan duk ba mai mata itace dai tak'i kulasu.

Saifullahi kwanan sa biyu a Abuja yamin waya akan ya gama abinda ya Kai shi gobe da sassafe zai taho.

Addua dawowa lafiya nayi Masa.

Yana kashe wayar na cewa Yesmeen su Shiga Kitchen suyi wa Saifullahi abinci.

Suna girki a kitchen Ina jiyo hirarsu Ina murmushi,a yanzu banida wani matsala sai dai nace Alhamdulillah burina kawai yanzu naga auren yayana.

Su Annur kuwa yanzu basa jiran sai Saifullahi ya Kai su asibiti wajen Kabiru da kansu suke tafiya asibitin duba shi,haka zasu zage su tafi da abubuwa,Yesmeen ce dai bata yarda ta bisu ban Kuma tab'a tilasta mata ba dan gani nake tsoronsa take ji.

Wajen karfe biyu muka ji dirin motar Saifullahi a k'ofar gida,sai da ya dade kafin ya shigo har Ina tunanin tura Yesmeen ta dubo Mai ya tsayar dashi sai gashi ya shigo d'auke da wata tsohuwa, mik'ewa nayi daga zaunen da nake Ina kallonsa har ya shigo da tsohuwar da ana shigowa da ita naji wani irin wari,yana isowa tsakiyar palon ya ajiyeta,na zubawa tsohuwar ido cikin tausayawa yadda take zuba wari,Ina k'ok'arin tambayar Saifullahi inda ya samo tsohuwa yace "Umma baki ganeta ba ko mama ce fa"

Kirjina wani irin bugawa yayi naja da baya tare da sakin sallati jikina ya dauki rawa,Taya wanan tsohuwar zata zama Yaya Abu, sallati kawai nake Saifullahi ya hau bani labarin yadda ya ganta da ya d'auko hanyar tahowa motarsa ta lalace,a garin Nemo mai gyara motar ya dan shiga bayan gari shine ya ganta a kwance kudaje nata binta ya dauka ma mutuwa tayi Saboda warin da take sai da ya tambayi mai gyaran motar ya hau bashi labarin ta akan almajira ce da suka kasa gane wane irin cuta ne da ita mutane ma kyankyamin ta suke dan har yanzu ma mamaki suke da bata mutu ba,cikin tausayawa Saifullahi ya matsa kusa da ita dan ya bata kyautar kudi,a daidai lokacin da ta bud'e idonta tana numfarfashi duk da tsufan da yaga tayi da yadda koma kamar kwarangwal sai da ya ganeta,jiki na rawa ya roki Mai gyaran mota akan ya taimaka masa zai biya ko nawa ne,a samu wasu su wanke ta a canza mata Kaya,yayar mahaifiyar sa ce da ake ta nema,abinka da kudi,tuni ya samo wasu mata suka kaita gidansu Suka wanketa suka Nemo Kaya suka saka Mata Saifullahi ya Basu kyautar kudi,ana gama gyara Masa mota suka dau hanya yasan Sajeeda zata ji dadi, dan daidaikun rana ne bata maganar Yaya Abun

Sajeeda

Kuka na fashe dashi,dan ba Wanda zai yarda Yaya Abu ce ta dawo haka,itama kallona kawai take tana hawaye ba mai imanin da zai kalli Yaya Abu bai tausaya mata ba,jiki na rawa na kaita bandaki dan wari kawai take,banji kyankyaminta ba na wanketa na bata abinci na Kira Gwaggo a waya na sanar mata da anga Yaya Abu yanzu haka tana gidana,yarana ma sosai suka tayani murna dan ban basu fuskar da zasu tsani yayata ba,tuni na hau hidima da ita,dan har ga Allah na yafe mata,ita kuwa kuka kawai take tana gurnani,Wanda halin da take ciki ya tuna min da Nima halin da na Shiga a baya, washegari da sassafe gwaggo ta duro ita da Yaya Asmau da Yar Yaya abu shemau suma sun girgiza da yadda ta dawo,shemau sai kuka take dan ta dade bata ganta ba,ita kanta batasan Mai yasa bata nemi Yaya Abu ba duk tsawon lokacin nan

Kuka muka ci muka koshi muka hau Taya Yaya Abu da Addu'a dan nasan ba maganin da zai warkar da ita sai karfin Addu'a.

A.ranar da ta cika kwana shidda a gidana muna d'akin a zaune  ciki kuwa har da Gwaggo dan baba bai dade da tafiya ba shi ma yazo ya dubata ba Wanda ma zai rike yaya Abu a ransa da idan ya ganta Bai ji tausayin ta ba,

Ganin kamar tana so a tayarta zaune yasa na mikar da ita na jingina bayanta da jikin gadon hawaye na zubo mata naga ta fara motsa baki kamar mai koyon maganar  ta fara "Sssaaj jj ee da ki yafe min Gwaggo dan Allah ki yafemin,kice baba ya yafemin, Yesmeen ki yafemin dan Allah ku yafemin na yafewa Kabiru dan inaso nima Allah ya yafemin.

A rude muka hada baki wajen cewa mun yafe mata Gwaggo kuwa sai saka Mata albarka take,a hankali muka ga ta fara shakuwa muka yi kanta gabad'aya cikin kiftawar ido ta daina motsi Yaya Abu ta amsa Kiran Allah

Munyi kuka Kamar ranmu zai fita,Muna ji muna gani aka yi Mata sutura aka kaita gidanta na gaskiya duniya zancen banza,duk San mu da duniya dole mu tafi watarana tunda mutuwa dole ce,a kwana a tashi sai gashi mun tafi wata biyar da rasuwar Yaya Abu da muke ta binta da Addu'a dacewa da Rahamar Allah

Kabiru kuwa da ya dawo hayyacinsa kad'an tilastawa yayansa yayi suka kirani Yana kuka ya hau Neman yafiyata nace Masa na yafe Masa yayansa suma suka ringa tayashi kukan,da Addu'a ya bimu gabad'aya sai da muka zo tafiya ya bawa Annur wani farin takarda akan ya bani, muna fita daga asibitin ya bani Ina dubawa naga takarda saki ne ya sakeni saki daya Wanda har ga Allah Dadi naji dan ko ya warke ba koma Masa zanyi ba.

Cikin sauki ya bani takarda ta a haka rayuwa ta cigaba da tafiya cikin rufin asiri, Saifullahi kuwa budi yake samu ko ta Ina Fahad shi ma ya samu aiki,Nusrah kuwa mallaminta daya dage mata sai da ya turo magabatansa aka sa musu rana, ni kuwa ganin Yesmeen na tsalle tsalle da Saifullahi na Kira Saifullahi har daki na fada masa Ina so ya auri Yesmeen dan babban burina kenan a rayuwata na dade da burin nan a zuciyata amma idan Yana ganin bazai iya aurenta ba shikenan.

Ga mamakina Saifullahi take ya amince da auren Yesmeen

Toh mai ya ragemin a rayuwa babu,Kamar a mafarki sai gashi na aurar da yayana uku Rana daya, Saifullahi a gidan da ya gina ya ware bangarensa da na Yesmeen Nusrahh kuwa itama bata da nisa dani,ba abinda yayi farko da bashi da karshe wuyanta kayi hakuri, Kabiru har gobe Yana asibiti dan idan ciwon nasa ya tashi Yana dan tab'a hauka.

Shekara biyu a tsakani Saifullahi ya biya Mana muka je muka sauke faralli ni dashi da Yesmeen da ke hidima dani kamar a baya.

Yanzu zan iya cewa Alhamdulillah rabbil alameen dan yarana gabad'aya ba Wanda bashida

abin yi ta hanyar halal har rububin kyautata min suke,duk da ba tsufa nayi ba bana kawowa kaina aure Wai kusa bansani ba ko nan gaba.......

Alhamdulillah rabbil ala meen anan na kawo karshen littafin RUFAFFEN SIRRI kuskuren da nayi a ciki rabbi ya gafarta min nagode da fatan alheri da hakurin da akayi wajen bibiyar littafin sai mun sake haduwa a sabon novel da zai zo muku nan da bayan sallah idan muna da tsawon rayuwa

Taku Mai kaunar ku sadnaf Dan darajar Allah Kar a hadamin document ngd🙏🙏🙏🙏